''taya kika san cewa yana sona?''
''ta yanda nasan cewa bakya son sa''
''taya kenan?''
''toh kina sonsa ne?'' ɗan shiru tayi na dan lokaci kafin ta girgixa mata kae tana cewa
''ni nasan bana sonsa kuma duk wacce ta kalleni xata gane cewar bana sonsa''
''toh haka shima ake gane yana sonki da kallo ɗaya''
''amma ae baya sona, aurena yayi for his personal interest''
''kinada tabbacin haka kuma?''
''sosae kuwa nakeda tabbaci''
cikin nutsuwa tayi mata summarizing ratuwar gidansu har xuwa kan auren da yanda aka yi sa, ga mamakinta sae taga hayiin tanata sakin murmushi tana jinjina kae
''kinata murmushi kinyi shiru kuma''
''toh ba dole inyi murmushi ba yarinya, yanxu ke in banda abunki anan har sae kin tambaya idan yana sonki ko a'a, karfa ki manta a yanxu anan da muke xaune kike cemin uwar riƙon tasa batason abun da farko daga baya ne ta amince toh a tunanin ki inda tana son abun xata hana ne da farko?'' kanta ta girgixa mata wani tunani na son faɗo mata
''bari na faɗa miki wannan, ni nasan Ibrahim tun yana matashin sa yarone mae mutuƙar nutsuwa da kuma hankali babu ta yanda xa'ayi xugar wani ko wata kokuma son rura wata wuta yasa ya aureki, baxai taɓa taya uwarsa tsanar ki ba indae har baxai iya gyara tsakaninku ba toh ba xai shiga ba, ki sani idan namiji yana sonki bayaji baya gani kuma duk yanda kuke xaman rashin daɗi da mahaifiyarsa duk yanda take ƙin ki indae shi yana sonki toh fa he can do anything to keep you by his side, karki yiwa kanki baƙin ciki, domin idan kika kashe aurenki baxaki taɓa komawa daedae da mahaifinki ba kuma ba xaki ƙara samun miji kamar Ibrahim ba'' daga haka ta wuce ta barta

tana tunani
Danne duk wani abu da takeji tayi washe gari tabi ayarin yan matan garin sukaje rafi kawae she wants taste how this kinda life is, da yake dama wanki ne duk xasuyi so samarinsu sunxo sun ɗan tattayasu ganinsu yasata komawa chan edge ɗin rafin tana kallon yanda ruwa ke tafi
Wani wutsil-wutsil taji ana jefa abu a rafin kuma ta gefen fuskarta abin ke wucewa ɗan juya kanta tayi suka haɗa ido da jarumin nata yana tsaye jikinsa sanye da mens kurti blue black wandon yasha wani uban naɗi an maƙala masa kalgi a tsakiya sae ya fito sakk ba'indiye
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 9
Typing.....✍
''Kaenee?'' da mamaki ta faɗa tana ɗora hannunta a ƙirjinsa, hannunsa ya ɗora akan natan yana sakar mata smile yace
''yess ya kika ganni?'' ɗan murmushi itama tayi tana janye hannunta
Binta yayi suka xauna a gefen ruwa, duwatsun daya ɗebo ya kamo hannunta ya xuba mata rabi ya riƙe rabi yana jefawa ganin tsaya kallon yanda yakeyi ɗin yasashi cemata itama tayi, sun yi nisa da abun ta juya tana tambayarsa yanda akayi ya iya abubuwan ƙauye kamar jira yake ya hau bata labarae akan ƙauyukan da yasan yaje
Sune basu baro wurin ba sae wurin 11 maxan sun wuce wani wuri matan ne kawae suka taho suna tafe suna fira duk da ita ba ganema indiyanci take ba amma tana ƙoƙarin famintar abunda suke cewa idan ta kasa kuma nandu ko boomi su faɗa mata da turanci yanxun ma kallonta boomi tayi tana ƙoƙarin ƀoye dariyarta tace
''kinji abunda suke cewa kuwa'' tana buga wani stick a hannunta ta girgixa kae batare da ta kalli boomi ba
''she said you've got a nice and lovable husband, that luv u morethan expressing, she wishes she were you'' murmushi takeso tayi amma hakanan taji bakinta so dry, bata ƙara tankawa ba har suka isa gida
Da dare ma tana xaune tanacin suya da yasa aka kawo mata hannunta riƙe da wayarta da tunda taxo batayi amfani da ita ba dan ba'ayi mata inserting sim ɗin ƙasar ba, wayarsa dake ringing ta katse mata tunani tana kallon wayar har ta tsinke wani kiran ya shigo dayake basuda nisa da wayar ajiye

tata tayi ta miƙa hannu ta ɗauko tasan daedae kiran na katsewa tana ajiyewa wani ya kuma shigowa bata tsaya dubawa ba kawae ta ɗauka ta miƙe dan xuwa dubosa, lelleƙawa tayi bata gansa ba sanda kira na biyar ya shigo wani dogon tsaki taja sae a lokacin ta kalli screen ɗin ''NATOU'' kallon sunan take da kyau tana tuna ranar dayake waya da meenal
''yaa Khaleel wae ina ka shiga naketa kiranka baka ɗaga ba?'' cikin shagwaɓa meenal ɗin ta faɗa jin an ɗaga wayar
''mtcheeeew sakarya yar wahala, ke saboda wahala da rashin xuciya daya tattare a kanki da har yanxu kina kiran mutuminnan?'' meenal dake chan tunda adawiyah ta fara magana ta miƙe tsaye dan dama a cike take da ita tace
''toh fa hada su kaxa a cin danƙo kekuwa meye naki a ciki Allah mun tuba mutum da nasa''
''ehh na gani kam, toh bay....baxan bari ya ɗaga wayar ba yanxu bacci xaiyi'' bayanan da xatace sae kuma wani tunani ya faɗo mata daya sakata saurin gyarawa, wanda saƙon da takeso ta isar yaje da kyau a ƙule meenal tace
''kinga dalla malama ina ruwan ki, ke asu wa da xaki hanasa ɗaga waya?''
''ni asu matarsa wacce wasu basu samu matsayin ba duk da yanda suka fito suka nuna xalamarsu a fili''
''kinga malama ni ba maganar iska nakira kiyi ba AUNTY ce takeso tayi magana dashi ki bashi waya kawae'' ɗan janye wayar tayi ta kalli number ta maeda kunne
''au AUNTYN ta fara binki yawon Dubai ɗinne itama? toh bara kiji koda late mahaifiyarsa ce ta kira a yau dae baxai ɗauka b.....''
''wae ke adawiyah dan kinga ya Khaleel yana tsananin sonki shine kike tunanin xaki taka kowa?.....''
Gaba ɗaya jinta ɗaukewa yayi lokaci ɗaya ta faɗa duniyar tunani wanda xuwansu nan ta fara irin wannan tunanikan a duk lokacin da xa'a faɗa mata kalmar 'yana sonki' itadae a iya saninta basu san juna ba, tadae sansa a suna, basu taɓa magana ba, wani event bae taɓa haɗasu ba kawae rana ɗaya akayi spreading pictures ɗinsu sae kuma maganar aure ta ƙullu
''Assalamu Alaiki'' firgigit ta dawo hankalinta tana sauke wayar dan meenal ɗin har ta kashe tuni
''are u alright?'' miƙa masa wayar tayi tana xarar mayafinta ta raɓasa ta fice
Da kallo ya sae kuma ya ajiye wayarsa kusa da tata ya bita, sanda ya fito har ta fice dan haka bin bayanta yayi amma bae tsaedata ba saeda ta iso wani ɗan ƙaramin fili aka kunna wuta a wurin, wutar ta ɗan yi sanyi ma da alama an jima da kunnata
Xama tayi tana haɗe ƙafafunta ta xagayesu da hannunta ta ɗora kanta a kan guiwarta tana lumshe ido shima xagayowa yayi ya xauna yana kallon wutar, a hankali ta ɗaga kanta tana kallonsa kamar mara lafiya tace
''me ya kawoka nan?''
''Ke na biyo'' batare da ya kalleta ba ya faɗa, ajiyar xuciya ta saki tana maida kanta ƙasa, kusan 5mnt of silent kafin yace

''idan kinada damuwa ba ƀoyeta ya kamata kinayi ba, confess it let someone hear it, let someone beer it for u too, let someone new be in your life may be that someone has something to offer that will change your life for good, ni bance dole ki faɗamin damuwarki ba but atlease talk to someone ta hakan xakiji sauƙi'' daga haka ya miƙe ya kama hanya, karaff yaji ta riƙe hannunsa tana ɗaga kanta ta kallesa
''shin da gaske ne ka aureni ne saboda kana sona? shin ba Hajiya Babba bane tayi instructing naka da ka aureni ba?'' dawowa yayi ya xauna yana naɗe hannunta a cikin nasa
''ko kaɗan ba AUNTY bace tace na aureki ba, bakuma AUNTY bace ta amince da auren dan kanta ba someone else ya saka ta amince ba'a son ranta ba'' wani kallo ta masa tana cewa
''me ka maeda ni ne? duk duniya akwae wanda kake tunanin xaiyi forcing hajiya Babba ne?''
''ABBY YOUR FATHER SHINE YACE YANASO INDAWO NIGERIA IN KUMA AUREKI'' wani irin xabura tayi yayi saurin riƙota
Haaaam bakina ya fashe bari na tsafa magani😜
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 10
Typing.....✍
''careful'' ya faɗa yana riƙeta, kwace jikinta tayi tana girgixa kae da ƙyar ta iya ta furta abunda ke bakinta
''karya kake, koh? nasan xewa ƙarya kake Abby baxai ce kaxo ka aureni ba''
''nasan ba lallae ki yarda ba amma ki saurareni da kyau xan faɗa miki komae''
THROUGH BACK
A lokacin da ta gama internship a lokacin akayi bikin faɗhima wacce taƙi yin aure har sae da ta gama masters ta fara aiki duk da tun a shekarun baya dama suna tare da shi wanda ta aura ɗin, toh a ranar da akayi sa lalle a ranar akeyin mother's eve ɗin yayar khaulat ya Biibah, tun da farar safiya mamy ta shirya da yake Abby baya ƙasar tace mata itama ta shirya su wuce amma sae tace wa mamy taje kawae tana xuwa daga baya
Ashe tasan abunda ta shirya, wuraren biyar na yamma aka fara kaɗe-kaɗe tana daga balcony ɗinsu tana kallo har aka fito da amarya aka fara saka lalle,

doguwar riga ta saka ta anko ɗin da aka yo musu duka yan gidan tare tayi makeup sosae abunda ba yi take ba, yan gidan duk sunyi mamakin ganinta dan koda hutu taxo xa'ayi bik idan taga dama ko sau ɗaya baxata fito ba anko kuwa koda an mata bata sakawa sae bayan biki amma yau sae gata da anko kuma a bikin faɗhima wacce basa ko ga maciji
Cikin su humairah taje ta xauna tare da wasu cousins ɗinsu wanda suke tsara hannunta na riƙe da wayarta tanata dannawa har iyaye suka gama yan mata sukaxo suma suka shasshafa mata bata tashi ba saeda motocin ɗangin ango ta tsaya suka fara fitowa da kayan saka lalle suka ajiye aka basu lallen dan su shafa mata
A nutse ta miƙe tana takwa har gaban aunty kubra ta ɗauki lallen dake wurin ta matsa kusa da amaryar ta ɗebo a hannu suka shafa mata a cin ɗinta ita da yayar mijin nata suka kalli juna kowa tayiwa kowa murmushi, tana ƙara kwasowa da gangan ta kae ƙafarta kusa da ta yayar mijin faɗhiman ita kuma bata lura ba ta ɗora tsinin takalminta akan fatar takalmin adawiyahn dake cover ne amma flat yasa tsinin ya soki ƙafar sosae, wani irin wurgi tayi da trayn tana sak dukkan ƙarfinta ta ture matar take tayi taga-taga ta faɗa cikin lallen da adawiyahn ta watsar
''baki gani ne xaki kasheni?'' gaba ɗaya wurin wani irin shiru ya ɗauka kafin lokaci ɗaya hankalin mutanen wurin ya dawo jikinsu faɗhima tayi ƙarfin halin cewa
''adawiyah meye haka ne?''
''abunda kika gani, wato tsanar da akamin har ta kae ki faɗawa wanda xaki aura shikuma ya faɗawa yan uwansa ake ƙoƙarin wulaƙantani dan na xo koh? toh bari kiji baku is ku hanni rawar gaban hantsi a gidan ubana ba wl.....'' bata ƙarasa ba AUNTY data mutuƙar fusata ta ɗauketa da wani xafaffen mari daya fasa mata baki lokaci ɗaya kama bakin tayi tana son haɗiye xafin daya karyo mata ta saki murmushi tana mere baki
''bakiyi laifi ba hajiya babba, babu laifi tunda ae uwata batanan xaki min abinda yafi haka indae kece'' sae ta juya da sauri ta ɗauki ruwan roban dake kan table ɗin amaryar ta buɗe bata jira komae ba ta juyeshi akan in-law ɗin faɗhiman da har lokacin take a ƙasa tana jinyar maxaunai
''wannan shine ramuwar da xany.....''
wani irin saukar duka ta fara ji kota ina, tun tana ƙoƙarin kwacewa har ta haƙura saeda suka mata ligis sannan suka rabu da ita, daganan sa lalle ya watse, wurin 8pm sae ga mamy afujajan a lokacin ma har adawiyahn tayi wanka ta sauya kaya tana shan tea taji dirin mamy da sauri ta ajiye cup din ta dawo nan ƙasan carfet tanata juye-juye
''baby nah, ina ɗiyata?'' hannunta ta ɗaga mata tana daga kwancen
Wurin 10pm sae ga motar police da yake asibiti mamyn ta kaeta suka haɗa baki da doctor ɗin akan ana buƙatar saka hannun police shine ita kuma mamyn taje dan ɗaukar police ta kuma faɗa musu komae shine sukace basu yardaba, a lokacin har sunyi shirin bacci police ɗin suka musu dirar mikiya da farko sodojin hanasu shiga sukayi saeda mamy tayi musu magana amma

dukace sae sun nemi izinin Abby da yake mamy tasan baya ƙasar sae tace toh su kira ɗin, kira Abbyn sukayi a kashe hakan yasa suna gani aka kwashe duk matan dake part ɗin AUNTY duk da yanda maxan dake gidan suma sukayita bawa police ɗin da mamy baki amma ko saurare batayi ba tasa aka kwashe su AUNTY aka wucee da su
Tabbbb lallae ashe anyi wani schene bamu
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae maen nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 11
Typing.....✍
In taƙaice muku xance dae, su AUNTY saeda suka kwana suka wuni kafin Allah ya kawo Abby wanda shima da ƙyar ya samu aka kyalesu bayan adawiyahn tace ta janye ƙaran wanda shine karo na farko da suka samu mummunan saɓani har ta kaeshi ga mata baraxana, tun daga lokacin kuma sae abubuwanta suka so barin kansa amma da yake mamy mace ce da tasan kanta tabi duk hanyar da tasan xata iya bi ta gyara tsakaninsu
Anyi haka da kamar sati biyu yace xaije wani business trip wanda a lokacin general checkup ne xaije London, instead of London sae ya wuce Moscow gun KONTO wanda yaje anual leave dan ya ɗan samu duba patient dan ya daɗe bae je can ba
Yana tsaye yana duba wata yarinya Abbyn ya isa gunsa yana dafasa jugowan da yake ya gansa aekuwa murna kamar yayi me, Ibrahim irin mutanann ne masu ƙa'ida dan haka wani daga cikin boys ɗinsa ya haɗa da Abby ɗin yace ya kaesa masauki amma fafur Abby yaƙi wae xai tsaya ya tayashi, tun asali shi ba mutum ne mae matsawa ba dan haka sae ya barshi suka je round tare kuma sosae Abby ya sake yana wasa da dariya da patients ɗin
Sanda suka dawo har an gama abinci dan haka suna fitowa wanka duk suka xauna ci, shiru wurin yayi dan kusan dukansu basa son surutu while eating, Abby da abu keta cixon sa a rae yanata jagula abincin gabansa dan tun da abunan ya faru bayada appetite sam, KONTO da tun ɗaxu yana lure da shi baece masa ƙala ba saeda ya cika cikinsa dan shi ba wasa da ciki janye kwanukan gefe yayi yana goge hannunsa da bakinsa sannan a nutse yace da Abby
''meye matsalar Abby'' ɗan xabura Abbyn yayi yana gyara glass ɗin idonsa yace
''ehm me kace'' ɗan shiru yayi yana kallonsa sae kuma yayi ajiyar xuciya yana

gyara xamansa daga ɗan ranƙwafawar da yayi xuwa xama da kyau
''Abby, something's bothering u'' murmushi yayi yana kaɗa kansa
''duk duniya kafi kowa saurin fahimta na mu'azzam''
''Abby kae fa mahaifina ne taya baxan fahimceka ba?'' kansa Abby ya jinjina yace
''na sani son nakuma gode''
''baxan taɓa takurawa akan sae naji damuwar wani ba, but u feel like talking am around''
''na sani son, nafi kowa sani'' ɗan matsowa Abbyn yayi gaba ya kamo hannayen KONTO ya haɗe da nasa ya jimƙe kamar wani mara lafiya a hankali ya soma magana
''Ibrahim ina cikin mutuƙar nadama wanda bansan lokacin da xan fice daga cikinta ba, bansan lokacin da xata barni ba ban.....''
''Subhanallah Abby wae menene?''
''Mu'azzam kasan cewar ni da Nana Aminatun tsofaffin masoya ne wanda naso na aureta tun da ƙuruciyar mu amma abun bae yiwu ba s....''
''Abby duka nasan wannan ae, just jump to the conclusion''
''Mu'azzam ina cikin nadama, ina cikin nadama Khaleel nadama kuma mara amfani saboda lokaci daya ƙuremin inama ace inada damar dawo da baya dana dawo da lokacin tun muna yara na goge Aminatu daga rayuwata'' sadda kansa yayi yana kallon hawayensa dake sauka akan hannayen su, kallonsa KONTO keyi har ya gama hawayen, tissue ya xaro ya basa yana harɗe hannayensa
''akan abunda ya faru da biki ne''
''ka samu labari kaema koh? kaji irin rashin arxiƙin da matata da yata suka min a gari koh?''
''Abby pls camedown mana u may stress u'r self fa u know ur condition, kuma ma naga ure sick already''
''Ibrahim na rasa ya xanyi, na ransa yanda xan ƀullowa gidana, abubuwan gidana are out of hand, na gaxa, ina tunanin na gax....''
''dan Allah Abby kayi shiru kaji ka daena faɗar haka''
''toh idan ban faɗa ba yaya xanyi? so nake ko ɗan yaya ne in rage abunda ke cin xuciyata, yaƴana dana haifa na raina na tufatar na shayar suna ƙoƙarin kaini ƙasa''
''Abbyy''
''bakasan yanda nakeji ba ne, inda ace ban haifi Rabi'atu ba, kaga yarinyarnan ita da mahaifiyarta? ina mutuƙar nadamar auren.....'' da wani irin sauri kamar guguwa KONTO ya ƙaraso gaban Abby ya saka hannu ya rufe masa baki yana girgixa masa kae
''dan Allah Abby kar kace haka'' janye masa yannu Abby yayi yana dafe hannuwansa a raunane yace
''bar musu gidan xanyi kokuma.....am aurar da ita xanyi'' ɗan buɗe idanunsa yayi yana murmushi yace
''aurarwa kuma Abby wannan yar yarinyar?''

''kwarae aure gwara in aurar da ita taje ta ƙarata''
''amma me yasa kakeson aurar da ita all of a sudden?''
''baxan ƃoye ma ba mu'azzam gaba ɗaya sun fita a kaena yarannan kuma ni nasan kae ne best husband that will handle Rabi'ah''
''ni kuma'' a xabure KONTO ya faɗa yana nuna kansa
''ehh kae''
''amma Abby me yasa kake tunanin ni xan iya''
''saboda kaene Ibrahim kaene Khaleel kaene mu'azzam kuma kaene KONTO'' ɗan kallon rashin fahimta ya masa hakan yasa Abbyn ci gaba
''ban haefeka ba amma na ɗauki roll ɗin uba a gareka ka tashi under my care, kaene yaro mafi nutsuwa dana taƃa sani a rayuwata kuma wannan nutsuwar taka ita ta bani sha'awar son haɗaka da Rabi'ah kamar yanda ake faɗa ne 'charbin kwae da nutsuwa kawae ake jansa idan akace xa'a jashi da gareje toh fa gangarawa yayan xasuyi tayi suna fashewa' idan har inaso in sauya yata mafi soyuwa a gareni toh fa dole ina buƙatar nutsatsen mutum irinka, domin ita da mahaifiyarta sune charbin kwan da na faɗama ni nawa charbin ya riga ya gama tarwatsewa, amma nasan kae xaka iya bin naka ta hanyar da xai koma dutse shiru KONTO ɗin yayi na minti 1 sannan kamar mae koyon magana yace
''Abby xanyi indae shine abunda kakeso toh xanyi maka''
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 12
Typing.....✍
Kallonsa takeyi babu ko kyaftawa hawaye duk ya jiƙa gaban rigarta kuma ta kasa tsaidashi kamar yanda hannunta yayi sanyin da ta kasa ɗagasa ta goge hawayen, shima KONTO ɗin kansa ya sadda a ƙasa yana ajiyar xuciya baeso koda sau ɗaya ba a rayuwarsa ya fitar da wannan maganar amma ya xaiyi abune da dole yana buƙatar ya faɗa mata dan gyara tsakanin ta da mahaifinta
''ke...ke.nan.....dam.a Abby.....yyya dd....'' wani irin kuka ne yaci ƙarfinta dole ta rufe bakinta
''ehh kwarae kin daɗe da barin xuciyar Abby mahaifinki! mutumin da ya soki fiye da komae na rayuwarsa ya ɗauki sunan mahaifiyarsa ya saka miki yayi miki duk abunda kike so kikayi karatu a best makarantu tun daga nursery har degree, ya baki best plaza da yake da ita kiyi running business ɗinki

amma duk kika watsar kika ɗauki abunda akayi tun kafin a haifeki kika ɗaurawa kanki kullum kina tayarwa da babanki hankali, duk wannan abubuwan dana faɗa miki babu wanda nayi making ɗinsa da kaena d.....''
''ina son kasancewa ni kaɗae'' cikin sanyin murya ta faɗa tana kallon wutar da ta ida komawa hayaƙi
Kansa ya jinjina mata ya miƙe ya wuce yana ɗan waiwayota, saeda ta daena jin motsinsa ta tabbatar yayi nisa sannan ta fashe da wani irin kuka tana saka kanta tsakanin cinyoyinta ta ƙanƙame jikinta tana jin wani matsanancin ciwo from inside
Yana kan sallaya ta shigo hut ɗin tana tafiya a harhaɗe taje ta janyo hijab ɗinta tana kaewa fuskarta ta faɗi anan, wani irin xabura yayi yana yin kanta koda ya ɗagota ma she already pass dole ajiyeta yayi akan bed ɗin yayi saurin sauya kayan jikinsa da na jiya da yayi hanging ya fice, 5mnt kawae ya ɗauka sae gashi da sauri ya ɗauko wata abaya ya ɗora mata akan kayan jikinta ya saɓeta yaxo ya sakata bayan motar ya koma ya ɗauko himar ɗinta yaxo ya lulluɓa mata
Manipal hospital shi ke kusa dan haka anan suka tsaya nurses ɗin da sukaxo ɗaukarta daya hango tun yana mota yasa yana fitowa ya saɓi abarsa yayi gaba suma sae suka mara masa baya, ''its so early most doctors didn't arrived sir'' cewar wata doctor data kwana
''what about u? aren't u a doctor?''
''yes i am'' kallonnan na 'then' ya mata daya sata saurin gyara glass ɗinta tana cewa
''i can't attend a patient'' kafin ma yayi magana ta wuce da sauri, kallon nurses ɗin da sukayi cirko-cirko yayi shi a ƙa'idarsa kwata-kwata bayason saka kansa on others business amma babu yanda xaiyi yau hannunsa ya sa ya xaro I.D ɗinsa ya miƙa musu
Ɗan jujjuyawa tayi tana buɗe idanunta, biji-biji ta fara gani saboda nauyi da sukayi sakamakon ciwon kae mae tsanani na kukan da ta sha, akan fararen farcinansa da suka xagaye baƙin hannunsa idanunta suka fara sauka, mini Qur'an ne a tsakiyar hannun yana karantawa, ƙara motsawa tayi tana kallon saman ɗakin dan tasan nan ba hut ɗinsu bane dan katifarta tafi wannan laushi nesa ba kusa ba
''u wake up?'' kanta ta jinjina masa batama ji sanda ya taso ba sae maganarsa da taji a kunnanta
''ok toh bara a haɗa miki bath, what do u want to eat sae na kawo miki''
''bana son komae kawae Abby na nake so'' ɗan dafa forehead ɗinta yayi ya taɓa gashin gaban kanta yana saddowa a hankali yace
''indae tanaso taji Abby toh dole tayi wanka ta rama sallahnta taci abinci then..'' jin bae ida ba yasata saurin ɗaga elbow ɗinta alamar 'then what'
''then baxata ji Abby ba, I won't call him'' bakinta ta tura tana yin narai-narai da idonta kamar wata yarinya ƙarama tace
''toh amma fa kamin alƙawari''
''idan kinyi wanka baa, who will talk to ƙaxama wacce batason wanka''

idanunta duka ta fiddo jin abunda yace mata shima idanun ya xaro yana karkaɗa mata kae alamar haka ne
Miƙewa tayi saboda babu inda yake mata ciwo in ba kanta ba, jin kamar wani xare-xare a ƙafarta yasa ta kae hannu xqta janyo lemar da taji ya sata ciro hannun, wani irin xaro idanu tayi tana ɗaga kanta ta kallesa ganin hankalinsa baya kanta da sauri ta wuce toilet ɗin, duk abunda take yana kallonta ta gefen ido ɗan murmushi kawae yayi
Tana xaune tsakiyar gadon shikuma yana daga tsaye ya dafa plot na gadon idanunsa akan wayarsa da yake kiran number Abby nata idanun kuma na kansa tana sipping tea, ɗaga kansa yayi yana sauke hannunsa ya kalleta bakinta ta tura tana kallonsa shima nasa ya tura yana girgixa mata kae
''amma karki damu nasan xai kira ltr''
''toh yaushe xaka sallameni?''
''Sallama kuma? ni ɗin ne xan sallameki?''
''ahh mana kaene fa kayi attending ɗina waye xai sallameni bayan kae'' xaiyi magana aka turo ƙofar wani doctor ya shigo, hannu suka bama juna cike da mamaki doctor ɗin ke cewa KONTO
''whatsup my guy? i've try to reach you after getting the information about your landing but the number we used to talk with when you're around doesn't reached''
''yaa i discarded the sim card, u know am a married man now I can't keep hanging around with bachalors'' baki Dr. Arsha ya buɗe cike da mamaki wanda ni kaena mamamin ya kasheni wae yau KONTO ne.....
''KONTO!!! when have you became this'' Dr. Arsha ya fqɗa yana kae masa duka a shoulder ya kauce yana dariya da nuna masa adawiyah da ta saki baki cike da mamakin daya hanata magana 'dama haka yakeda sakin fuska?, wae tsaya ma yana da abokanae ne? yana wasa irin haka da mutane dama? gaesheta doctor yayi yana tambayar jiki
''in amsa masa?'' kallonta KONTO yayi da sauri jin wae tambayarsa yau take akan tayi wani abu ganin ta ƙara buɗe idanu alamar dashi take yayi saurin kaɗa kansa yana haɗiye saurin dariyarsa da bae ƙarasa ba
''big sis how u feeling?''
''am feeling better doctor''
''gud, is there anywhere you doesn't found as before? is somewhere in your body paining u?''
''no am completely recovered''
''yah i see but am not surprised because.....'' yana maganar ya tsira yatsarsa ɗaya yana ɗan juyawa kaman mae hajijiya da sauri KONTO ya koma gefen gadon yana cewa
''don't point that stupid finger of urs in me'' baki Arsha ɗin ya taɓe daga farko sae kuma ya saki murmushi yana sauke yatsar
''you say you're comfortable now right?'' ya faɗa yana kallon ta, kanta ta jinjina masa
''so no need to undergo a test?''

''yes doctor but do u check him too?''
''who?'' da idanunta ta nuna masa KONTO da ya nutsu yanata danna waya bae ma ji ba, sae ji yayi kawae an jasa an xaunar da shi akan plastic chair
''hey''
''what should I check?''
''his temperature i think he's running fever on his body''
''mene lfy ta klau fa'' bakinta ta ɗan gwaɓe tana karya wuyanta, Thermometer Arsha ya ɗauko yaxo ya kama gaban rigar KONTO ɗin da sauri ya riƙe yana cemasa
''kae ɗan iska ne?'' baki Arsha ɗin ya karkaɗa yana girgixa kae, da ƙyar ya samu ya saka masa ita
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 13
Typing.....✍
''am asking for your permission sir, i wan't take my thermometer'' hararansa yayi yana xarota ya miƙa masa, dubawa yayi ya juya ya nuna mata ganin temperaturen KONTO ɗin is normal yasa yace bari ya sallamesu kawae, har bakin mota ya rakosu yana gaisawa dasu yones, tsaye KONTO yayi saeda yaga shigarsu duka sannan ya juyo yana kallon Arsha buɗewa KONTO ɗin yana miƙa masa hannu
''this is the key proprietorial pass for the villa door'' karbban pass ɗin yayi yace
''thank u mah boy, see y''
''we'll meet up before down I'll came to overcheck on my patient insha Allah''
''insha Allah'' side hug sukayi ya shige motar suka wuce
Tayi tunanin khimsar xasu koma sae taga sunyi wata hanyar daban ɗan kallonsa tayi amma batayi magana ba har sukaxo wani kyakyawan estate, as usual daga ita sae shi suka shiga yana riƙe da hannunta har ƙofar
''wait lemme open it'' xaro pass ɗin yayi ya danna yana gama scanning ya tura mata ƙofar yana kallonta
A hankali ta shiga ciki tana kallon cikin falon, kamata yayi ganin tayi tsaye yayi tunanin kasa tafiyar tayi ya wuce da ita har ɗakin
''ki samu ki huta koh, bara na watsa ruwa'' kanta ta jinjina masa tana kallonsa har ya fice ɗan komawa tayi ta kwanta sae kuma da sauri ta tashi tana wucewa toilet
8:17 doctor ɗin yaxo a lokacin suna dinner sanin halin KONTO yasa yayi

xamansa a falo bae ƙarasa dinning ba ya jira har suka gama kuma da yake ma a cikin sauri yake yana dubata ya wuce, har ya shigo ma bataji ba shima ganin tayi nisa a tunani yasa bae katseta ba yayi xamansa yana sauya channel abunda ya dawo da hankalinta kenan ta kalleshi da sauri tana gyara xamanta
''Am inaso na tambayeka'' ta faɗa bayan gama mutsu-mutsun da take, hankalinsa na kan Tv ya amsata
''ina jinki'' ɗan kallonsa tayi sae kuma ta miƙe ta ƙarasa inda yake hannun da ke riƙe da remote ɗin ta kama ta ɗorasa kan laps ɗinta tana xama a center table dake gabansa tana cewa
''hankalinka yayi wani wuri kuma ni magana nakeso nayi da kae'' idanunsa da yayi wani wuri-wuri da su ya kyafta yana kaɗa mata kae kamar ƙadangare
''kana ji na?'' kansa ya jinjina, a hankali ta fara magana
''kae kasan Abby fiye da mu yaransa kuma kasan abunda yake sakasa farin ciki saboda da kae yake sharing duk wani joy da sorrow nasa, huuuum inaso ne ka faɗamin abunda xanyi dan gyara tsakanina da mahaifina'' kallonta yake yanajin wani irin tausayinta na shigarsa, shima cikin kwantar da murya yace mata
''nasani nima na sani cewa kune hasken idaniyar Abby babu abunda yakeso sama da yaransa musamman ma ke amma ki sani ko ƙafar son da yakewa bintu baki kama ba, idan har kinaso ki gyara dukkan wasu kurakuranki toh dole ne ki gyara tsakaninki da AUNTY da kuma bintuu har da su meenal dama yaran ɗakin hajiya infact ma duka yan gidanku''
''ae kae ka sani koda xan gyara da kowa banda yan ɗakink.....''
''toh saboda me?'' cikin hanxari ya katseta, itama da yake jira take batasan sanda ta fara magana cikin faɗa ba
''toh saboda me xan shirya da su? waɗannan mutanan sune sanadiyyar yayyena suka tashi a gidan wani uban daban ba abbi ba, waɗannan mutanan suna suka xama dalilin da mamy ta rasa soyayyarta ta shekara da shekaru, saboda Hajiya Babba ne mamy ta ɗanɗani xawarci da ɗacin mutuwar miji, ka faɗamin shin Hajiya Babba ta cancanci mutuntawa koda ta sisin Kobo ne daga garemu? Inda ace ta tsaya a matsayinta na aminiyar mahaifiyarmu taje can ta nemi mijinta da kanta ta aura da duk hakan bata faru ba, da mamy itace uwar gidan babanmu''
wani irin kallo yake mata da idon da bae taɓa kallonta ba, wani irin tausayinta ne yake kwarara a xuciyarsa ganin all this years tayi rayuwa ne cikin duhu ta tashi da tsanar matarda bata taɓa fatan ɓatawa mahaifiyarta rae ba, matar da ta rufe abunda mahaifiyarta tayi mata bata taɓa nunawa yayanta su ƙita saboda past ɗinsu ba, ashe ita abunda aka gaya mata kenan game da baya? lallae tayi rayuwa cikin duhu mutuƙa
A hankali ya fara bata labarin da yayi kama da wanda mamy tasha bata time without number, da farko har ta tsaidashi dan ta san labarinnan dan ta hardace shi ma amma sae yace ta dakata tukun akwae inda yakeso suje, aekuwa ba'ayi nisa ba ta fara jin labari ya sauya itadae tana saurarensa har

ya gama bata kankat labarin ya ɗora da faɗin
''wallahi, tallahi, billahi a abubuwan dana faɗa miki yanxu babu ƙarya wannan shine ainahin gaskiyar da dukkan gidan babu wanda ya santa in kika cire iyayenmu, ni da kuma yayarki Aliyah'' wani irin miƙewa tayi xumbur tana girgixa masa kae da kyar tana cewa
''ban yarda ba, ba gaskiya bane, wannan samm ba gaskiya bane mamy bata yaudari Abby ba ummanah bata aure fiancee ɗin mamanka ba!!'' ɗan runtse idonsa yayi saboda tsawar data masa yana ɗaga wayarsa sama
''kinga nutsu ki kwantar da hankalinki yanxu xakiji gaskiyar lamari, pls ki nutsu'' saeda ta jararesa sannan ta xauna
''Salamu Alaikum Abby'' daga cikin wayar muryan Abby ta fito sanda yake amsa sallaman
''malam Ibrahim ya gidan ya kuma aiki?''
''Alhmdlh Abby.....am..Abby....am eheem Abby dama xan cike wani form ne akan wani tsari na business da nakeso nayi so the file required some headed about father or guardian history am....shine nake tunanin idan nace xanyi amfani dana Dr. info ɗin will be somehow tunda kaga he'snt nigerian kum.....''
''toh in banda abun Khaleel ae da kayi amfani da nawa koh?''
''ehh Abby am about to amma kuma akwae wani wuri da nakeso na ɗan yiwa makeup shine nakeso ka ɗan ƙara bani labarin yanda akayi har ka auri AUNTY bayan mamy ka SO
Tirkashi jama'a😳 yau ranar tonon silili ce da alama bari nayi nan ina dawowa faka-faka🏃🏃
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Assalamu alaikum jama'a nasan xa'a ji book 2 ya ɗan jima shiru banyi releasing ba toh wlh exams muke kuma ansan final Exam yanda take i need to focus on my studies but now that am done insha Allah we'll be back from where we stop

18/1/2024
Page 14
Typing.....✍
Wani irin biji-biji takejin kunnuwanta nayi kamar bataji da kyau ga wani irin juyawa da kanta ya fara duk da haka sae da ta daure ta ida jin ainahin

labarin daga bakin da har abada baxai taɓa mata ƙarya ba, batama isa ba ba'a haifeta ba, hawaye kuwa dama yayi mata jaga-jaga da gaban riga fuskar duk tayi wani ja abunku ga farar fata kafin 10pm wani irin xaxxafan xaxxaɓi ya mata diran mikiya
Shigowa yayi hannunsa riƙe da injection dayaje toilet ya haɗo, yafi ƙarfin 13yrs yana riƙe siringe amma hakanan yakejin wani iri yau da xai mata, dan ko sanda ya mata gyaran hannu Ja'afar ya baewa yayi mata, ajiyar xuciya ya sake yana ɗan jan duvet ɗin fuskarta ta bayyana a dakensa yace
''turn na miki allura'' da ƙyar ta iya girgixa masa kanta tana wani irin nishi, hannu ya saka xai juyota da sauri ta riƙe hannun tana ɗan kwaɓe baki da ƙyar tace
''babu komae a ciki'' ɗan juyawa yayi ya juyo irin ya ɗan ruɗe ɗinnan amma da yake mutum ne mae kamewa bae ma bari ta lura ba kawae ya kama duvet ɗin yana cewa
''ki juya sae na miki, ko na ɗauko miki towel?'' kae ta jinjina masa
''yauwa tashi ɗaura toh'' hannu ta miƙa masa ganin yanda hannun nata ke ɗan karkarwa yasashi fuskewa kawae ɗora towel ɗin a bayanta ya ɗagata dukanta ya xagaya dashi ta baya ya juyata ta koma rub da ciki yayi mata alluran
Da yake ba sallah take ba washegari bata tashi ba sae wurin 9am, tana shiga toilet ta iske ya haɗa mata bath yayi locking glass Jacuzzi ɗin dan kar ruwan yayi sanyi, tana fitowa yana shigowa ɗan kasaƙe tayi da farko while shi ya fuxge yana cewa
''ya ƙarfin jikin naki?'' gaban mirror ta tafi tana buɗe oil ɗinta tace
''naji sauƙi'' ɗan matsawa yayi yana feeling temperature ɗinta yace
''ae har yanxu da sauran xaxxaɓin'' bakinta ta kwaɓa tana kama hannunsa tace
''kaga fa Allah ni naji sauƙi banason ka kuma min allura koh ka bani magani'' kallonta yake har ta kae aya sannan yayi murmushi yana janta ya xaunar a gefen gadon saboda riƙesan da tayi a yanxu yaji yanda xafin hannunta yake shigar nasa hannun
''kinga bara naxo'' daga haka ya wuce gun kayanta daya jera mata a walldrope dan a suit ɗinta da kayan suke
Da kansa ya haɗa mata breakfast ya kuma tayata ci da ƙyar ma ta ɗaure tasha tea daga haka taƙi ƙarawa, shima bae matsaba ba ya kamata ya kaeta kan sofa yaje haɗo mata magana, ɗan kwantawa tayi a sofa tana kallon sama ta naɗe kafarta da teletubbie ɗin jikinta dan avianda cotton trouser and shirt ne masu kauri ya ɗauko mata saboda sanyi
''tashi kisha toh'' ya faɗa sanda ya dawo ya duƙa a gabanta, motsawa tayi tana ƙarfafa kanta ta tashi
''yauwa here'' karɓa tayi tana amsan can ɗin daya buɗe mata daedae an kira wayarsatana ganin ya miƙe ta sha ruwan kaɗae ta miƙe taje ta buɗe back door ɗin apartment ɗin tana kallon ƙasan balcony ɗin yanda mutane keta xirga-xirga kawae ta watsa magungunan ƙasa ta rufeta koma ta xauna

Cikin ikon Allah wurin 2pm wani xaxxafan xaxxaɓi ya rufeta a lokacin ya ɗan je ya dawo tanata juye-juye akan sofa har ta dawo ƙasa sae kuma ga vomiting kafin ma ta kae toilet ɗin dake falon ta soma kwararashi tun tanayi a tsaye har ta duƙa sae kuma ta ɗan ja jikinta tana miƙewa da kyar ta ƙarasa wurin sink ɗin dake gefen falon ta kuskure bakinta, kasa dawowa tayi kawae ta silale tayi kwance anan ƙasa

Babu jimawa ya dawo hannuwansa cike da shopping bags, yana ajiye kayan hannunsa yakejin breath ɗinta sama-sama duddubawa yayi sae ya hangota kwance a gefe da sauri yayi wurin Allah ma ya tsare ya lura da aman da tayi sae ya xagaya ya cicciɓeta ya kae ta kan Couch ya kwantar yana shigewa ɗakinsa

Sauri nayi na runtse ido saboda wata kunya data kamani ganinsa da Armani 3½ with armless red a karo na farko kuma sosae jan kayan suka amshi jikinsa sae ya fito kamar wani ɗan 20, toilet ya fara shiga ya ɗauko towel ya jiƙosa yaxo ya goge mata fuska ya sauya mata wata coat yaxo ya ɗora mata wani ƙaramin towel a ka, da kansa yaje ya ɗauko moper ya jonata anan socket ɗin kusa da inda ta ɓatan ya gyara wurin tsaff ya kunna humidifiers ɗin dake falon ya ƙara mata gudun heater

Kunga miji na gari Lol ??????

Egg wasads yayi ya haɗo mata pan-seared green chilli papper dan ta ɗanji daɗin bakinta ya jerosu a tray ya kawo kan center table ɗin ya ajiye ya jawosa kusa da inda take kwance sannan ya duƙa yana taping fuskanta, a hankali ta buɗe idonta da hawaye ya kwanta a ciki sosae dan doe eyes gareta koya ya sauya colour xa'a gane

''tashi kici abinci'' bakinta ta motsa da ƙyar amma maganar bata fita sosae ba hakan yasashi ɗan matsar da kunnansa kusa da bakinta dan yaji abunda ta faɗa, miƙewa yayi ba jimawa ya dawo da wani bowl da goran ruwa yana xuwa ya ajiyesu ya ranƙwafa ya tadota xaune da kansa ya buɗe can ɗin ya kae mata baki ta kuskure ya ƙara kae mata saeda taji bakin ya mata yanda takeso sannan ya ɗauke abubuwan

Da kansa ya fara bata abincin dan batada ƙarfin ci daga pan-seared ɗin har egg wasads ɗin favourite ɗinta ne, kallon yanda ya riƙe wuƙar yana yanko seared ɗin take komae nasa cikin nutsuwa ba garaje kokuma sauri kuma duka abubuwan da dama yake yinsu idan ya yanka da dama xae maeda wuƙar hagu ya ɗauko pork da dama ya bata da shi, cikin ikon Allah sae da ta cinye tass wasads ɗin ne ma ta rage dan cikin ya cika

''toh sae muxo muyi allura koh'' ya faɗa sanda yake fito da alluran da ya riga ya haɗa daga pocket ɗinsa

''toh wae nafaji sauƙi koka manta ɗaxu nasha magani?''

''au kinsha magani ɗaxun?''

''ji wani tambaya fah! irin bashi ya bani ɗinnan ba ni naji sauƙi basae kamin ba''

''shiyasa naga maganin baeyi aiki ba?''

''xaiyi fa xuwa anjima Allah kuwa''

''inda kinsha koh? ae matsalar da bakisha bane'' idanunta ta xaro waje tana rufe bakinta da hannu, shima idanun nasa ya xaro mata yana cewa

''nasan komae ae nasan kuma bakisha maganin ba''
''kae aljani ne dama'' bakinsa ya tura gaba yana girgixa kansa
''toh taya akayi ka sani?''
''saboda nan ba nigeria bace shiyasa na sani, maintainance office ne suka kirani daga chan ma nake, sunce nan ba Mumbai ko Madras bace nan rajsthand ce so suna maintaining healthy issues, shine naje na amsa query akan magungunan da kika xubar ta balcony'' wani irin tsumu-tsumu tayi tana kallonsa dan har taji xaxxabinta na neman komawa sabo
''yanxu ya sukace?''
''task, juya na miki alluran mana''
''amma a hannu xakamin koh?'' ta faɗa tana ɗan marairaicewa
''kin taɓa ganin anyi alluran masassara a hannu ne?'' bakinta ta buɗe cike da mamaki tana cewa
''kaee a ina ka iya hausan Zamfara'' kafaɗubsa ya ɗage yana taɓe bakinsa yace
''nida nakeda mata wacce ta xauna a Zamfara har an tambayeni, nidae juya na miki'' tana ɓata fuska a haka ya mata aekuwa batayi 5mnt ba wani irin bacci yayi awon gaba da ita, cover yaja mata xuwa ƙirjinta ya ɗan shafa fuskarta yace
''rigimanaaah sleep tight''
Omooo cee luv????
Officialraah444

CHARBIN KWAE ??
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 15
Typing.....✍
Jinyar kwana 3 tayi ta dawo garas period ɗin tare suka tafi da xaxxaɓin da yake bae kuma barinta yin kuka ba da ta taso masa da tambaya xai haɗe fuska yace ta masa shiru kuma sae tayi shirun kamar ba ita ba duk tayi wani sanyi
Yanxun ma a tsaye take a kitchen dan yunwa takeji kuma ba komae take ci taji daɗi ba, toh da yake akwae sauran grocceries a gidan wata simple rice ce ta dafa da green beans sae spices kaɗan, tana cikin ci ya dawo daga inda yaje ɗin
''welcome'' ta faɗa tana kallonsa yana jona wayarsa a chargy
''yauwa sannu da gida madam'' murmushi tayi tana ɗebo abincin a spoon ta miƙe masa tana cewa
''Bismillah kaci abinci toh'' murmushin ya mayar mata yana saddowa ya buɗe baki ta xuba masa (readers gulma na ciciya na fa????)
Wanka ya shige yayo dan tun safe ya fice sae a lokacin wurin 2:30 sannan ya dawo, wani ash cotton trauser ya saka da white shirt irin wannan ƙatuwar mae

uban faɗi kaman buhu wandon ma sakwa-sakwa ne sae roba daga ƙasansa (nifa na kasa ganewa saboda idan kun lura shifa KONTO baya saka ƙananan kaya kullum manyan kaya ne a jikinsa koh jallabiya koda kuwa a gida ne, toh yaushe har sukayi irin sabonnan ne¿?)
''ya Allah'' ya faɗa yana faɗawa kan bed ɗinsa dan da gaske ya gaji ga kuma wata irin yunwa da yake ji amma har ga Allah ya gaji da cin abincin indiyawannan, ɗan turo ƙofar tayi da sallama amma bata shige ciki ba kanta kawae ta leƙa tace masa
''na kawoma abincin ne?''
''akwae saura ne?'' ɗan shiru tayi tana kallonsa sae kuma ta juya ta fita ba jimawa ta dawo hannunta ɗauke da babban tray, anan ƙasa ta ajiyeshi tana miƙewa tace
''gashinan kaci idan ka gama ka fitomin da kwanukan'' daga haka ta juya ta fice
Da saurinsa ya sauko ya ƙaddamar wa abincin duk da a ido bawae yayi kyau bane amma a baki the taste is different, tana tsaye tana wanke-wanke ya kae kwanukan yana ajiyewa ya saka hannunsa yana mata ɗauraya, ɗan kallonsa tayi da mamaki sae ya sakar mata murmushi yana hanging plate ɗin daya ɗauraye a rope ɗinsu itadae tanata kallonsa har ya dawo ganin kallon da take masa ya sashi kae forehead ɗinsa ya ɗan bugashi a nata, murmushin da bata shiryaba ta sake tana maeda hankalinta ga aikin
Da dare tana kwance a gado tana game ya shigo, kallon rigar jikinta yayi silky gown ce har ƙasa amma fa duk tayi kwance a jikinta shikuma mutum ne da bayason matsawa a rayuwarsa hakan yasa cikin sanyi da wayo irin nasa yace
''jibi nake saka ran xamu koma gida fa'' ajiye wayarta tayi da sauri tana cewa
''da kyau, dama ni na gaji da garinnan gwara mu koma gida wata huɗu mutum bata ganin yan gidansu''
''ehh shine nake tunanin this's the perfect time da ya kamata muje shopping amma inaga xanje ni kaɗae saboda dare da ke ƙarayi tunda baki shirya ba'' miƙewa tayi tana cewa
''bani just 5 minutes ina xuwa''
Aekuwa in 5mnt ɗin ta fito sanye da Turkish Abaya maroon wacce ta ƙarɓi fatarta fiye da tunani (just pictured a fair lady wears red) tunda ta fito har suka shiga motar kallonta yake shi irin basarwa da maxa suke idan mata suka kamasu suna kallonsu ma bayayi da ta haɗa ido da shi sae yayi murmushi ko ya mata wink da ya gaji kuma kawae hannunta ya kama ta ɗago da sauri tana kallonsa ƙasa sosae yayi da muryansa yace
''baxan iya ɓoyewa baah kinyi kyau mutuƙa, kwalliyarki tana ɗaukan dukkan brain ɗina, i can't stop staring'' xatayi magana suka iso 'zeelo ka sahar market' dole shiru tayi suka fice
Sosae kasuwar ta mata kyau ɓangaren lehenga ta tafi bayan ta samu ya sake mata hannu akan taje ta xaɓi abunda take so duk da dare ne amma wurin kamar safiya, India isn't her fav country cox tana mata kallo kaman naija dan haka lehenga ta ɗauka sae ta duba masa Pakistan na maxa ta taho gun cashier suka haɗe abubuwan data ɗauko ta nuna masa kansa ya kaɗa yana fito da

hannuwansa daya ɓoye a baya ya nuna mata warwarayen daya ɗauko kala biyu maroon and coffee, shes'nt font of abun hannu amma hakanan yau batason tace masa a'a dan haka hannu ta basa ya saka mata abun hannun ya ɗauki hannuwanta sosae kuwa, daganan wani shagin suka kuma shiga, in taƙaice muku dae sosae sukayi siyayya dan basu samu komawa gida ba sae wurin 12pm
Suna isowa sallama kawae sukawa juna suka shige dan sun riga sunyi dinner kuma duk a gajiye suke ko buɗe shopping bags ɗin basuyi ba anan falo suka barsu
Suna xaune akan bench a cikin airport ɗin hannunta riƙe da wayarsa da ta kira Aliyah suna magana yayin da shikuma yayi relaxing a bencin ya maeda duka hannuwansa baya ya ɗaga kansa sama idonsa a rufe yana sauraren wayar tasu, gaba ɗaya xaƙin muryanta is taking him somewhere else har ta gama bae ankare ba saeda ya fara jin ƙaran Flash kota ina da sauri ya ɗago toh da yake ta tashi tsaye ne ta matsa gabansa sosae saboda fuskarsa da ya ɗage sae ta matsa xata iya ɗauko fuskar da kyau, ɗagowar da yayi ita kuma sae tayi baya xata faɗi dan kansa ya ɗan tureta da wani irin speed ya janyota sae ta dawo jikinsa instead of ƙasan da ta kusa kaewa
A jirgin ma haka ya dinga tarairayar ta itama duk abunda ya mata sae tayi murmushi unlike before da bae ma samu damar hakan ba, duk a gajiye suke kuma a Lagos suka sauka, wata quite area aka nufa da su wurin luff dashi blooming flowers everywhere gidan nasa kamar wani Singapore Bay
Masha Allah munje yawon buɗe ido mun dawo lfy ??
Officialraah444

CHARBIN KWAE ??
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 16
Typing.....✍
A daren da suka dawo ɗin yana xaune akan Couch jikinsa sanye da denim jeans yellow iya kwabri laptop ɗinsa a tsakiyar laps ɗinsa ya ɗan rufeta kaɗan wayarsa kare a kunne da alama waya yake, ajiyar xuciya tayi bayan ta gama kallonsa a hankali ta tako har wurin Couch ɗin ta tsaya tana ɗora hannayenta duka kan fingertips ɗinsa tana wasa da su, kasa ci gaba da wayar yayi dole sae kashewa yayi yana kallonta
''amm ummm nace gobe xamuje Abuja ne?'' kae tsaye ya girgixa mata kansa yace ''ba xamuje gobe ba''
''dan me baxamuje gobe ba? nidae gaskiya inaso naga mamynah besides ni bana

son Lagos''
''akwae dalilin rashin xuwa goben kuma nasan kema da kanki xakiso wannan dalilin'' kamar xatayi magana sae kuma kawae ta juya tana cewa
''sae da safe toh''
Washe garin kuwa wurin 9am sae ga ya Usman da iyalansa, sosae abun ya bata mamakin dan ita daya shigo yace mata ya Usman yaxo bata yarda ba, a lokacin tana tsaye a kitchen tana wanke kwanonin da suka ɓata dan da kanta tayi girki, rasa inda xata sa kanta tayi tsabar daɗi, wuni cur suka mata sae 5 suka tafi
Washe gari kuma sae ga Aliyah da nata yaran habawa ae kamar an tsunduma ta aljannah sosae sukasha firan yaushe gamo khadeer kuwa da ya fara rigima koshi koh Aysha xatayi sauri ta runguma, itadae Aliyah murmushi kawae take tana bin ƙanwarta da kallo, tare sukayi girkin rana suka kuma gyara gidan, wurin 4:18pm sae gashi a gurguje ya gaeshesu da gida yana janye hannun Aysha data rike masa ƙafa yace
''kuɗan min afuwa nayi sallah kunji banyi Asr''
''yo meya ɗauke wa ya Khaleel hankali yau baeyi sallah a lokaci ba?''
''wlh kuwa mom boy wani wuri ne mukaje ban samu kaena ba tun safe, so sae a hankali dae, bara na watsa ruwa nayi sallahn ina xuwa''
Ganin kusan 1 minute da shigewarsa bata tashiba sae ita Aliyahn ta miƙe da kanta ta haɗa masa abinci a babban tray ta ɗauko ta ajiye a ƙasan kujeran da adawiyahn take tana cewa
''gashinan namiki rabin aeki sae ki ɗauka kije ki kae masan'' da sauri tace
''baece xai ci ba ae, bayajin yunwa''
''bayajin yunwa? kin shiga cikinsa kin gano ne? ke dallah bana son shirme tashi kije ki kae masa abinci kinaji yace ko sallah baeyi akan lokaci ba'' bakinta ta buɗe xata mata rashin kunya jin a yanda take mata magana sae kuma ta turashi gaba tana sauke khadeer ta ɗauki trayn ta wuce part ɗinsa
Yana tsaye a gaban mirror ɗin falonsa jikinsa ɗaure da towel yana shafama kansa wani oil ta shiga, da sauri ta juya tana cewa
''sorry bansan kana falo ba''
''it's ok ki shigo ki ajiye mana''
''ka saka kaya'' kallon cikinsa dake motsin yunwa yayi ya ɗaga kae ya kalleta yace
''banda kaya anan ae''
''toh ka koma ciki koh''
kaucewa yayi da yake madubin a kusa da ƙofa ta bayan kujerun sa yake sae ya koma tsakiyar kujerun daga gefen TV ya bata hanya, aekuwa tana ajiyewa da sauri ta juya dan barin ɗakin sae ta ganshi tsaye a gabanta ajiyar xuciya ta saki da sauri tana cewa
''xann..wuce'' kallon fuskarta yayi yana haɗiye dariyar da ke taso masa saboda tuna wancan lokacin da yayi
''Aliyah ta bada ki kawomin ne?'' da sauri tace
''me kake nufi'' kafaɗu ya ɗage yana cewa
''gani nayi taxo sae nayi tunanin idean ta ne kawo abincin''

''kana nufin kenan ni bana baka abinci?''
''atoh'' hakananan maganar tasa ta bata haushi, sae ta juya tana cewa
''let me carry it o.....''
A hankali ya rungumeta yana sakar mata ?? a wuya yana saka kansa jikin wuyan ya lumshe ido, itama shirun tayi tanajin yanda sanyi fatarsa yake ratsa singalalin hannuwanta dan hannun cap ne da rigar jikin nata, miƙis dukansu sukayi wurin 1minute yana ƙara nitsa kansa cikin gashinta
''karkiyi fushi kinji wifeee'' wani irin lumshe ido tayi tanajin saukar maganarsa a ƙofofin kanta, juyo da ita yayi yana grabbing waist ɗinta yace
''wasa kawae nake ƙoƙarin miki fa, kinsan i didn't mean what i said''
''kaje ka saka kaya toh'' kamar wanda wuta ta taɓa ya saketa lokaci ɗaya yana wucewa ciki, ajiyar xuciya ta sauke tana xama a ƙaraman freezer dake kusa da ita ta jimƙe tafin hannuwanta cikin na juna
Long sleeve set ya sako red yaxo ya xauna a ƙasan yana kallonta, itama ganin a ƙasa ya xauna sae ta ɗauko xuba masa komae taxo ta rinƙa jerasu a gabansa har ta gama
''kaci, ni bara naje gun Aliyah'' ta faɗa xata juya yayi saurin cewa
''amm kinga'' tsayawa tayi tana kallonsa, ɗan sosa kansa yayi yace
''ki ɗan tsaya ma toh, inaso muyi magana da ke ne''
Hakanan abunda ya faru ranar da ta fara mantawa da kuma abunda ya faru a moment ago suka hanata nutsuwa, da a ƙasan xata xauna sae kuma ta kasa ta koma kana kujeran dake gefensa na dama yanda baxai rinƙa ganinta sosae ba ta xauna tana wasa da fingers ɗinta, shiru-shiru baeti magana ba sae cin abincinsa yake ita kuma gashi so take ta koma ɗan motsawa tayi ta kalleshi a hankali tace
''inaso na koma gun Aliyah kartaga na jima'' ajiye spoon ɗinsa yayi ya juyo gaba ɗayansa ya kalleta kusan 4sec sannan yace
''mutum nawa ne tsakaninku da Aliyah?'' ɗan shiru tayi tana tunani
''amm kaga khaleed, Ja'afar, mammadu sae Aadii, hudu kenan''
''wato ke yarinyarnan a taƙaice ma ke incomplete ce''
''incomplete kumaa?''
''ehh mana incomplete kinga fa yayyenki 7 sannan a giun Abby kece ta 30 yayyenki 29 ƙannenki 3 kinga kenan incomplete ce ke'' kallonsa take tana motsa bakinta, yana kae aya ta sheƙe da dariya harda su taɓa hannu da su dafe ciki
''toh ae gwara ni kae fa kaene babba kuma ƙanwarka ɗaya kuma kaene kaɗae namiji kuma kaene kaɗae bakada ɗa ko ya kum.....''
''kae a'a, kuma kaene, kuma kaene nifa har na gaji da ji komae ni'' ya faɗa a shagwaɓe, idanunta duka ta fitar waje sae kuma ta kwashe da dariya hada wani jan kae tana cewa
''wae dama kaema ka iya shagwaɓa ne?'' janye kayan abincin yayi gefe ya harɗe hannunsa a ƙirji yana kallonta ƙasa-ƙasa
''kin iya dariya irin haka dama'' ya faɗa ganin dariyar taƙi tsayawa, ajiyar xuciya ta sauke tana saukowa ta fara tattare dishes ɗin
''bara naje nabar Aliyah ita kaɗae''
''am yauwa ae bamu ida maganar ba koh?''

''wacce maganar fa?''
''wacce muka fara yanxu, meyasa kike kiran sunan yayyenki kae tsaye, i mean ga mom eesha bafa immediate sis ɗinki bace she's your superior amma kina kiran sunanta directly wich is not gud'' shiru tayi tana kallon ƙasa
''kinga ni da Mustapha shekara wurin 5 ne a tsakaninmu amma bana cemasa haka broh nake cemasa, sannan ni da usman ɗinku shekara wurin 3 ce shima kinga ae bama faɗar sunan juna'' shiru
tayi tanajin duk ta muxanta shima hakan da ya gani ya sakashi ƙara yin ƙasa da murya yace
''kinga ranar kin min alƙawarin you will set all the differences bitwin u and u'r siblings dan Allah wife badan ni ba just this once ki kira Aliyah da yaya kinji my love''
??????
Officialraah444

CHARBIN KWAE ??
(Janka sae maen nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 17
Typing.....✍
Fitowa tayi da trayn a hannunta, Aliyah bata falon hakama yaranta cikin ɗakita dubasu basanan bedroom ɗin gefe duk basanan da sauri ta ɗauki wayarta sae kuma ta ajiye tuna babu nigerian card a ciki, kitchen ta je kae kayan dan ta koma gunsa ya kira mata Aliyah sae tajiyo kamar hayaniya daga backdoor da sauri tayi wurin tana jan ƙofar amma da alama an ɗan jima ba'a buɗeta ba dan ta cije, dole ta fita ta xagaya ta bayan, aekuwa sune suketa wasa a tsakar gidan Aliyah kuma tana kan wata rope chair dake nan garden ɗin
''haiii wallahi duk kin tayarmin hankali'' ta faɗa tana yarfe hannu sanda ta iso itama tana jan kujera ta xauna, ɗan kallonta Aliyahn tayi for some secs ta maeda hankalinta kan wayarta tana cewa
''ehh mun gaji da xaman cikin ne shine muka fito musha fresh air'' sadda kanta tayi tana wasa da fingers ɗinta hakanan taji wata irin kunya ta lullubeta tunowa da daɗewar da taje tayi agun KONTO wanda ita tama manta saboda ruɗewar rashin ganinsu
''amm.....am....mmm..'' ɗaga mata hannu tayi tana kallonta tace
''kinga! yaushe kuke saka ran xuwa Abuja ne?'' still toeying her fingers she said
''nima dae ban saniba''
''why didn't u ask him'' bakinta ta taɓe tana girgixa kanta
''u better know so that u can prepare peaceful''
''Ali....am ya Aliyahh'' ta faɗa tana ɗan karkata kanta data sadda ta kalli Aliyahn

da gefen ido
''menene?''
''amm.....in.in ina c..ewa will mamy be happy when she see me?''
''of cause she'll''
''amma everything seems right sanda munacan idan na kirata but now am feeling as if kar na haɗu da ita'' da sauri Aliyah tace
''inji waye? wae shin kin manta ne you're mamy's fav fa, karki manta har kishi muke da ke lokacin kina yarinya muyita dukanki idan mamy bata kusa idan ta dawo kika faɗa mata sae ta rama miki, dan haka har abada ke ɗinnan babynta ne sannan kene babban treasure ɗinta, so?'' ta ƙarashe tana ɗaga mata gira tare da buɗe mata hannayenta cikin sauri ta shige tana dariya tace
''thank u so much cwt sis, thank u yaayah''
Shafa bayanta Aliyah take cike da tausayi yarinya tun tana ƙarama an mayar da ita kamar wata taɓaɓɓiya an ɓata mata rayuwa yanxu kuma data haɗu da tsanin da xata taka rayuwarta ta inganta anaso a hanata samun hakan after all, she doesn't want whatever mamy wanted to do to happen, so xata kare yar uwarta baxata bari rikicin mamy da mutane ya ƙara shafar yar uwarta ba kuma
Sakin curtains ɗinsa yayi yana juyowa daga gun tagar shi ƙadae yake murmushi duk da baeji abunda suka tattauna ba amma yanada tabbacin wata muhimmiyar magana sukayi wa juna kuma da alama hankalin Adawiyah ya kwanta
9:34pm khareem yaxo ɗaukarsu daga guk aeki nan ya taho direct, lokacin aun riga sun gama dinner amma KONTO da Aliyah suna kan dinning ɗin da alama wata maganar suke ita kuma tana tare da yaran sunata Mario game a iPad ɗinsu bacci duk ya ɗaukesu sae ita taci gaba da bugawa abunta, da yake gidan is so deep yasa su basuma ji isowarsa ba sae da yayi knocking daga inda suke xaune take tambayar KONTO ko xa'a kawo masa wani saƙo ne, a'a yace mata sae kawae ta miƙe tana gyara scarf ɗinta taje ta buɗe
''au Ya kaene?'' ɗan shiru khareem ɗin yayi da farko amma jin ta ƙara maemaeta the same abunda tace yasashi kaɗa kansa, ɗan janye masa tayi ya shige
''Aly your baby is around'' da ƙarfi ta faɗa yanda har wanda suke daga wajen ƙofar xaku iya ji, juyowa sukayi suna masa welcome
''babe how's u'' Aliyah ta faɗa tana grabbing hannunsa sanda ya isa dinning ɗin ya tsaye suke gaisawa da KONTO
''amm ka jima wlh, i didn't expect you to be that late'' ta faɗa tana miƙa masa ruwa, kafin kuma yagama sha har ta fara xuba masa abinci
''bara naje falo mu gaisa da yarancan kuci gaba da magana kawae'' ya faɗa yana ɗaukan abincin
''aah kayi xamanka kawae idan ya gama na dawo muyi maganar''
''togh kuma banda abun KONTO muda xamu wuce gida dana gama kawae ka xauna kuci gaba da maganarku bara naje gun yarana da ƙanwata nima'' daga haka yayi falon
Kasa jurewa dukansu sukayi daya ɗan ɗaga kansa dan yayi magana da adawiyah sae ya kallo matarsa har kunya ta fara kama ta, shima KONTO ɗin yana lure da su saboda yana mata magana ne tana ɗan juyawa tana kallo mijinta, shikuma

mutum ne a rayuwarsa bayason takura ma wani dan haka yayi cutting chat ɗin short yana miƙewa itama kaman jira take ta miƙe da sauri tana ƙarasawa kusa da shi
''bae na gama maganar'' ta faɗa tana goge masa gefen baki da hannu, abincin da ya ɗebo sanda take maganar ya xuba mata a baki tana kae aya sae suka saki dariya da sauri adawiyah ta ɗauke kae sae suka haɗa ido da KONTO da yake pretending as yana danna waya da sauri kowa ya ɗauke kansa
Suna tsaye daga jikin mota suke magana chan ƙasa sukuma maxan suna magana ne akan wani company adawiyah na saƀe da khadeer ita kuma Aysha na hannun mijinta, saeda suka gama maganarsu almost 11pm sannan suka wuce, juyowa tayi tana hura iska a bakinta, shima juyawar yayi suka soma takawa xuwa ciki
''amm mu xauna na ɗan lokaci a wajennan mana'' ta faɗa tana nuna masa inda lilo suke, bakinsa ya ɗan haɗe yana kaɗa kansa suka yi wurin kamawa tati ta xauna tana riƙe igiyoyin ganin yayi tsaye yana kallonta ta ɗan tale lips ɗinta da ido ta masa alaman ya xauna mana
Ummmmm me xa'a tattauna out of moon ne?□□□
Officialraah444

CHARBIN KWAE □
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 18
Typing.....✍
Bakinta ta ɗan tura gaba tana taƀesa ta kalli sama yanda wata ya fito tarwae
''ahhhh ina son farin wata'' ɗago kansa dake ƙasa yayi yana kallon yanda take kallon sama, ɗan kauda kansa shima yayi yana wasa da fingers ɗinsa
''me kake tunani a game da ni?'' ta faɗa tana juyowa dukanta ta kallesa sae ya girgixa mata kae alamar bae ganeba
''amm u see me i can't withstand u before i mean i don't like u back then, what about u?''
''about me?'' ya tambaya yana nuna kansa, ɗan murmushi tayi tana riƙe wrist ɗinsa tace
''ehh mana kae, ina nufin kafin muyi aure and abubuwan da suka faru bayan auren and u're feeling towards me before''
''em....u see before we're married i never looked at u with any eye, infact ma ban sanki ba saeda Abby yaxo ya faɗamin abubuwan da suke faru wich is October 7th, so a lokacin abun yayi mutuƙar ɗaga hankalina, gashi na kasa tuna any single abu from u're yarinta, so sae na saka aka turamin pictures ɗinki ina

tunanin xan ganeki but unfortunately..... xuciyana is telling me kaxo 9ja kaga wace yarinyarnan da har take tayarwa da mahaifinka hankali, so bayan naxo i start watching your moves without u noticed nasan almost everything da taimakon yayyenki tun daga kan Usman har Adeel mutum ɗaya ne yaƙi yarda shida muh'd, u know? that guy have incredible love for u yace indae abun xaiyi hurting nake he's out, so we count him out and start our moves wanda har ya kae mu ga aure''

Juyowa yayi ya kalleta jin tayi shiru, a hankali itama ta buɗe idanuwanta dake lumshe tana saurarensa suna haɗa ido ta sakar masa wani busashen murmushi tana cewa

''kenan an sakaka aurena that's y ka shirya yanda xata sanni dan kaji idan xaka iya or not? amma meyasa toh ka bibiyeni tunda haɗa abun akayi?''

''saboda na fara sonki a ranar farko da naga pictures ɗinki so a lokacin ban fahimce mene ba saeda naxo muka fara facing juna a lokacin ne na faɗawa kaena 'chill man u've got her' shine babban dalilin bibiyar, kusan komae daya faru dangane da auren Abby da siblings ɗinki ne suka shirya the only thing danasan bamuda masaniya a kae shine wannan pics ɗin da aka mana'' ya ƙarasa yana juyowa ya kalleta girarta ta ɗaga da sauri tana kaɗan kanta ta miƙe tsaye tana kakkaɓe bayanta tace

''toh bara naje na kwanta'' yana daga xaunen ya kaɗa mata kansa shima yana nuna mata hanya da hannu ya ɗora da

''sae da safe?''

''ehh sae da safe'' daga haka ta wuce ciki

Kansa ya maeda yana kwantar da shi baya idanunsa akan☁ abubuwa da yawa suna yawo a kansa game da gidan da yake shirin kaeta gobe batare da ya faɗa mata ba dan yanaso yayi surprising nata amma wannan abun daya faɗa mata yaga kaman ya sanyaya mata jiki sosae

''i will always be there wifey''

Washegari wurin 11am suka ɗauki hanya tanalulluɓe cikin lafaya royal blue and golding shima royal blue shadda ce a jikinsa motar shiru dagasu har drivern sunyi shiru, shi yana meeting ne through MacBook ɗinsa ita kuma tana kwance jikin window saboda batajin daɗi tunda ta tashi cikinta wani iri take jinsa, tun tana saurare har wani bacci ya ɗauketa

Ɗan kallon idanunta da suke motsawa kamar idon ta biyu yayi yana sauko da su kan hancinta data ɗauko sak na babanta sae bakinta dake a haɗe kamar irin an ɓata mata rae ɗinnan, ajiyar xuciya yayi yana tunanin yanda xae tasheta dan ba wani iyawa yayiba yana ɗaga hannunsa muryarta na shigowa kunnansa

''yaaaaa khaleeel'' sunan na gama shigowa kunnansa tana xabura ita kuma da sauri ya tare ta dawo hannunsa tana yamutsa fuska

''sorry are u alright?'' kanta ta jinjina masa tana son barin jikinsa ganin meenal tsaye tana kallonsu tace

''Wae gida mukaxo? bara na fita toh kaema xagaya'' daga haka ta janye tana fitowa, kallon jakarta yayi saekuma ya ɗauka yana ficewa shima

''anty meenal'' ya faɗa yana mata smile, she smiled back and said

''welcome back yayanmu''
''ina godiya my lo.....''
''ga khalilu naa, ga khalilu na'' cewar AUNTY dake fitowa cikin sauri jikinnan yasha ado
''ga Hajiyata'' ya faɗa hugging her tightly, jin tayi shiru ya sakashi janyewa yana kallon inda take kallo daedae Adawiyah data shaya gyara lafayar data tattare tana baro inda motan ta ɓoyeta ta fito fili, kallon kallo sukama juna daedae mamy ma na isowa aekuwa basuyi wata wata ba suka rungume juna (nikuwa nace wata 4 bakwa tare dole)
''mamy how are u?'' ta faɗa tana kama hannayen mamyn, Ummah da tun ɗaxu take kallonta irin kallonnan na ƙurilla ce ta matso tana cewa
''hajiya tunda yarinya taxo ae kamata yayi a shiga da ita koh'' wani irin kallo mamy tajuyo ta mata tana kallon khaleel shima da yaketa gaesheta tun da ta iso
''dan Allah lfy lau'' ta faɗa a ƙage tana kama hannun Adawiyah da tun kwaratsin meenal kanta yake sara mata yanxu kuma different scent da taketa shaƙa yasa cikinta ƙarasa rikicewa burinta kawae su tafi subar compound ɗin, suna fara takawa wani irin vomit taso mata aekuwa ba shiri ta soma kwararashi a gun
A mutuƙar rikice KONTO ya sake AUNTY yayo gun yana taya mamy riƙeta aekuwa riƙetan yayi amfani dan saeda gaba ɗayanta ta galabaece dan ba ƙaramin amae tayi ba, sudae su AUNTY da tawagarta suna tsaye suna kallo hakama mommah dake ƙarewa anyn kallo daga sama xuwa ƙasa tana ƙaryata kanta na abunda take ganowa
''kamata kae ka kaemin ita ɗaki kaji'' mamy ta cewa KONTO tana gogewa antyn forehead ɗinta daketa xufa
''ahhh.....a..xan...iy.a'' adawiyah ta faɗa da kyar tana taka ƙafarta ta soma tafiya
''Rabi'ah ciki ne dake dama'' 😨😮
Pen ɗina ya faɗi bara na ɗauko
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 19
Typing.....✍
Wani irin xabura da AUNTY tayi sae da ta faɗi flat mamy kuwa wani wawan kallo ta jefawa mommah tana ƙarasa matsawa ta rungume Adawiyah cikin jikinta tana yin tofi a gefen Ummah tace
''toh kurwanta kurrr dangin maciya daga isowarta har kin xuba mata ido kina neman makusa kinga yarinya tayi fess shine kike tunanin cikine koh uwar mugun

abu''
''ae bama xai yiwu ba, wannan shirme ne da sakarci ke Amina kamani in miƙe kinji'' inji AUNTY da ta samu nutsuwa
''ke Ummah dama bakinki baya taɓa faɗan alkhairi wlh, yanxu meye haka pls'' cewar meenal sanda take kakkaɓewa AUNTY baya lokacin ma KONTO har yariga ya saɓi matarsa yayi part ɗin mamy da ita
Akan sofa dake bedroom ɗinta ya ajiyeta kamar wata yar ƙwae yana xare mata pin ɗin gefen kanta mamy ta shigo hannunta riƙe da glass cup, da ɗan sauran ƙarfin da takeji kamar yarage a jikinta ta ɗan janye kanta daga lap ɗinsa inda ta jinginasa dan bataso mamy ta gani, mamy kuwa da bama ta wannan takeba matsawa kawae tayi tana miƙa mata ruwan aekuwa sae sa ta shanye kaff sannan ta koma xata kwanta da sauri ya tareta amma kafin yayi magana mamy ta rigasa tana cewa
''kaga ka tafi i will take care of my child''
''toh mamy ae indae tare da ke ne nasan banda matsala bara naje'' daga haka ya juya yana satar kallonta ya fice
''sannu dota, dama bakida lafiya ne?'' cewar mamy tana warware mata laffayar dan tasan halin yarta yanxu haka bata saka kaya a cikiba inears ne kawae a jikin, daƙyar ta iya amsawa mamyn
''yau dana tashi ne naketa jin masassara''
''toh Ilahu ya baki lafiya bara naje ina xuwa koh'' daga haka ta fice, itama nata idon ta lumshe tanajin yanda jikinta ke kwankwatsa har ma bacci ya ɗauketa
Humee taxo ta tasheta akan Abby na falo yace a fito da ita
''humee banda lfy banason fita wlh''
''sannu anty ko na faɗawa Abbyn sae a shigo nan a dubaki?'' samu tayi da kyar ta tashi xaune tana nunawa humeen wardrobe da sauri taje ta ɗauko mata dogon himar taxo ta kamata suka saka
''sannu koh, muje''
''ya banga mamy ba''
''mamy tana falo tare da Abby''
Suna saukowa idonta kan babanta ya fara sauka wani irin faɗuwa gabanta yayi tana shirin sadda kanta ya sake mata wani sassanyan murmushi wanda yasata ɗan ware idanunta, Abby dake kallonta da kyau ya kuma karya kansa yana ware mata hannayensa ae kaman an tsige mata ciwon dan ita kanta batasan sanda ta ganta a gaban Abby ba jinta kawae tayi a jikinsa tana sakin kuka, tapping ɗinta yakeyi yana bata baki
''Abby kayi haƙuri'' ta faɗa sanda ya ɗagota yana share mata hawaye
''dota kema kiyi haƙuri'' da sauri ta riƙe wrist ɗinsa tana girgixa kanta tace
''a'a Abby bakayi komae ba nice nayi laefi kullum inayi ina ƙarawa dan Allah Abby ka yafemin''
''uhm toh ba komae ae''
''Abby a'a ni nasan akwae komae babu abunda banyi babu irin trouble ɗin da ban haddasa ba dan Allah Abby kayi haƙuri, namaka alƙawarin xan...nama sauya xanyi duk abunda kakeso Abby nix....'' bakinta ya rufe da hannunsa ɗaya ɗayan

kuma yana shafa forehead ɗinta da yaketa ƙara ɗaukar xafi
''kefa yata ce kuma halitta mafi soyuwa a gareni, har abada kece abunda nakeso sama da abubuwana da yawa so kiyi shiru kinji''
''na gode babana'' ta faɗa tana kallon Alii da ya shigo shima, hannu ta miƙa masa tana kwaɓe fuska shima fuskar ya kwaɓe yana jan checks ɗinta, wani irin amae dataji ya taso mata sakamakon gaesawar da sukayi ya sata ƙoƙarin miƙewa amma da yake ba ƙarfin kasawa tayi sae ta soma xuboshi duk ta ɓata jikin Abby da yayi sakato suma su mamy duk kanta sukayo suna kallonta
''wae menene yake damunta ne?'' cewar Abby sanda ake kwantar da adawiyahn bayan an gyara mata jiki
''wlh Alhaji ban saniba tunda suka iso take amae tana laƙailaƙaitu amma tace wae fever ne''
''a'a wanne irin fever kuma? baradae na kira najibu muji'' daga haka ya miƙe yana barin falon
Tana daga kwancen tanata juye-juye dan cikin wani iri yake mata Najeeb ya shigo mommah da yan ɗakinsu na binsa a baya, a falo duk suka tsaya sae shi daya shige tare da mamy dan dubata, Abby kuwa daketa faman kiran KONTO dakecan AUNTY ta sakashi bacci kuma ta ɗauke wayarsa ganin anata kira sae ta sakata a silent so batasan duk kiran da Abby ketayi ba
''ke Aysha jeki ɓangaren babarku kice nace taxo'' miƙewa humee tayi da sauri ta fita babu jimawa suka shigo da AUNTY daketa faman rausaya kaman wata gimbiya
''Rabi ina Ibrahim?'' abunda Abby ya tareta dashi kenan yana gyara babbar riga
''Ibrahim yaci abinci yayi wanka shine nace masa yayi bacci ya ɗan rage gajiya''
''toh ki tasosa immediately'' wayarta ta ɗauko tayi dialing number meenal tana faɗa mata taje ta taso yayanta, a fusace Abby yace
''kije da kanki ki tasosa mana!!!" xata juya najeeb da mamy suka sauko sae ta tsaya tana kallonsu kamar yanda duk yan falon sukayi, Najeeb kuwa da dama abunda yakeso kenan ɗan gyara eyeglasses ɗinsa yayi da yake tare suka sauko da mamy so suna kusa da juna sae ya bar wurin yaje ya tsaya daga ɗan tsakiyan falon idanunsa na yawo tsakanin fuskar mamy da AUNTY ya fara magana
''tun ma ban kae ga aunata ba nasan abunda yake damunta, amma duk da haka sae da na aunata so congratulations mamy and Aunt....an u Abby adawiyah is 7month pregnant'' wani irin shiru falon ya ɗauka dan har shi Abby ruwan jikinsa tsayawa yayi
''me naji ka faɗa?'' cewar KONTO dake tsaye a ƙofa shida meenal da basuji farkon ba
''matarka ce keda seven weeks ciki, congratulations Ibrahim'' cewar mommah tanason ganin reaction ɗinsa amma kafin yayi magana Abby daya samo kansa ya gyara hularsa yana miƙawa najeeb hannu yace
''thank u dr. Najeeb, can i go and see her'' kae najeeb ɗin ya kaɗa kamar a hospital yana nunawa Abby hanya da hannu
''u can sir amma dan Allah don't make noise'' da sauri Abby ɗin ya wuce yana tattare babbar rigarsa dan yaji daɗin hawa case, da sauri KONTO ma ya rufa

masa baya shida humaerah ganin haka duk suma sauran suka bisu banda mamy da AUNTY da har a lokacin basu koma daedae ba
''hajiya lfy na ganku haka'' cewar Ummah da dawowar ta kenan aka faɗamata adawiyah ba lafiya tana shigowa kuma ta iske su mamy cirko-cirko, wani irin dogon numfashi mamy tayi tana yin gaba da sauri itama AUNTY tabi bayanta dole tasa ummah mara musu baya itama
Duk su Abbyn na xaune a gefen gado suna kallonta KONTO kuwa na tsaye ta wurin ƙofa, itakuma tanata bacci saboda allura da Najeeb ya mata, Alii ne ya fara fita bayan ya shafa yayarsa sae mamy ma ta juya ta wuce a haka duk suka xaxxare juyawa AUNTY ma tayi tana yiwa KONTO daya xubawa matarsa ido wani kallo ta masa jikinta da bae ida dawowa daedae ba tace
''wuce muje kallon me kake?'' Abby dake jinsu ya juya yana cewa
''matarsa ya tsaya dubawa ke ki wuce ki tafi tunda bakida abunyi mana'' kamar baxata wuceba sae kuma ta ja tsaki a fusace ta fice, miƙewa shima Abbyn yayi yana wucewa ƙofar ya dafa shoulder ɗin KONTO yace
''everything will be alright ok?'' kansa ya jinjina ma Abby dan yasan me Abby ɗin yake hango masa
Allah sarki babana nima har na fara tausayinka wlh dan nasan me xaeje ya dawo😣😵
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Typing.....✍
Ajiyar xuciya mae nauyi KONTO ya sauke sanda ya xauna a gefen gadon yana kallon ƙirjinta dake sama yana ƙasa in speed alamar shes'nt alright, hannunta da yake siriri ya kama yana ɗan feeling pulse ɗinta, idanunsa na kan hannunta da tafin ya ɗan ciko yayi wani irin fari da bae taɓa tsayawa ya lura ba, a hankali tunanin abunda ya faru tsakaninsu a Khimsar lokacin daya faɗa mata abubuwan da bata sani ba, abun isn't intentional wanda har yau dashi da ita sun ƙi su tsaya suyi magana akan abun ma
''Rabeenah, Kyautanah, Abun ƙaunanah, Kayatahh'' sunayen daya faɗa mata kenan yana sakin murmushi for the first time ya ɗora kansa jikin shoulder ɗinta yana xagaya hannayensa ta left side ɗinta yana sakin dariya mae ɗan tsayi
''u are mine completely''
That's how kyautar Allah feels

Baesan ya akayi bacci ya ɗaukesa a wurin ba sae jin saukan ruwa yayi a kansu shida ita wanda hakan ya farkar da su a tare, miƙewa yayi yana kallon mamy dake tsaye riƙe da bucket tanata huci, itama adawiyah mamyn take kallo cike da mamaki tunda batasan abubuwan da suka faruba ita
''har kaxo kana naniƙarta anan koh ka nunawa kowa kae wanne irine bah, kekuma b....Rabi'atu ni xx.xaki...to..xa..r.t'' kasa ƙarasawa tayi saboda wani tuƙuƙin baƙin ciki daketa taso mata
''mamy dan Allah mana, nifa yun.....''
''idan kika sake kika ƙarasa sae na karyaki anan dan u*ki'' idanunta ta xaro waje tana kallon yanda idanun mamyn har wani wuta-wuta suke tarawa
''dan Allah mamy kiyi haƙuri karki mata faɗa kinga situation ɗin a....''
''kyaleta Ibrahim duk yanda xaka mata bayani baxata fahimta ba, tunda kwalwan yarane da ita'' cewar Abby da yake shigowa jikinsa sanye da simple jallabiya da alama bae kuma fita ba
''au Alhaji ya ƙyaleni tunda ga mahaukaciya?'' wani kallo Abby ya mata yana cewa
''ehh, kwarae dalilin kenan, saboda bakida hankali ne nace ya ƙyaleki kiyi haukanki ke kaɗae'' aekuwa wani irin kukan kura tayi tana ɗaga bocket ɗin hannunta Abby ya warce da ƙarfi yana haɗawa harda ita ya riƙeta a jikinsa yana cewa KONTO
''Khaleel ɗau matarka ku wuce kaji'' shima KONTO da abun ya tsoratar da sauri ta kamata yana xaunar da ita ya rungumeta sosae, maids ɗin mamy aka kira da saurinsu sukaje ɗauko mata himar akayi a locker ya saka mata yana kamata ganin yanda taketa kallon mamy daketa xagin Abby tana son ƙwacewa daga jikinsa tayasa sukayi aka fitar da ita, itadae ta kasa magana dan bakinta ma ya mutu da alama
Tasan dama baxasu wuce gidansu ba, dan haka suna isa ɗakinta ya rakata yana xaunar da ita xai fice tayi saurin grabbing hannunsa tana cewa
''wae menene yake faruwa a gidanmu ne?'' xaiyi magana wayarsa ta fara ringing ganin Ummah ke kira yasshi nuna mata yana cewa
''ki ɗan yi excusing ɗina xanje gidan idan na dawo xamuyi magana koh?'' kanta ta kaɗa masa tana cije lips ɗinta na ƙasa saboda murɗawa da cikinta yayi
''yunwa koh?'' kanta ta ƙada masa, sae ya matsa yana kae hannunsa da bata riƙeba ya tallabo ƙeyanta yayi kissing forehead ɗinta yana matsawa ya fice
Saeda taji ta gaji da tunanin sauyawar mamy datake tayi sannan ta tashi ta shiga wanka saboda xafin da yake ta damunta, ƙaramar riga ta saka iya guiwa sky blue kanta da ke kwance ta kame a bant ta ɗaure, fitowa tayi saboda shi bae dawo ba dan haka batama yi tunanin jiran ya kawo mata abinci ba kitchen kawae taje, kusan babu komae ma a kitchen ɗin na ci komae an kwashe sae oils da seasonings Allah ya taimaketa ta samo wata Cherie babba da alama an barta ne a gun kwashe kaya

Da sauri tayi lightening gas ɗin ta ɗora ta haɗa komae ta matsa jikin fridge ta jingina tana lumshe idonta, wani abu ne yake tsikaran xuciyarta kamar kuka na

taho mata amma tana ƙoƙarin mayar da shi saboda alƙawarin da ya sata ta mishi, tayi nisa sosae a tunaninta har batasan shigowarsa ba sae maganarsa da taji a kanta a xabure ta kallesa sae kuma ta kalli girkinta jin ƙaurin da kitchen ɗin yake
''ya ilahi abincina'' ta faɗa da sauri tana kae hannu xata kama tukunyar yayi karaf ya riƙe hannunta yana cewa
''ke xafi fa'' hannun takeso ta ƙwace tana cewa
''wayyo abincina ya ƙone, wayyo ka sakeni'' kallonta yake ganin kamar ta ɗan ruɗe dan har wani hawaye ta fara
''kinaji nutsu mana'' ya faɗa yana karyar da wuyansa dan yaga fuskarta da kyau, cikin kukan da dama take neman hanyar fitowarsa take cewa
''dan Allah ka barni abinci na'' rungumeta yayi tsam a jikinsa yana shafa bayanta
Sosae tayi kuka bae hanata ba shima saeda ta gaji dan kanta sannan ta ɗago tana kallonsa, kamata yayi ya janyo island chair ya ɗorata ya koma ya ɗauko mata ruwa a fridge a cup ya xuba mata saeda ta shanye cup 3 sannan ya ƙyaleta, kneeling yaxo yayi a gabanta ya ɗaura hannayensa akan guiwarta cikin kwantar da murya yace
''me kikeso kici?'' kallon tsakiyar idanunsa take kamar yanda shima yake mata
''duk abunda ya samu''
''xakici awara?'' tsikar jikinta taji ta tashi jin ya ambaci sunan awara
''kasan awara dama?'' murmushi yayi yana nodding
''muje toh kici'' ya faɗa yana kamata suka fita
Tun da ta sako kanta falon wani uban ƙamshi ya mata maraba sosae aromatic scent yake tashi, akan dinning chair ya xaunar da ita da kansa ya buɗe warmer ɗin ya saka spoon yana dauko awaran da tasha grocceries a ciki ga ta soyu da kyau
''a'ina ka samo wannan kayan?'' ta faɗa tana shafa jikin warmern
''daga gida aka kawo''
''gida dae?''
''ehh naxu fitan da nayi naje ne munyi magana da Abby so na tarar sunayin na duka gida shine Hajiya tace in tsaya a soya miki tunda kina so''
''wacce hajiyar?'' ta tambaya idonta kansa
''hajiyan Alii mana'' dan lumshe idonta tayi can ƙasa yanda ita kaɗae xataji kayanta tace
''i also miss ummah''
''kici abincin data haɗa miki xaki rage kewan nata'' kanta ta jinjina masa tana mamakin irin kunnuwan da yake da su, duk yanda xa'ayi magana indae yana kusa toh xaiji, tunda ta kama awaran bata barta ba saeda taji cikinta ya mata wani uban nauyi
''huuuum, bacci'' ta faɗa sanda ta gama hamma, murmushi yayi yana ajiye awaran hannunsa dan shi bae iya ci ba
''ya kamata dae queen tayi bacci kam'' ya faɗa yana xagayowa ta gefenta, kafin ma tayi magana ya saɓeta yanayin hanyan bedroom ɗinta da ita, dariya ta saka tana xagaye hannayenta da wuyansa tayi lamo

****

''Alhaji a kae fa nake magana'' cewar AUNTY dake tsaye a falon Abby tana riƙe da ƙugu, a haka mamy da AUNTYN ce da kanta ta sa aka kirata ta shigo tasha ture kaga tsiya anata taunar chewingum, kallon juna sukayi ita da Abby sae ta taɓe baki tana cewa AUNTY
''lfy Hajiya Rabi kika aeka kirana?'' itama AUNTYN a ɗan fuxge ta kalli mamy tace
''akan maganar cikin jikin yarki ne, dagani har ke babu wacce ke som cikinnan so munyi magana da Alhaji yace shi baxae sakasu su xubar da cikin ba tunda nice kaɗae banaso dan haka nasa a kiraki dan yaji daga bakinki'' wani irin murmushi mamyn ta saki tana mummurxa bakinta tace
''toh in banda abun Hajiya Rabi nice nace miki banason cikin jikin yata? kokuwa nice nace miki ban shirya xama granny ba?'' buɗe baki AUNTY tayi dan yin magana mamyn takuma riganta
''kinga fa yarannan bamu muka basu cikinnan ba Allah ne ya basu dan haka Alhaji indan babu wani ƙwaƙwaran abun faɗaaa nayi nan''
Kuttttt naji da kyau kuwa? Mamy ce fa😮 uhmm I smelled something wallah
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 21
Typing.....✍
Kasa magana AUNTY tayi har mamy ta fice bakinta a sake ta juya ta kalli meenal daketa ƙoƙarin controlling kanta ta dawo da idanunta kan Abby daya juya shima ya haye sama, ganin an barsu su kaɗae yasa a wani irin fusace tace
''meenal muje kiyi driving ɗina xuwa gidan Ibrahim ɗin'' daga haka ta fice meenal na mara mata baya
''mamy saedae fa mu nemi wanda xai kaemu dan baxan iya driving ba'' ta faɗa tana dafe kanta datakejin kaman xai tarwatse, wurin get ɗin mamy tayi tana kiran one of their servant da sauri ya ƙaraso yana gaesheta
''kaje kaɗauko mota xaka xamu fita'' ɗan sosa bayan kansa yayi yana cewa
''amm madama alhaji gave others that u can't go anywhere'' wani irin glance tayi irin 'haaaa' ɗinnan tana kallon meenal da har ta saki kanta data riƙe dan mamaki
''kae bawa! mene kake cewa?''
''order dana saka ni ubanki ake cikawa'' cewar Abby da ya fito dan yana kallonsu duk abunda suke daga window shine ya xagayo

''kae wuce gun aikinka'' da saurin yaron ya jinjina kae yana wucewa
''ke kuma'' Abby ya faɗa yana murxawa meenal yatsunsa a gefen fuskantar ransa a mutuƙar ɓace yacigaba da magana
''nabaki daga yau xuwa sati 5 masu xuwa ki fito da miji, kuma wlh, wlh, wlh idan har baki fitar da bakinki a cikin wannan batun ba wlh ranki xaiyi matuƙar ɓaci'' daga haka ya juya abunsa ya barsu nan tsaye
''mamy wae me yake faruwa ne?'' cewar meenal dakejin duniyar kaman tana juya mata
Mamy kuwa tana komawa falonta ta kira mamman khaulat da itace ta tsara mata yanda xatayiwa AUNTY, mom na ɗagawa ta labartawa mata duk yanda akayi aekuwa mom ɗin ta kwashe da dariya itakuwa mamy da takasa gane inda wannan abun na mom ya dosa yasata cewa
''wae ni dan Allah aminiya ina kikeso ki kaeni ne?'' wani gyaran murya mom tayi tana sakin yar dariya tace
''akwae abunda nakeso ki lura da shi aminiya, kinga dae wannan yaro dake auren yar wajenki shine babban tinƙahon Hajiya Rabi shine abunda kullum take kuri da cika bakin yafi mijinta dukiya hakane?'' kae mamy ta kaɗa kamar suna gaban juna, itama mom bata tsaya jiran jin ta bakinta ba taci gaba
''idan har kika janyo yarki a jiki ku raeni cikinnan tare idan da hali ma ta dawo gunki wannan exercise da sukeyi duka gidan kullum ki rinƙa fita da ita hajiya Rabi ma ganin tulelen abu a jikinta kuma abun y kasance na ɗan da take kurari dashi ne, ke ya kike ganin abun xai kasance?''
''toh meye amfanin yin hakan wae?''
''kae Amina kae, wlh matsalata dake wani lokacin rashin ɗaukar haske, kina tunanin duk wannan soyayyar da Hajiya Rabi ke nunawa Ibrahim itace wacce xata gajesa ne? kifa tuna cikin ɗansa ko yarsa na farine a jikin yar, inaso ki hango mana irin daular da xamu kwasa idan ta haifa masa magada, shin baki hango faɗuwar Rabi ƙasa warwass ba?'' wani irin tamne yatsanta da ƙarfi mamy tayi tana kwashewa da wata irin dariya
Xaune suke a gidansu na Lagos dan sun koma, akan carpet suke xaune gabansu farar shinkafa ce da madara sae grapes da aka yanyanka a ciki tun ɗaxu take cinyewa yana ƙara haɗa mata wani yanxun kuma ya gama haɗawa yana kawo mata ta sakashi a gaba akan shima sae yaci
''kinsan Allah baxan iya cin wannan haɗin naki ba''
''kasan me? yanada mutuƙar daɗi tun ina yarinya shine best abincina shiyasa yanxuma kaga inata ci ina ƙari'' murmushin da baya barin fuskansa idan suna tare yafaɗaɗa cikin magana ƙasa-ƙasa yace
''wato magajiyarki xaki haifa'' ganin tana kallonsa sae ya ƙara sakin dariyar yana cewa
''nifa na cicci sanda ina haɗa miki shiyasa kuma ya isheni'' bakinta ta taɓe tana jan kayanta ta saka hannayenta ta rufesa
''toh tunda dae kace baxakaci ba bari kallemin abu'' dariya yayi yana tsunkulan bayan wuyanta ya miƙe da sauri yana wucewa

''whyy areee uuuuu like thattttt'' ta daɗa da ƙarfi tana dariya
Tunda sukaxo Abuja ake bata wata irin kulawa Abby kullum da safe xaixo hakama da dare sannan yayunta maxa da suke xaune anan Abuja ma suna xuwa wani lokacin daga aeki wani lokacin kuma da safe kafin suje aekin, uwa uba kuma mae gayya mae aikin dan shikam kamar ya haɗiyeta, bata faɗa masa idan tana buƙatar abu dan komae ta saka a cikinta xama yake amma da tsiya ya koya mata kwaɗayi dan kullum sae ya tambayeta idan tanason abu idan tace a'a haka xaiyita lissafa mata abubuwa har ya saka kwaɗayinta tashi, kuma har yau babu wanda ya faɗa mata ga abunda take ɗauke da shi kuma da yake ita ba period takeba bare idan ya maƙale ta gane
Ringing ɗin da wayarta ta fara ne ya sakata fasa tashin datayi niyyar yi dan binsa kitchen, ta ɗauki wayar da sauri ganin mae kiran
''barkanki mamy'' ta faɗa tana tattara dukkan nutsuwarta
''yammatana ykk? koda yake yanxu kin girma tunda har xaki xama uwa kema'' bata fahimci maganar mamy ba dan haka ta shiga gaesheta
''yaya jikin naki? hope dae kina cin abinci kuma bakya laulayi sosae koh?''
''wae mamy koh bakisan wa kika kiraba?'' mamy da dama tasan xa'ayi haka ta kwashe da dariya tana cewa
''kee, karkiji kunyata nifa mamankine kuma tun kafin ki sani na sani ae, nidae fatana Ilahu ya raba lafiya, sannan kuma duk abunda kike buƙata ki tabbatar kin kira kin faɗamin kuma idan kikaji ciwo ko ɗan yayane ki faɗawa mijinki maxa a kaeki asibiti idan baya kusa ni ki kirani ko ki kira babanki'' daga haka ta kashe wayar
Tanajin mamy ta kashe tayi wani xabura tana miƙewa, yana tsaye gaban wash basin yanata goge kwanukan daya wanke, ga kitchen ɗin yayi fes dan duk ya goge inda ya ɓata ya gyara kuma
''ammm.....um..in..aso.....inaso.ka faɗami..n'' juyowa yayi yana kallon yanda tayi wani irin laushi, yasan dole an faɗa matane dan yaji sanda aka kirata dama amma sae yayi kaman bae saniba idanunsa na kan abunda yake yace
''da gaske me?''
''da gaske abunda mamy ta.....'' shiru tayi tana kallonsa, shima abun hannunsa ya ajiye ya ciri tissue ya goge hannunsa sannan ya juyo gaba ɗayanta ya cire daga ƙasa ya xaunar da ita akan kitchen Island ya saka hannayensa ya xagaye waist ɗinta yana kallon cikin idanuwanta yace
''ehh munada cik.....''
''how comes?'' ta faɗa da sauri tana riƙe hannunsa dake jikinta
''kyauta ce, kyauta daga Allah, wanda bamu taɓa tsammani ba infact ma bamu shirya ba kawae Allah ne ya kawosa batare da shawararmu ba''
''hakan yamaka ne kae? kaefa ba sona kakeba taya xaka amshi abu daga wacce bakas..''
''ni bantaɓa ƙinki ba, van taɓa jin sonki ya ragu daga xuciyata daedae da one second ba, nidake duka munsan cewa ina sonki kuma ina maraba da duk abunda xaixo daga gareki''
Takusa 3mnt kafin ta iya dawowa cikin hayyacinta, a hankali ta ɗago

hannunta ɗaya ta ɗora akan cikin hawaye na saukowa tace
''da gaske ne wae?, da gaske xan xama uwa?, nidin? Mamynah xata xama kaka?'' murmushi yamata yana cubbing face ɗinta yace
''ehh ke uwace dana ranar da kika samu ciki''
''me yasa toh ka kasa daena fara'a kana farin cikine har haka?'' dariya yayi har teeth ɗinsa suka bayyana yana matsawa jikinta sosae yace
''extremely!''
Awwn am happy too
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 22
Typing.....✍
Kasa xaune tayi takuma kasa tsaye, hakanan takejin farin ciki amma kuma tana ƙaryata kanta ganin ta rasa abunyi yasata janyo phone ɗinta tayi dialing numbern Aliyah tana kallo kamar idanunta xasu faɗa screen ɗin har kiran ya katse ta kuma aeka mata da wani, wasa wasa saeda ta mata kira 7 har landline ɗin gidanta saeda ta kira bata ɗagaba ɗan tsaki tayi tana jefa wayar akan bed tana wucewa toilet
Tana xaune akan sallaya bayan Asr kiran Aliyah ya shigo cikin sauri ta ɗauka tana kaewa kunne ta shiga gaesheta
''lafiya dae autar mamy tamin kira har haka?'' ɗan shiru tayi tana ƙoƙarin kamo maganar
''bakiji labari ba?'' ta samu kanta da faɗa
''labarin me kenan?'' tasan halin Aliyah da maeda komae wasa sae ta ƀata rae tana cewa
''shikenan ae tunda bakiji ba'' dariyan da taketa riƙewa ne ta fito dagacan tace
''au wae kina nufin da kika kusa xama uwa?'' bakin ta kuma turawa amma batayi magana ba
''kinga toh meye nayin shiru kuma? ko kin manta yanxu ke ɗin kin girma?'' narae-narae tayi da ido muryanta har ta fara ɗan rawa tace
''yanxu Aliyah shikenan komae ya ƙare kenan? burina, fatana, mafarkina and most of all career na, na rasa dukkan wasu burikana xan xama uwa a daedae lokacin da ban shirya.....'' kuka ne ya ƙwace mata kawae sae ta sadda kae tana yi da ɗan sauti
''kinaji Rabi'ah inaso ki saurareni sosae kinji, indae akan old life ɗinki ne

aure babu abunda xai hanaki yi, idan kikaga mace dagayin aure dukkan wani babi na rayuwarta ya tsaya toh daga mijin data aurane, kuma duk namijin da ke sonki baxai taɓa tanƙwafeki daga cika burikanki ba koda kuwa ace karatune kokuma aiki dan haka ki kwantar da hankalinki mijinki ba jinin maxanmu nanan garesa ba sannan yanada ilimi yasan abunda duniya ke ciki, yau KONTO koda bake yake aureba na tabbatar baxae xama daga cikin maxa masu baƙin ciki da cigaban tayensu ba, dan haka ki kwantar da hankalinki kiyi ƙoƙarin xama ta kusa da mijinki ta yanda xaki iya faɗa masa abunda kikeso nasan xae miki'' kanta take jinjinawa Aliyah tanahhoge sauran hawayenta tace
''amma idan kuma Hajiya babba taƙi barifa?''
''wacece kuma hajiya babba a rayuwarki baby? mariƙiyar mijinki ce ba mijin nakina ae, dukda yana binta sau da ƙafa amma karki manta Ibrahim mutum ne mae ilimin addini yasan haƙƙin AUNTY a kansa yakuma san haƙƙinki na matarsa kuma yanda yakeda ilimi yake aiki dashi nasan baxai taɓa cutar da xamanku ba, besides ma cikinsa ne a jikinki fa kokin manta? from the moment u delivered your child shikenan he's yours completely, kuma nasan baxaiso yaronsa ya taso yaga yana tauye haƙƙin uwarsa ba so chill up lady cox you're not a baby anymore'' dariyan da bata shiryaba tayi tana cewa
''kaeee Aliyah''
''ehh mana wannan shagwaɓan duk sae kinxo kin daenata sannan yan gidanku wanda kuke baba ɗaya dakuma steps mom ɗinki dolene kixo ki shirya dasu barinma AUNTY that woman has gud intension towards us nasan kema kin sani'' kanta ta jinjina tana cewa
''insha Allah xan gyara kamar yanda nayi alƙawari''
''masha Allahu maman unboarn ɗinmu, wae!! Allah nuna mana ranar da xamu ɗauki babynki'' ɗan murmushi tayi jin hau exciting yayartata is
''kina farin ciki yaayah?'' dariya sosae Aliyah tayi tana share ɗan hawayen dake maƙale a idonta tace
''ehh ina farin ciki, mutuƙar farin ciki ma, bama ni kaɗae ba duk wasu masoyanmu suna farin ciki hada mamy ma'' wani sassanyan murmushi tayi tana ɗora hannunta kan cikin jin kamar tanajin bacci sae tayiwa Aliyagn sallama tana jefe wayan kan bed sae ga Kiran humee
''toh ita kuma wannan lfy?'' ta faɗa tana ɗaukan wayar ta kae kunnanta
''ina kwana anty'' ciro wayar tayi daga kunnanta kallon screen ɗin tayi tana girgixa kae ta maeda kunne muryanta a sake tace
''ina kikene?''
''Gani a get'' ta faɗa dagacan
''ok toh bara nax....''
''a'a karkixo kiyi magana kawae axo a buɗe mana'' humee ta katseta da sauri jin xata taso, bata tsaya har suka shigo faloba tana bada umarnin a buɗe masu ta miƙe tayi falon tanata xuba uwar hamma
''oyoyo oyoyoooo'' cewar humee tana sakin akwatinta da gudu ta faɗa jikin adawiyah kaman tayi shekara bata ganta ba, ga mamakinta itama antyn

rungumeta tayi ƙam tana cewa
''i miss this trouble maker sis of me'' cike da jin daɗi humeen ke kallonta ganin ta sake da ita, hajjah da keta faman riƙe bako saboda ganin yanda sukeyi kaman ba komae jikin Adawiyah yasata cewa
''keh!keh! A'ishatu ki rufawa kanki asiri nima danaxo dake ki rufamin, zygote ɗin cikin nata xaki xubar?'' itafa sam bata lura da hajjah ba sae da tayi magana, ita kuwa humee da sauri ta saketa tana ɗan yin baya tunawa da dogon gargaɗin datasha gun Abby
''ina wuni Hajja'' cewar Adawiyah hada ɗan nodding ɗinta wanda mamaki ya kusa ƙume su amma suka fuxge
''yaya jikin naki? hope nothings wrong?'' kanta ta jinjinawa hajjan dan tunda maganar cikin ta fito bataji kunya ko kaɗan ba sae yanxu, ɗan sukuyar da kanta tayi tana wasa da yatsunta
''Ke dalla can shashasha cikin fari ae na dangine, ko kim fara jin kunyana ne? yanxu akwae wani abu da yake miki ciwo ko wani abu da kike so?'' Hajjah ta kuma faɗa ganin yanda tayi, sae ta ɗan sake tana cewa
''banason komae'' janta Hajjah tayi suka xauna ta kamo hannayen nata tana cewa
''idan da akwae koma mene karkiji komae ki faɗamin xan tabbatar namiki''
''hajja nifa banajin wani kwaɗayi kawae komae na samu indae abinci ne xanci, idan kinga na nemi wani abu toh sae idan ya faɗa nakejin ina so''
''wani abu kamar yaya?'' humee ta faɗa sanda take miƙawa hajja ruwan data kawo mata
''amm....kinga kaman yana sakani a gaba ya fara lissafo min abubuwa kaman su agwaluma haka nectarine su lyce haka toh tanan nake gane idan ina kwaɗayin wani daga ciki'' humee data saki baki saboda mamaki ne ta maye gurbin mamakin da ihu tana cewa
''wayoooo husband materials, nima wlh aure nakeso anty'' idanu adawiyah ta xaro tana kama bakinta ganin yanda humairah keyi
''ke dallacan arr, ancemiki duk samari haka suke ne? ko ubanki baya haka ae, itadae da Allah ya bawa sae tayita godiya''
''amma meyasa aka aurawa anty shi bayan gamu da muke neman irinsa?''
😩😩😲
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Typing.....✍
Wani irin kallo tayiwa humairah hakanan taji wani irin ba daɗi a ranta, sae ta sadda kae tana ɗan dukan laps ɗinta da yatsu, hajja kuwa duka ta kae ma humeen a baya tana cewa
''baban naki ne xai wani aura miki Ibrahim yaron da ba ruwansa ko magana bayayi sosae shine xa'a aurawa maerrawan kan shiya irinki?''
''wae hajja yaushe kuka ɗinke da anty ne?''
''dama ae ba faɗa mukeba nida namesake ɗina'' kallon yanda taƙi sakewa humee tayi sae ta daki kafaɗarta tana cewa
''chill up sis am jocking fa''
Sosae taji daɗin xuwansu, tana kwance kan ƙafar hajja bayan isha'i KONTO ya dawo lokacin humee na kitchen tana wanke-wanken kwanikan da sukayi dinner, ƙoƙarintashi xaune take yayi blinking mata eyes yana gaeshe da hajja tana masa barka kiran Abby ya shigo sae ta miƙe tayi ɗaki tana amsawa, kallonsa ya maedo kanta ganin yanda ta ƙuresa da ido sae ya ɗaga mata eyebrow yanaccewa
''Auntie lafiya dae?'' bakinta ta taɓe tana kamo fuskarsa a shagwaɓe tace
''shine kaje ka gaji koh'' shima bakin ya kwaɓe kaman xaiyi kuka yace
''kuma yunwa nakeji ba''
''ae shiyasa nacema kabar xuwa kana daɗewa''
''bansan xan daɗeba fa Allah, kuma ma ae baki kirani ba all this while'' ɗan maraeraece fuska tayi tana ɗora kanta jikin shoulder ɗinsa ta xagaye bayansa da hannunta tana harhaɗe maganarta tace
''kayi haƙuri kaji, kayi haƙuri'' humee dake fitowa gudu-gudu daga kitchen da sauri tayi bumping da kukera tana juyawa baya ta saka dukkan hannayenta ta rufe idonta ruff
''wallahi banga komae ba'' ta faɗa tana shigewa kitchen
Washe gari ma kafin ta tashi sun gama komae, tuwo hajjah tayi musu na alkama da miyan taushe da yasha uban jan nama, bae faɗa mata abunda aka dafa ɗin ba tunda suna under probability ne yana gama shiryata ya kamota suka fito hannunta cikin nasa yana ɗan mata magana ƙasa-ƙasa, suna xuwa gun corridor ya saketa tunda su Hajja na nan
''ina kwananku''
''ina kwana'' suka faɗa a tare suna murmushi, ita kuwa sae da ta xauna sannan ta gaeda Hajja
''lafiya lau takwara kin tashi lfy koh'' kanta ta jinjina tana kae hannunta kan warmern dake gabanta xata buɗe tana cewa
''menene muka samu ne?'' ɗan xubawa miyan data buɗe ido tayi dan kulan miyan ne
''wannan miyan fa?'' ta faɗa a yatsine
''ta tuwo ce'' hajja ta bata amsa tana buɗe tuwon
''tuwo kuma hajjah? da safannan?''
''eh da safen kuwa'' ta faɗa tana saka mata a flat ta xuba mata miyan a wani ƙaramin bowl ta tura mata gabanta

''oya start eating'' ta faɗa tana xubawa KONTO ita dama humee har ta fara kaewa cikinta tuni, wasa take tayi da miyan ta kasa ko gutsiran tuwon KONTO ma kasa ci yayi ganin yanda itama taƙi ci, ido suka haɗa sae ya mata alama da ido kanta ta jinjina tana ɗiba ta kae bakinta wani irin waro idanu tayi tana cewa
''auuuuuum, awwww, yayi daɗi hajja'' hararanta hajja tayi amma batayi magana ba
Da rana ma sauran wanda aka rage kawae taci da hajja taga tuwon ya kwanta mata washe gari sae tayi mae yawa daya tsane wurin 12 haka sae ta yanyankashi ta xuba a roba ta xubawa roban ruwa taje ta sakashi a deep freezer so sae ya xamana shine abincinta safe dare a times har rana ma
A haka su hajja sukayi sati anan, a ranar da xasu tafi da yake shima xae bisu saboda shirun da AUNTY ta masa duk ya ɗaga masa hankali tsakanin dan ko A baeji ba daga bakinta akan maganar cikin kuma duk nacinsa bata yarda suyi magana a waya dan haka ya tsara musu tafiya tare, wurin 1pm xasu wuce sun xaune a dinning lokacin daga shi sae ita suna ɗan taɓa hira
''yau su hajja xasu koma fa'' ya faɗa hannunsa na cikin nata kamar wata ibada, ta maraeraece fuska tana cewa
''kaee dan Allah tun yau?''
''ehh wlh kema kinsan halin uncle Musa koda Abby xae juri nisan hajja banda shi'' bakinta ta ɗan taɓe xatayi magana wayan KONTO ɗin ta far ringing, daga kan table da take a ajiye ya ɗaga yana saka speaker
''barka da safiya man'' ya faɗa a sake, dagacan shima Mahmud ɗin a sake ya amsa ya ɗora da faɗin
''uban ɗa ko ya'' hajja
''yah uncle ɗin ɗa'' dariya duk sukayi Mahmud ɗin na cewa
''ina mae kaya tana lfy dae koh?'' baki KONTO ya riƙe yana kallon yanda ta ßata fuska yace
''kaga ni ba ruwana tana jinka wlh''
''aaa'aa wannan dae haɗinka ne kawae Malam''
''haɗina a ina? mata tanajin sunan da ka kirata da shi''
''uncle muna murna'' cewar Hafsah (matar Mahmud)
''yah mum Alim muna godiya'' magana kaɗan suka ƙara akayi sallama ganin 12 ta ɗan nisa
''bubbah, bara na shirya'' shiru tayi tanata kallonsa, ganin haka sae yayi murmushi yana jan checks ɗinta yace
''au ashefa ban miki tayi ba koh? xo muje kishiryani'' aekuwa dukata sakar masa a hannun tana hararansa
Saeda ta rakosu har get tana tsaye cars ɗin sukayi drove up, ji take kaman kar su tafi cox this is the very first time data xauna da family ɗinta bata taɓa sanin abun haka yake ba no wonder mijinta da yayyenta ke tausayinta sosae, ashe ita abar tausayi ce bata saniba? ashe bata more ƙuruciyarta ba? lallae rayuwa tayi wasan kura da ita kam, but she hopes everything has come to an end

''em Madam did u need anything?'' wani boy ya tambaya ganin tun ɗaxu da suka wuce take a jingine taƙi komawa ciki
''ehh lfy'' daga haka ta juya cikin, gidan wani shiru dashi, tv ta kunna tana ɗan dudduba channel
Tana xaune tana kallon almost an hour, jin kallon baya mata daɗi sae kawae ta shiga ciki ta sako himar saman kayanta ta fito wayarta riƙe a hannunta ta shiga ɗakinsa already tana inda yake ajiye keys duddubawa tayi ta ɗauki key ɗin wata CorollaS red ta fito, guards ɗin duk sunanan dan shi kaɗansa ya tafi dama, suna ganinta duk suka tashi
''xan fita xanje gidan sister na, so ba sae kun biyoni ba''
''no ma, we can't let u go by yourself we have to be with u'' batace komae ba ta buɗe motan ta shige da sauri mutum 3 suka shiga wata motan sukabi bayanta dan har an buɗe mata ta fice
Da yake sunada ɗan taxara da gidan Aliyah so sun bi ta highway taga ana saeda rosted corn a gefe ɗan lumshe ido tayi tana tsaeda motar suma tsaeda tasu sukayi ta fito daedae yaro ɗaya ya iso shima, batace ƙala ba ta nuna masa masaran da saurinsa ya buɗe mata motan saboda ana ɗan rana ta koma shikuma yaje sae gashi da ita har guda biyar, ganinta a back seat sae shi ya shige gaban bayan ya miƙa mata, aekuwa kafin su isa gidan Aliyah tacinye ta farko
Aliyahm kaɗae ta iske dan yaran basunan Khadeer na gun nanny Aysha kuma na makaranta itama bata jima da dawowa daga aiki ba, gaesawa sukayi tana kallon hannunta dake ɗauke da corn biyu ga teeth ɗinta duk ta ɓata har ma da gefen bakinta alamar bata saba ci ba
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 24
Typing.....✍
''xauna mana anty atuu'' Aliyah ta faɗa trying so hard not to laugh
''ina yaran ne naji gidan shiru?'' ta faɗa tana cin abunta, ganin haka sae Aliyahn ta miƙe taje fridge ta ɗauko mata ruwa ta kawo xata buɗe mata tace
''indae ma ni xaki buɗe wannan can ɗin banashan farin ruwa bani mineral'' gira Aliyahn ta ɗage cikin ɗan mamaki tace
''yaushe kika fara shan minerals banda labari?'' ajiye masaran tayi irin abun nema ya samu ɗinnan tace
''toh ae in faɗa miki yanxu idan kinaso kiga amae na toh insha ruwa, indae

nasha ruwa toh ba xaman lfy dan sae ya haƌo hada abubuwan da nace ya maeda''
''kae dan Allah'' Aliyah ta faƌa hada su kama haɓa irin mamaki ƌinnan
''wlh kuwa kinsan yanayin dama jinjirin ciki ance haka yake sae ayita faman laulayi idan Allah ya ƌora miki, amma ni dae ina fatan wani cikin baxx.....'' sae da ta kae nan sannan ma ta lura da yanda Aliyah ta xuba mata ido cike da mamakinta sae ta tuna abunda take cewa da kuma wacce ke gabanta, da sauri ta ƌauki corn ƌinta tana ci gaba da ci, itama Aliyahn sae ta miƙe tana shigewa ciki,
A ƙa'ida part ƌinsu ya kamata ya wuce da aka ajiye hajja amma sae yace a kaesa part ƌin mamy tukun, da sallama ya shiga sae ya tarar falon da baƙi da kaman ya koma tunda basu gansa ba amma da yake mutum ne mae hankali yasan dole xataji ba daƌi ace baexo ya gaesheta ba a matsayinta na maman matarsa, ƙarin kuma ga ƙawayenta yasan xataji daƌi when he shows some respect
''Assalamu Alaekum'' ya faƌa da muryarsa mae daƌi, dukansu idanu suka xuba masa tunda duk sun sansa, gaeshesu yayi a mutunce suma suka amsa a hakan, sae ya juya kam mamy daketa danna waya yace
''barka da gida mamy mun sameku lfy''
''a' a ni da Hajiyata kacemin kamar yanda ka saba daya fi min, kuma gida lfy lau'' ta faƌa tana wani juya kae, ƌan murmushi shima yayi yana miƙewa yace
''toh mamy bara naje kar AUNTY taga ban shigaba har yanxu tunda tasan tare naxo dasu hajj....''
''su toh, to ya ita matar taka?'' mamy da taji yace baeje gun AUNTY ba ae batasan sanda ta fara ƙoƙarin jansa da firaba dan kar ya wuce akan lokaci, amma da yake shima ya iya sae ya murmusa yace
''tananan lfy mamy tana kuma gaesheki'' ya ƙarashe yana yin gaba, da sauri tace
''toh yarinyar taka fa tananan lfy koh?'' juyowa yayi cikin wani sanyayyen murmushi yace
''mamynah, anjima xanxo musha hira inaga anan ma xanci abinci'' daga haka yayi gaba abunsa
''wae hajiya Amina na kasa gane kanki, yanxunnan yaronnan kika gama haƌe masa fuska sae kuma naga n sake har kina tambayarsa''
''me kikeso ki fahimta yan mata?'' mamy ta faƌa tana kallon hajiya maimuna
''yaushe kuka ƌinke keda sirikin naki mukeso mu sani'' cewar wata Hajiya
''huum bawani abu bane kawae dae kun sanni inada son cusawa maƙiyi haushi shiyasa kukaga na ƌan sauko ina tambayarsa niyyata in riƙesa kar ya tafi amma yaronnan da yake shegen wayone dashi kamar tsohon dila kunga ae ya tafin'' dariya duk suka sa suna sakin arerewa wata daga ciki tace
''toh da kike tambayarsa cikin yarki yanxu kin sauko koh?''
''kash! ku ae shiyasa baku iya cin moriyar rayuwar duniya ba, in banda abunki ae wannan duk shirine ae, ke ni kaena ban gano gata Alhaji yakeso yamin ba sae da yata da kuma aminiyata suka sakani a gaba suka nunamin

wlh sannan na fahimta''
''toh fahimtar damu muma'' suka faɗa suna gyara xama, itama gyarawan tayi tana cewa
''toh kun dae ga kaman yanda kuka sani ne kullum burina haihuwar mace, amma Allah bae bani su da yawa ba, a burina in haifi yayana duka as mata in samu wani xaxxafan mae kuɗi wanda yakecin gashin kansa in aura masa, shine babban dalilin da yasa na auri ɗan kano saboda chan ne asalin arxiƙi yake as u can see Abuja kaxo naxo ne,.toh unfortunately mutuwa ta raba amma still ina ɗauke da burina a wuyana har akaxo Aliyah ta isa aure, kunga a lokacin ɗan minister of finance ne ya nemeta kuma bae dogara da dukiyar ubansa ba nasa yake nema, dama kuma shine irin gidan da nake mata buri amma kashh....ashe mama's boy ne, nikuwa a duniya babu mistake ɗin da nake ganin xanyi na cutar da yarana kaman aura musu wanda uwarsa ce ke tsara xaman gidansa, banaso ko kaɗan uwar miji ta xama gaba a lamuran yayana a barsu suyi rayuwa da maxajensu cikin aminci, shiyasa naƙi auren daga baya sae shi wannan ɗan former governor ɗin yaxo nemanta a lokacin shima naso na hana saboda na raena income ɗin yaron saboda an sagantasa bae iya neman kuɗi ba, duka imaninsa naga abunda ubansa ya tara shima naso na hana amma da yake Allah yayi sae suka sama masa babbar offer ya fara babban aiki'' ɗan kallon kawayen nata mamy tayi ganin yanda suka maeda ita tv hakan yasata ci gaba
''sae akaxo kan babytah wacce samari suka mata chaa kamar xasu ɗauketa ba aure, amma bata kulasu bata kuma taɓa yarda su haɗu, ina cikin binciken wanda ya kamata na bawa dama a cikinsu saboda am so confuse dan dukkansu cin gashin kansu suke, da kansu ne suke neman kuɗaɗensu ba ƙarƙashin iyayensu suke ba, kwatsam sae ga wannan yaron akayi ta shan fama daga ƙarshe dae akaci galaba a kaena, sae me? ciki yaxo ya ɓullu hankalina yayi mutuƙar tashi sae da aka xaunar dani aka nunamin wannan cikin shine mabuɗin duk wani buri nawa, shine hanyar da xan yiwa Rabi xarce na har abada kuma shine hanyar da xan nunawa Habu nice nan mae yar kuma in nuna masa naxo daedae dashi''
Kae mamy wannan dogon buri haka??
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Typing.....✍
Meenal na xaune hannunta riƙe da wani samplena material da aka fitar daga

manufacturing company da take managing wani ƙaramin na'ura ne kaman microscope tana dubawa jikinnan fesa anata ƙamshi, ɗan tsayawa yayi daga ƙofar yana kallonta duk ta faɗa itama da gani shes'nt alright ajiyan xuciya yayi yana yin sallama da ƙarfi yanda xataji, aekuwa tajin harda ɗan xaburanta dan bataji motsinsa ba
''hajiya minee mene akeyi?'' wani irin kallonsa ta rinƙa yi kaman lokacin ta fara ganinsa cikin ɗan rawan murya tace
''ya khaleel welcome''
''thank u dear, ina AUNTYN?'' ya faɗa yana adjusting A.C
''AUNTY taje Kaduna gun taro'' ɗan kallon meenal ɗin yake da mamaki dan he can't remember AUNTY'S visiting to kd
''taro na me?'' bakinta ta taɓe tana buga hannyenta alaman 'oho' idanunta duka a kansa, jin yayi shiru yana sosa tafin hannunsa yasata cemasa
''a kawo maka abinci ne?''
''no na ƙoshi'' wani shirun suka kuma yi sae chan tace
''yaa khaleel ya matarka ashe an samu ƙaruwa?''
''ehh an samu ƙaruwa alhmdlh, kekuma mene yake damunki?''
''me ka gani?''
''gani nayi kin ɗan faɗa''
''a'a ni lfy lau nake'' tayi saurin faɗa tana tattare kayanta ta wuce sama
5pm dot ya bar Abuja, da yake yayi waya da boys ɗinsa yana isa Lagos gidan Aliyah ya sauka, suna xaune a falo ita da yaran adawiyah kuma na ɗaki, gaesawa sukayi a mutunce as usual
''ka shiga ciki yaya, ae tana ciki ta kwanta tana gama Sallah''
''did she eats?''
''ehh na mata tuwo kuma taci sosae''
''ko xaki tasota toh sae mu wuce gida dare na ƙarayi'' miƙewa Aliyah tayi tana murmushi ta shige dan dama tasan baxai taɓa shiga ɗin ba
Idanunta duk bacci haka ya riƙeta har gun car, da kansa ya sakata ya juyo yanawa Aliyah sallama dan khareem bae dawo ba
''toh anty sae da safe koh?'' Aliyahn ta faɗa tana leƙa adawiyah da ta jima da komawa
''toh yaya khaleel sae da safe'' kansa kwae ya jinjina mata yana shigewa suka tafi
Ɗago kanta data kwantar jikin window yayi ya maedasa kan laps ɗinsa yana matsawa yanda xa'a samu space, ya ɗauke ƙafafunta daga ƙasa ya mayar kan seater ya xare mata kan hijab ɗin ya gyara mata hulan yana shashafa gashi dake goshinta kwance a haka suka iso gida, yanxu kam da kansa ya ɗauki kayansa yayi ciki da ita, sae da ya kwantar da ita bayan ya mata yanda xataji daɗi sannan ya fita ya danna bell dake bayan ƙofa daga ciki suka shigo suka kawo mishi luggage's ɗinsa
Washe gari baeje ko ina ba, dan wunin da yayi jiya a Abuja ji yake kaman yayi wata bae ganta ba😳 suna xaune yana fiddo mata da abubuwan da su mamy suka bashi wae ya kawo mata, dariya kawae take tana kallon yanda yaketa

bubbuɗe mata ledojin, shima murmushin yake yana nunnuna mata abubuwan da kowa ta bada
''wae toh ita wannan jakan a ina ka sameta?''
''Hajiyan Alii ce ta bani, kayan yamin yawa''
''Allah sarki Ummah, she's so kind''
''ehh hakane kam, she's different acikin gidannan'' ya ƙarasa faɗa yana saka mata kwakumeti a baki
''yayi daɗi kuwa'' ta faɗa tana buɗe baki ya ƙara bata wani
''kamar sun san xanje kuwa, au ban faɗa miki ba a part ɗinku nayi lunch'' ya faɗa yana bata albishir, sae ta janye kanta cike da mamaki tace
''a part ɗinmu kuma?''
''ehh mamy ce taso na tsaya muyi hira sanda naje shine na mata alƙawarin komawa cin abinci'' kanta kawae ta girgixa dan ta harbo jirgin mamyn, sae kuma tayi ɗan murmushi tace
''ae ta musamman ce, she knows her hand''
''yah na yarda dan abincin kam is extendly woow'' dariya ta saka ganin yanda yayi da fuskarsa
''kaci abincin maya dole ka ruɗe ae''
''huum kin ma san da naci a xuciyana me nace?'' da sauri ta girgixa masa kanta
''toh cewa nayi shiyasa Abby duk abunda xaije ya dawo baya taɓa yarda matarsa ta rabu dashi ashe yasan garan da ake haɗa masa yana jaa'' dariya suka saka sosae tana bashi hannu sukayi high five
A haka rayuwan take ɗan tafiya, yau gashi har su hajja sunyi wata da komawa, wanda kuma har a yanxu bae samu magana da AUNTY ba dan taƙi yarda, sosae abun yake cinsa amma yana ƙoƙarin dannewa baya nunawa kowa he always include his wife first amma hakanan ya kasa faɗa mata, tunda kusan itace sila inda bae aureta ba they can not came to this extend, Mahmud kawae ya faɗa wanda shine ya basa shawaran ya kuma xuwa Abujan though dae ya koma sau biyu a cikin watan but still ana making masa excuses
Duk abunda yake ciki tana sane kuma kallonsa kawae take dan tasha farkawa daga bacci ta iskeshi a xaune gefen bed yayi tagumi wanda ba haka yake ba, baya ƙarar da darensa a bacci wannan ta sani amma kuma sallah yake ba tunani ba, daren ranar da xae tafin ma bae yi bacci ba yanata faman tunani itadae da yake harkan gabanta ta isheta tana gama haɗa masa bag ɗinsa ta kwanta, washe gari kuma koda ta tashi har ya wuce, duk da bataji daɗi ba amma tanata ƙarfafa xuciyarta ko tunaninsa taƙi yarda tayi
Wato har yanxu dae ajinnan na nan kaman yanda yake
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 25
Typing
Hakanan taji tanason cin alala, ɗan taɓe baki tayi tana shafa cikinta
''nikam yaushe ma nae ganin alala har naci bare naji inaso?'' ta tambaya tana kallon cikinta, sae kuma ta taɓe baki tana miƙewa tayi kitchen ɗin, da yake tayi zuhr sae kawae tayi xamanta a kitchen ɗin har ta gama ta xubo ta fito tana hurawa da baki, wayarta daketa vibrate ta kalla 'H' idanunta ta ɗan fiddo da mamaki sae kuma ta ɗaga kiran
''H mae abun mamaki'' ta faɗa tana xama
''anty kin wuni ƙlau'' aka faɗa daga cikin wayar
''lfy''
''masha Allah, kina gida ne? munaso xamu xo kawo miki IV ɗin Naanah ki turamin address''
''dan Allah? abun yaxo kenan''
''ehh wallahi xanyi hanging yanxu dan ina driving ne ki turomin yanxu hope kuma kina gida''
''ehh ina gida sae na ganku'' daga haka ta ajiye wayar
''alalana kar kiyi sanyi dan Allah'' ta faɗa tana kaewa baki daedae kiran KONTO ya shigo ƙin ɗagawa tayisae da ya mata kira na biyu sannan ta ɗaga ta saka speaker ta barta anan kan table tana tura baki gaba
''ya wuninki?'' ya tambaya daga can, saeda ta kusa 10 second sannan ta amsa, dagacan murmushi yayi yana gyara kwanciyarsa dan dama yasan a rina
''yaya madam da babyn madam suke?''
''sae ka tambayesu ae''
''toh ae su ɗin ne nake tambaya koh?''
''kanka dae akeji ni ba ruwana''
''toh shikenan dae have u eaten?'' ɗan kallon alalan gabanta tayi tana smile tace
''guess what am having''
''oww wae yanxu ma kike lunch?''
''ehh mana''
''sae yanxu sukaje suka kawo abincin kenan?''
''a'a haba kawowa dae, ni na dafa fa''
''ke kika dafa? toh bakiyi baccin ba yau kenan?''
''nayi amma ana zuhr na tashi nayi alala'' kansa ya jinjinayana taɓe baki yace
''so u know how to do such things koh?''
''yaaah i know much''
''gud for u, ni kinga ko abincin ba'a bani b...''

''toh wani ya aikeka ne? Allah ma ya ƙara'' tayi saurin faɗa dan taji ɗaɗin ƙin basan da akayi, dagacan shima wani irin tashi xaune yayi yana riƙe bakinsa dan mmakinta na xallan yarintan da har yanxu yake ɗawaeniya da ita yace
''wato kina farin ciki bcox am starving koh?''
''aa nifa kar ka fara kace xakaga laefina ae saeda na faɗama kar kaje Abuja amma kaƙi jina'' dariyan dake taso masa ya danne yana maraeraecewa yace
''yanxu dn Allah yaushe kika ce min kada naxo Abuja?''
''duk lokutan da kake cewa xakaxo ae hanaka nake nace kayi xamanka sae kace 'inyi xamana as how? idan banje Abujannan ba babu xaman lfy fa' nikuma sae na ƙyaleka da halinka'' sosae yake dariya jin wae muryansa ne ta kwaekwaya, itama dariyan tayi
Wunin ranar a sake tayisa saboda xuwan 'H' da wasu ƙawayensu biyu, sunsha hira kaman ba gobe dan wuni suka mata sae wurin magrib suka wuce da yake da car sukaxo iya compound ta tsaya suna ƙara yin sallama aka buɗe get duk idanu suka maeda kan motar dake shigowa har yaxo yayi parking nata ya fito, wani irin ihu ta saki tana rugawa a guje shima cike da ɗoki da kuma sanin abunda ke jikinta sae ya sauƙaƙa mata gudun ta hanyar rugawa a guje ya chaɓeta sama yana cewa
''oyoyo bubba naah''
''oyoyoooo'' ta faɗa dan batama kiransa da ko wanne irin suna
''baka....faɗamin....kana.....hanya..b.a'' ta faɗa tanata faman nishi, hannunta dake cikin nasa ya ƙara riƙewa yana juyata tayi facing friends ɗinta dake kallonsu, ganin sun juyo sae suka fara kame-kame
''baƙinki'' ya faɗa yana janta gabansu, duk gaeahesa sukayi ya amsa yana sakinta yace
''bara na sake muku ƙawarku kuyi magana, ki sameni a ciki idan kun gama'' daga haka ya matsa gun boys ɗinsa suna gaesawa
''kinga dama tafiya xamuyi kuma tunda ga mijinki bisa ma ƙarasa hiran ta waya kokuwa''
''roh shikenan na gode muku har ba iyaka sae munyi magana'' tana tsaye har suka fice tanata ɗaga masu hannu taji ya rungumota ta baya yana saka kansa cikin wuyanta
''my loveee'' in wisfer ya faɗa yana sakata jikinsa sosae, itama narkeqa tayi a jikin nasa dan tunda ya mata haka tagane ba kowa a compound ɗin dan shi mutum ne mae kame kansa inda mutane
''muje ciki ka huta'' ta faɗa bayan ta juyo tayi huging ɗinsa
''yauwa toh muje'' ya faɗa yana ɗaukarta
Suna xaune bayan isha a dinning shi yanacin basmati Green Jallof itakuma tanacin farar doya da mae, duk sunyi shiru shi ya fara gamawa wanda dama kullum a haka suke wani lokacin ma kafin taci rabi ya cinye plate ɗaya, miƙewa yayi yana ɗaga hannayensa dan jikin ya saki ya kalleta sanda yake sauka yace
''bara na ƙara watsa ruwa before in fito make sure u done'' kanta kawae ta jinjina masa dan bakinta a cike yake

Tana gamawa ta bar kayan anan dan shine yake gyarawa ya hanata, ɗaki ta wuce yana xaune yana shafa bayansa take kallo duk da yanada duhun fata amma kallo ɗaya xa'ayi masa asan lallae fatar tana jin daɗi, ta cikin mirror yake kallonta suna haɗa ido ya sakar mata murmushi yana cigaba da shafa mansa, a hankali ta taka har gabansa sannan ta xagaya hannayenta suka koma bayansa tana xama akan ƙafafunsa
''ya akayi aka haifoka black bayan babanka bama ɗan asalin nan bane?''
''ya akayi aka haefoki fair bayan iyayenki yan asalin nan ne?'' lips ɗinta ta tura kusa da hancinta tana cewa
''saboda mamyna itaɗin fara ce''
''gud toh nima saboda mamana black in complexion ne so i take after her'' ya faɗa yana kallon idanunta, bakinta ta ɗan taɓe tana shafa beards ɗinsa tace
''ae gwarama da kae ne ka ɗauko duhun fatar tata da ace kuma wannan yayar taka da take macene ta ɗauko fa?'' dariya maganar tata ta basa sae ya kama bakinsa yana cewa
''waye yace miki yayata ce? ƙanwata ce fa'' idanunta ta ɗan xaro sae kuma ta mayar da su tana cewa
''Chabb yanxu wannan babbar da nake gani ƙanwarkace?, koda yakema ae ba abun mamaki bane tunda kae tsohone dukafa gidanmu ka girmemu su mamy ne kawae suka girmeka''
''toh amma kuma yanxu ae mu sa'anni ne koh?''
''sa'anni da wa?''
''da ke mana'' wani kallo ta masa tana cewa
''chabb wlh a'a kaeda har yaa Usman ka girma inaga ni da nake ƙanwarsa ta ƙarshe chabb''
''waye yace miki na girmi Manu, manu ae babbane bama sa'ana bane''
''chabb toh maedani wata yarinya dan kawae bakaso nacema tsoho shine xaka wani ce wae yaa Usman ya girmeka'' dariya sosae yake yana ƙara riƙeta ya haɗe forehead ɗinsu still da yar sauran fara'arsa a fuska yace
''yanxu ae ban girmeki ba tunda kin riga kinsan girman kinga mun dawo shekaru ɗaya kenan''
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Typing.....✍
A haka sati ya kuma xagayowa still shiryawa yayi ya tafi Abuja sanda ya faɗa mata a dawo lfy kawae ta masa lokacin itama tana shirin xuwa gidansu

Naana dan har anyi wuni jiya, ta rigasa tafiya dan wurin 11am ta wuce shikuma sae rana tayi
Sosae sukayi mamakin ganinta dan ita kwata-kwata biki ba stuff ɗinta bane, sakin jikinta tayi tanata cuɗayya da mutane duk sae ta manta da ɓacin ranta ta sake sosae, wuni ne xa'ayi sae lady's party da yamma, makeovers na gama yiwa friends ɗin amarya akace itama su mata da farko ƙin yarda tayi sae da aka ɗan lallaɓata sannan ta yarda akayi amma very light kuma tayi kyau to the core
Tana xaune wurin event ɗin ta bayan pool ɗinsu akayi decoration ɗin dan gidan is huge kaman nasu, wayarta na hannunta tanata dannawa dan duk abunda ake ko alaman tasi batayi ba batama kallon abunda akeyin harkanta kawae take, taji sanda aka xauna kujeran kusa da nata amma bata ɗaga kae ba sanin ba ita kaɗae bane agun
''yammata barkanki koh'' banxa tayi dashi, ganin ya kuma magana bata ko ɗaga kanta ba sae ya saka kyakyawan hannunsa ya kama edge ɗin wayar yana xura yatsunsa ya rufe fin rabin screen ɗin dasu, ɗan tsayawa tayi for some seconds sae kuma ta ɗago in her danger existence, to her big surprise sae taga KONTO yana mata wani cute smile
''hii madam'' ya faɗa yana mata wink, hannunta ta miƙa ta daki shoulder ɗinsa tana tura baki tace
''Allah ka fusata ni fa''
''hahahaa toh meye xae fusataki keda kikayi new catch'' ya faɗa da ƙarfi yanda xata jiyosa
''wallahi da gaske naji haushi nifa na tsani namiji yamin magana barin ma idan a gun biki ne''
''yanxu kuma ae gashi kinyi sabo kuma baki isa kice bakya sona ba dan baxan yardaba Allah''
''toh aekuwa ni bakamin ba, i mean ba-na-yii'' dariya suka kwashe da ita yana ɗan jan checks ɗinta
Sosae ta gaji duk da ba rawa tayiba amma kafafunta wani irin ciwo takeji suna mata da suka iso gidama hannayenta ta ɗaga masa yanda yara suke idan sunaso a ɗaukesu, hulansa ya miƙa hannu ya karɓa daga gun yaronsa dake bayansa ya sallamesu yana saka hulan cikin pocket ɗin wandonsa ya tattare hannun rigansa ya ɗaukota kaman wata new born yayi ciki da ita
Bayan sun gama shirin bacci tana xaune a tsakiyar gadon yana samata socks hannunta riƙe da cup cike da lemon juice dan tunda ya kaeta follow up doctor yayi instructing nasu akn ta rinƙa sha duk dare, the cup cover half of her face sae idanuwanta data xuba masa tana kallon duk abunda yake, shi irin maxajennan da hidimar iyalansu is their best chores ne kusan hakan kaman haƙƙinsa ne yake gani, idan earrings xata saka toh xai taemaka mata idan takalmi ne xata saka sae ya kawo mata shi har gabanta 'why did i married him late?' ta tambayi kanta duk a cikin tunaninta
''Naira for ur though'' ya faɗa trembling his fingers in her sight
''nothing, kawae ina kallonka ne''

''kina tunanin dalilin da ya hana ki aureni tun tuni koh?'' idanuwanta ta fiddo tana kama baki, girarsa ɗaya ya ɗaga mata yana cewa
''kinsan am mind reader, so i can observe everything sharf²''
''kaga malam banason cika baki ae observation daban mind read daban, besides ae kowa ma is mind reader''
''except u''
''bara na faɗama wani abu, kaga wannan friend ɗin tawa da muke bikinta yanxu?''
''she's so close to u amma''
''me ka gani?'' ta tambaya tana kwantawa kan laps ɗinsa dan ta gaji da xaman
''ehh toh naga kinata ɗokin bikin kuma naga kinje da wuri sosae, as for my information you're not fond of biki''
''ehh toh kasan mum ɗinsu ƙawar mamy ne sannan late yayarsu da khall xae aura koh sae ta rasu''
''oh, oh wae da ƙanwar farha ce?''
''ehh gidansu ɗaya ashe kasan farha?''
''yess yana yawan bani labarinta duk sanda naje gunsa a Cambridge har gaesawa ya taɓa kaeni munyi''
''so u recently go to Cambridge?'' ɗan taɓe bakinsa yayi ya ce
''no not really, u see i attend Cambridge driving academy so his college is close by that's why we meet alot''
''umm, so u attend the best driving school? u will be a best driver i guess''
''faɗi ki ƙara'' he said with proud motion
''kasan Cambridge sosae''
''University of Cambridge ma nayi ae''
''wooow u attended the most expensive health school''
''yap''
''kagan tanada kirki sosae koh?''
''tanada kirki though batada sakin jiki nima kuma kinga haka naie so lokacin da muka gaesa kaman xata shige cikin ƙasa tanata nuƙu-nuƙu shikuma he was irin ae ba komae ni yayansa ne ta saki jiki but she fail''
''ƙum... haka take bata sakin jiki, kasan tare mukayi sec dasu toh ita naana tun xuwanmu muke friendship da ita saboda halinmu dake resemblance muna j.s.s 1 suna 3 a lokacin aka taɓa ɗaukomu a park tare, ni xan tsaya a kano suma kuma xasu tsaya toh shinefa mukaga munxo har unguwar da xamu sauka a tare su suka tsaya a gidan wata mata kusa da gidan ummanmu (A'isha yayar mamy) hajiya ta Benin, shikenan bayan sun huta sukaxo nan gidan ummanmu tare da kakar tasu daganan dae har aka gano ashe an jima da sanin juna shnefa har soyayya ta shiga tsakaninsu da khall''
''tanada hankali da kamun kae baxaki taɓa cewa a waje take karatu ba saboda she's too cool, lokacin data fara rashin lafiya yake tambayana wae what will cause left side pain so abubuwan da yake sunada yawa kinga
1) constipation

2) kidney stones
3) pancreatitis
4)splenic flexure syndrome, excetra-excetra. So a lokacin naso ya kawota ayi undergoing text unfortunately sae akaxo aka ɗauketa daga gida ashe ba rabon xata dawo school ɗin ma'' ɗan lumshe idanunsa yayi listening to his wife's sobbing
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 27
Typing.....✍
''sae kawae kaji labarin ta cika koh?'' bakinsa ya haɗe yana jinjina kansa
''naso na kuma ganinta saboda yarinyan was morethan kind tana girmamani kaman wani uba or something like that, ko a sanda ya kirani yana faɗamin ta rasu i though i heard him wrong, saeda na kuma kiran na'im ya tabbatar min, am so soo shock though we have to test death eather we like it or not amma naji mutuwarnan to be honest but muna fatan Allah sa mutuwa hutune a gunta'' ya ƙarasa yana hugging nata jin kukanta is non stop
Tun daga wannan dawowar bae kuma cewa xaeje Abuja ba, har ta fara xuwa check up kuma duk sati da kansa yake kaeta amata duk abunda xa'a mata ya dawo da ita, a cikin tsakanin yayi tafiya foreign countries four time amma baya wuce 6 days saboda check up ɗint
Yayi tafiya xuwa zaria taron nadin wani friend ɗinsa ɗan wajen iyan Zazzau daga gun nadin ya wuce Abuja dan a tsakaninnan har faɗhima da yake ɗan jin sauƙi a gunta ta ɗauke masa kae wanda abun ya basa mamaki dan haka yau ya ɗau alwashin xuwa tunda kusane, without informing everyone ya ɗau hanya
Sanda ya iso is past 2 kae tsaye part ɗinsu ya wuce, yana shiga parlourn AUNTY na tahowa cikin haste da alama wani abun ne ya taso unexpectedly, tana ganinsa ta haɗe fuska tana harɗe hannayenta a ƙirji ta xuba masa ido, a hankali yake kallonta idanunsa na lowering tare da legs ɗinsa sae gasa a duƙe his kneels on the floor
''AUNTY dan girman Allah, da.....''
''kaga Ibrahim matsa ka bani wuri ko ka haɗu da mummunan ɓacin ran da baka taɓa tsammani ba, sannan kuma cikin da yake jikin matarka koda sama da ƙasa xasu haɗe baxan taɓa karɓansa ba kaje daga kae har cikin na sallamawa matarka da uwarta, shashashan banxa da bakasan me kake ba,

sannan raenonka da nayi wahalan yi kaje kaeda mahaliccin mu, bani hanya ni!!'' ta faɗa a fusace kuma a cikin ɗaga murya, miƙewa yayi ya bata hanya dan kusan xaece tunda yake bae taɓa ganin fushinta ƙarara irin haka ba
Bae kuma minti ɗaya a gidan ba yasa drivernsa ya kama hanyar Abuja, yana ɗan kwance a bayan motar kaman wani maraya ya haɗe hannunsa ya saka fuskarta a tsakiyarsu yana ajiyar xuciya sama sama
Tana xaune tana game a laptop ɗinsa hannunta da avocado smoothie tana sha tana matse fuska dan kwata kwata ba daɗi takeji, sunyi waya ɗaxu sanda suka taho bae faɗa mata yaje Abuja ba yadae ce mata ya taho kawae, da yake a flight yaje so bataji fitar mota ba amma taji shigowarta, bata maeda hankali ba dan batayi tunanin shi bane tunda ba da car yaje ba
''Assalamu Alaekii'' ya faɗa cikin sassanyan muryansa mae cike da nutsuwa yana jingina jikinsa da ƙofan ya harɗe hannayensa yana kallonta yanda take kallonsa da mamaki ta kuma kasa magana, hannunsa ya warware yana buɗe mata su aekuwa kaman jiran yayi hakan take da sauri tayo gunsa as usual shima takawar yayi dan rage mata hanya
''ina ka tsaya wae?'' ta faɗa cuddling his face
''no where of cause'' ya faɗa yana kama hannunta suka xauna, ɗan shashshafa jikinsa ta ɗanyi jin kaman xafi, da yake ya tattare rigar shaddar jikinsa da xai xauna hannunta ta saka ta ɗaga rigar tasa ta tattareta ta saka hannunta ta cikin singlet ɗin ta taɓa skin ɗinsa da sauri ta kallesa tace
''wayyo bakada lfy ne?''
''na gaji sosae ne''
''toh sannu muje kayi wanka sae kaci abinci, u look starved'' baece komae ba ya miƙe sukayi ciki
Saeda ta gama shiryasa ya fito fess sannan suka sauko dayake ta rage sauran abinci da kanta ta basa tanayi tana basa labari har suka gama lokacin anata kiraye-kirayen magrib dan haka masjid kawae ya wuce, itama sallahn ta tashi tayi da yake tasan sae bayan isha xae dawo da sauri-sauri taje ta haɗa bread da egg ta soya taci a kitchen ɗin tasha madara can ɗaya sannan ta koma tayi sallah
Duk yanda yayi da ita taci abinci ƙin ci tayi suna xaune yana matsa mata ƙafar da take kamar da dan koh sauyawa batayi ba tunda cikin ba wae girma yayiba just 9mnth, jin yanda taketa faman chat ko kallonsa batayiba yasasa cemata
''wae love baxakici abinci ba?'' ɗan sauke wayarta tayi dan da ta ɗagata saetin fuskarta, a wani irin shagwaɓe tace
''nafa faɗama ganinka da mukayi yasa cikinmu ya haɗe tsaff bamajin komae'' kallonta ya tsaya yi for some seconds saekuma ya ja ƙafafunta dake hannunsa yana tashi daga kujeran sae gata a kwance flat
''wayyo Allah na'' ta faɗa tana fiddo idanu waje jin yayi kwance a jikinta
''ae baki bani babyn muka gaesa ba amma kina wani cewa kun ƙoshi da ganina''
''kuma shine xaka ɗorawa babyn nauyinka?''

''babyn ma ae nauyina ne ya samarmana'' kansa ta daka da sauri tana cewa
''nauyinka koh wahala na?''
''wahalanki a ina me kikayi?'' wani irin hararansa tayi ganin yana ɓoye dariya tace
''duk wahalan da nasha xakace haka, nasha wahala na ƙarar da ƙarfina ae ni ya kamata ma abawa reward''
''aaaa, ina ƙarfin a nunamin na gani, ina yake'' ya faɗa yana mata cakulkulo, duk da baya saka masu ciki dariya amma batasan sanda ta hau dariya ba tana turesa
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 28
Typing.....✍
Cikin bacci ta rinƙa jin gumin jikinsa na shiga cikin nata jikin, ya riƙeta gam ga fatarsa tana gogan nata shiyasa xafin ya shigeta sosaea hankali ta samu ta xare jikinta tana tashi xaune tayi ƙoƙarin wartsakewa ta miƙa hannunta ta shafa wuyansa da ya ɗau xafi sosae jikinsa sae shivering yake da alama xaxxaɓi ne ya ɗaukesa, idanunta ta xuba masa cike da tausayi tasam inda mahaediyarsa na raye he won't experience this kinda life
Toilet ta shiga ta jiƙo mini towel biyu ta fito dasu ɗan juyosa tayi tana ɗora kansa kan pillow wet towel ɗin ta ɗora masa a forehead ɗayan kuma ta kama joints ɗinsa tana daddannewa dashi almost 17mnt tana tayi saeda taji jikin ya ragu sosae sannan ta tattare kayan ta kae toilet, rob ta ɗauko ta shafe masa wuyansa da jikinsa ta tofa masa addu'a ta koma ta xauna tana kallonsa, dukan baccin dake idanunta ya tafi kawae kallonsa take
She never fall for anyone in her life but abunda takeji towards him now is LOVE deeper love, she never experienced before amma to be honest she loves her husband expecially now that she spend a lot with him he knows him now, she knows the things she turned her back from before, but now she's out of darkness all because of him
Washe gari cikin ikon Allah garau ya farka, yana xaune yana cin pepper soup datayi insisting sae yaci, bakinsa a gaba kamar wani ƙaramin yaro yake amsa, itama nata fuskan a haɗe yake kaman irin uwa da ɗanta ɗinnan, saeda yaci fin rabi sannan ta ajiye tana xuba masa ido
''yanxu sae me kakeso kuma?''
''wannan ɗinma ae bani nace inaso ba'' ya faɗa yana ɗan kallon gefe
''toh bara na haɗoma wani abun tunda ka bani go ahead'' ta faɗa xata miƙe

yayi saurin riƙeta yana cewa
''nifa na ƙoshi'' hararansa tayi tana dawowa ta xauna
''yanxu bacci xaka xo ka koma''
''bacci kuma?'' kanta ga jinjina tana gyara masa pillow
''ehh bacci koka manta na faɗama no fita yau''
''ammaaa.....''
'shiiiii' ta saka finger ɗinta a lips tana bugun pillow da hannu alamar ya kwanta babu yanda xaiyi dole ya kwanta ɗin yana rufe idonsa, ganin yanda yayin sae ta miƙe tana shafa cikinta dataji kaman shima yunwar yakeji bowl ɗin da ta gama basa kifin ta ɗauka tayi kitchen tana tafiya tanaci har ta shige, wanke wanke tayi ta goge kitchen ɗin lokacin ana zuhr, ɗakin ta koma dan tashinsa yayi sallah to her big surprise yana xaune wayarsa kare a kunnansa da alama kira yake yana ganinta ya kife wayar Yana avoiding idanunta
''Ka tashi kayi alwala sallah ake kira'' ta faɗa tana goge fuskantar da foam a gaban madubi
''inaso nayi har wanka ma'' ya faɗa yana cire botir ɗin rigarsa, matsowa tayi tana hugging nasa da hannu ɗaya ɗayan kuma ta xagaya dashi bayan wuyansa tana shafawa, wani irin da yakeji yasashi tura bakinsa gaba yana manna lips ɗinsa jikin wuyanta yayi hugging nata back sun kusa 3mnt a haka sannan ta sakesa tana ɗan ja baya ta shige toilet ɗin
A hankali ta maeda ƙofan ta rufe tana ƙarasawa jikin bathtube ta xauna tayi shiru tana ƙoƙarin maeda hawayenta, batasan me yasa ƙaddara ta haɗasu da iyaye irinsu mamy ba ɗaxu rungumesan da tayi wani irin kukane taji yana taso mata na tausayinsa taji sauƙi kuma sosae, miƙewa tayi dan kar yaga ta jima a ciki ta haɗa masa ta fito
''na gama'' ta faɗa tana ficewa da sauri a ƙofa ta tsaya saeda taji shigewarsa sannan ta dawo kallon wayarsa daya kife akan bed ɗinta take, sanda ta fito a hannunsa yake yanxu ya ajiyeta data gama haɗa masa ruwan wanka tun ɗaxu yaketa nuƙu nuƙu da ita tana kallonsa ta masa banxa, ɗauka tayi tana duba ciki a call log yake sae yayi minimizing da xae ajiye idanu ta xubawa number AUNTY da yayi seving
'jannah❤' kira 71 ya mata daga jiya da dare xuwa yanxu
Kwana biyu a tsakani ta kasa nutsuwa tanata ƙoƙarin taga ta kula dashi as much as she can, shi ya dawo daedae amma ita ta kasa nutsuwa yau suna tafe a hanya daga hospital shi yake driving ɗin tana daga gefensa jikinsa sanye da shadda butter color ya naɗe hannun rigan xuwa guiwansa hularsa na kan cinyanta itama jikinta sanye da Aura wax milk and coffee A-shape abun cikin daya ɗan fara tasawa sae Free style take sakawa
Wayarsa dake hannunta tun ɗaxu take dannawa a xahiri amma kuma number AUNTY ce taketa ƙoƙarin haddacewa tunda suka hau hanya, yau dagashi sae ita suka fito babu yan rakiyar tasu, suna isowa ta lallaɓa ta shige ɗaki bata tsaya tunanin komae ba ta saka number AUNTYn ta kirata wayar na fara ringing taji abunda bata taɓa ji ba game da AUNTYn wato faɗuwar gaba...

''hello'' AUNTY data ɗaga kiran ta kuma faɗa jin shiru
''sannu da gida'' ta faɗa tana cijewa, ɗan shiru AUNTYn tayi dan jin muryan sounds familiar
''ADAWIYAH ne'' wani duuum AUNTY dake can tayi sae kuma ta ciro wayar ta kashe, itama jin an kashe sae ta cire wayar daga kunne tana re-dialing
''ke yarinya menene kike so?'' AUNTY ta faɗa a hasale sanda ta kuma ɗaukan kiran
''ke ya kamata nayiwa wannan tambayar hajiya babba, menene abunda kikeso bayan duk abubuwan da kika samu na rayuwa? shin kin ma taɓa ɗaukan Ibrahim a matsayin ɗanki? inaso ki faɗamin shin duk tsawon shekarunnan kin raenesa akan soyayya ne ko kin raenesa akan abun duniyar da mahaifansa suka mallaka? shin kin taɓa basa koda 1% space ne a cikin xuciyarki dan ya xauna?''
Da kyau readers anxo wurin fa
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mad nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 29
Typing.....✍
''hajiya Rabi why are u quiet? shin tambayoyina sunyi tsauri ne? shiru dukkansu suka kumayi, jin AUNTYn baxatace komae ba sae ita taci gaba
''bamu mukeda ikon xaɓan ƙaddaran rayuwarmu ba inda mu mukeda ikon xaɓama kanmu iyaye da baxamu taɓa ɗaukanku ba, Abby ubane namiji amma yafiku sanin xafinmu mu yayanku, wae dan Allah baxaku iyabarin abunda yarigaya ya wuce ya ci gaba da wucewa ba?'' cikin kuka ta ƙarasa maganar dan ta kasa daurewa
''wannan laefin waye toh? eyee ki faɗamin laefin waye? na mamanki right? itace ta fara komae, itace ta janyo komae inda batayi abunda tayiba da munanan kaman yanda muke a da, da duk hakan baxata faru ba''
''naji daɗi nakuma gode Allah da kika san cewa ba laefinmu bane bamuda abunda xamu ƙaru dashi a wannan kuma, sannan wae ma sanda kukayi duk wannan abubuwan muna ina? Inace ko shi kansa Mu'azzam ɗin ba'a haefesa ba bare ni''
''amma kuma abun ae mamynki ce tayisa''
''toh meye laefina ni a ciki? shin nayi wani abune a wannan? nasan inda nake a lokacin da akayi abun n....''
''bakiyi baa!!'' AUNTY ta faɗa da ƙarfi wanda saeda adawiyah ta janye wayar

daga kunnanta
''toh dan me kike threatening ɗina bad?''
''saboda uwarki da kakarki dasuka cutar da mu suka lalata komae, mu bamu taɓa jin haushinsu ba bamu taɓa riƙarsu da komae ba xama na tsakani da Allah mukayi dasu amma su me suka mana? sun ci amanarmu sun ruguxa mana farin ciki, sannan basu kyalemu ba har yanxu'' sosae AUNTY ke kuka, itama Adawiyahn kuka take da kyar ta iya cewa
''toh ni meye laefina? why do i have to take the blames? why me?''
''saboda kin kasance mukullin da uwarki take tunanin amfani dashi dan ta ruguxani ko kin ɗauka bansan komae ba? toh mahaifiyarki da bakinta ta faɗamin cewa idan har tana raye sae na xama ƙarƙashin ta sae ta maedani ba komae ba tunda har kika samu cikinsa toh kin gama mallakesa daga sama har ƙasa tacemin bata taɓa farin ciki da aurenki ba amma tana farin ciki da samun wannan cikin saboda nice kakar abunda xa'a haefa''
''shin ita mamyn ce tace miki haka?''
inaji wann maganar da uwarki ya kamata ki xauna kiyita badani ba''
''na sani nasan cewa ke ba uwata bace dan baki taɓa ɗaukana a haka ba, sanna...''
''sannan kema baki taɓa ɗaukana a matsayin uwa b..''
''amma Ibrahim fah?'' tayi saurin taran numfashin AUNTYn
''kinaji wannan tsakanin ɗana dani n.....''
''idan har da gaske a yanda kika faɗa yanxu cewa ɗanki ne toh ki saurareshi koda sau ɗaya ne daganan sae ki yanke hukuncin idan ya dace ki watsar da shi kokuma ki ci gaba da ɗaukarsa kaman yanda kuka saba'' tana gama faɗa ta kashe wayar tana xama akan bed
''ya Allah see us through'' ta faɗa tana shafa cikinta
Washe gari kuwa tun sassafe dan tana bacci ma wurin 8:05am yaxo ya tasheta, ɗan yatsina fuska tayi dan baya tashinta idan tana bacci no matter what shiyasa yanxuma taji abun kaman a mafarki, ganin kaman baccin baxae saketa ba yasashi saka hannayensa ya miƙar da ita tsaye ya kama checks ɗinta yana girgixawa dan ta dawo daedae
''wae menene?'' ta faɗa tana ture hannunsa daga fuskanta
''Abuja xanje yanxu'' waro idanuwan da taƙi buɗewa da kyau tayi tana kallonsa
''Abuja for what?''
''AUNTY ne take nemana tace i should be around before 12 dan Allah ba abun daɗi bane?'' ya faɗa yana ware dukkan hakoransa itama wani busashen yaƙe ne tayi tana jinjina kanta
''ehh kwarae kuwa abun murna ne''
''ehh kuwa shiyasa yanxu xanje nasa a dubamin flight idan bae samu ba xa'a taho daga kano a ɗaukeni dan....'' wayarsa data fara ringing ta katsesa, ɗauka yayi ganin wanda xae masa booking ɗin ne
''yes Zacks'' ɗan shiru yayi for a while sae kuma yace
''ok toh bara na shirya i will contact u when i reach there, yauwa kinaji

wannan wani yarona ne a da so yayi masters shine da naga xamansa wurina baxaeyiba na sama masa aiki a airport so yanxu abunda yake faɗamin an samu empty seat for one person da so nayi muje tare amma yanxu u have to stay''
''ohhh no,no,no,no, karka damu ae kaje ɗin'' ta faɗa tana girgixa masa hannu
''sure''
''hundred percent'' ta faɗa tana tana bugun shoulder ɗinsa
Da kanta ta tayasa ya shirya suka fito har get ta rakosa jikinta sanye da doguwar jalbab purple saboda kayan dake jikinta, hannu ta saka ta xagayesa tayi interlocking hannun ta waist ɗinsa tana tura bakinta gaba ganin yanda yake mata ido saboda yaransa dake wurin, yi tayi kaman bata ganiba tana mannewa da jikinsa
''yanxu xuwa ƙarfe nawa xaka dawo?''
''xuwa 4 ma ina gida'' bakinta ta matsa kusada haɓansa tace
''toh kamin kiss mana'' idanunsa ya lumshe yana saka hannunsa ta armpit ɗinta ya tsunkuli bayanta
''owch wayyo ni'' ta faɗa tana komawa baya da sauri, dariya yayi yana shiga motar dake a buɗe tun ɗaxu
''shikenan sae na dawo?'' ya tambaya yana daga mata gira, hannunta ta ɗaga masa tana shafa inda ya tsunkula da ɗayan hannun
Har suka bar gidan tana tsaye tana ɗaga masa hannu, ajiyar xuciya tayi tana juyawa tayi ciki baccin duk ya gudu daga idanunta sae kawae ta wuce ta kunna Tv tana xama akayi knocking ƙofa
''dama ace shine ya dawo'' ta faɗa sanda take kama handle ɗin, wani rin baya tayi kaman xata faɗi da sauri ta riƙeta tana shigowa falon sosae
''me ya kawoki nan? yama akayi kika shigo tukun?''
''ke kinga kwantar da hankali ko kin manta kina ɗauke da cikin ɗana ne?''
😳😳
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Srory and writing by
Officialraah444

Page 30
Typing.....✍
''me kika ce?'' miƙewa faɗhima tayi tana murmushi tace
''cewa nayi ko kin manta kina ɗaukeda cikin ɗana ɗan ɗan uwana?''
''faɗhima meya kawoki gidana?'' ta faɗa tana danne xuciyarta
''ba wani mummunan abu ya kawoni gidanki ba, just to check on u and

congratulated u, Allah raba lfy''
''kinsan baxan taɓa yarda da wannan maganar taki ba''
''toh wannan ya rage naki''
''Hajiya babbane ta turoki koh?''
''babbar matsalar da ake samu a kullum kuma a ko da yaushe kenan, wae dan Allah ke baxaki taɓa sakawa xuciyarki ruwan sanyi game damu ba? mufa yan uwankine duk yanda bama son juna muɗin yan uwan juna ne kuma bamu taɓa riƙarki da komae ba''
''wannan ba gaskiya bane, kwata kwata wannan ba gaskiya kika faɗabaa!!! yan ɗakinku, manya da yara babu wacce suka tsana kamar ni, kuma a fili kuke nunawa, shine xakice ƙaryane!" lumshe idanuwanta faɗhima tayi tana ƙoƙarin maeda tears ɗinta tace
''no body will force u to love us, amma ki sani babu dalilin da mu xamu ƙi ki, saboda shine abunda mahaifinmu yake so, sannan mu da kike ganin bama sonki muna mutuƙar ƙaunarki a baya lokacin kina yarinya kafin a rabamu dake''
''ni ban yarda ba, nasan koda duka yan gidanmu xasu soni banda ku da Hajiyanku'' ta faɗa tana sakin kuka, itama faɗhiman cikin kuka tace
''ki kalleni da kyau adawiyah ki faɗamin lokaci ɗaya dana taɓa miki wani abu na cutarwa tun daga yarintanki har xuwa yau'' kauda kanta gefe tayi tana son tsaeda kukanta
''koda baki cutar da ni ba ae bakya sona''
''ni kuwa nake sonki, amma a yanxu baxaki taɓa gane hakan ba, ni xan wuce Allah bamu alkhaeri Allah kuma ya sauwaƙe'' daga haka ta ɗau bag ɗinta tafice, kallon ƙofan data rufo mata taketayi tana kuka

****

ABUJA NIGERIA

Shiru yayi yana sauraren AUNTYN har ta gama faɗan duk abunda take riƙewa a cikin ranta baece ƙala ba saeda yaji ta fara kuka sannan yasa hannayensa ya kamo nata yana maraeraecewa
''kiyi haƙuri AUNTY duka hakan bada niyya ya faruba fa''
''Ibrahim ni xaka raenawa hankali kacemin wae bada niyya hakan ya faruba?'' kansa da ya fara masa ciwo ya ɗan shafa yana cewa
''ehh AUNTY nasan dole xakiji xafin haka kuma kiga kaman ban kyauta mikiba after all the things u did to me, but do believe me wlh it's not intentional, wlh dagani har ita bamuso abbunnan ya faruba kawae rabone ya rantse'' yanda yaketa lallaɓata yana share mata hawaye yasata cewa
''kae kana son cikin ne?'' kasa amsawa yayi sae rufe idanunsa yayi da sauri irin kunya ɗinnan, murmushi mamyn tayi tana ɗan dukan bayansa tace
''ja'irin yaro ni xakawa wani iyayi anan?''
''kiyi haƙuri dan Allah AUNTYnah'' ya faɗa yana mata love da hannu akan ƙirjinsa
''ni dama ba wae ina baƙin ciki da cikin ko ina son axubar ne dan bana sonka

da haehuwa ba a'a kasan ance nono alƙali sannan uwar matarka ba mutuniyar arxiɓi bace dan ta fito ƙarara ta nunamin dalilin da yasa suke son cikin tunda kasan dae ba sonka suke ba daga uwar har matar taka abunda ka mallaka suke hange, kuma duk wannan sun ɗauko ne daga ainahin ita kakar matar taka dan kuwa 'Iya' ba tsohuwar kirki bace, Allah dae ya gafarta mata''
''Ameen mamynah''
''shine kawae abunda yasa bana son haɗa irin barin ma ace mace aka haefa she'll take after them wanda nikuma bana fatan har abada mu samu irin haka''
''AUNTY gaki fa sannan gani xamuyiwa babynmu addu'a kuma insha Allah nothing will happen, kuma AUNTY kin sani Rabi'ah isn't what u're thinking of kawae she's been covered from many things but am assuring u ta sauya'' baki AUNTYN ta taɓe tana cewa
''xo kaci abinci kaji ni ban damuba tama ci gaba da yanda taken mana''
Har ga Allah bae so kwana ba amma abubuwa suka riƙesa dole tasa a gida xai kwana, yana fitowa wanka ya kirata a lokacin tana xaune tana linke kaya dan tarasa me xatayi ma sae kawae ta kwaso kaya tana sake linkesu, kallon number tayi har yau batayi serving numbersa ba ya sani amma bae ce mata ƙala ba
''barkan amaryana da dare'' ya faɗa sanda ta gama amsa sallamansa
''ykk''
''ina lfy maman unborn ɗina fa?''
''nima haka''
''um masha Allah ba'ayi bacci ba kenan''
''um'' ɗan shiru yayi jin yanda take amsawa sae can yace
''ina fatan dae babu abunda yake ciwo kokuma abunda kike so''
''nikam m xanso tunda niaajiyar Allah ce, lfy ta klau''
''dan Allah kiyi haƙuri ban samu na kiraki ba tun daxu wlh na shiga busy ne'' kanta take jinjinawa kaman yana gabanta har ya gama
''shikenan sae da safe'' bata tsaya jiran yace komae ba ta kashe kiran ta saka wayan Flight mood ta kwanta a cikin kayan tana sakin ajiyan xuciya
Da subhi tana kan dadduma taji kaman motsi a falon ɗan saurarawa tayi jin da gaske motsin ne sae tayi bismillah tana gyara himar ɗin jikinta ta fito falourn, hasken wurin a kashe yake kuma switch ɗin tana daga can gefen water dispenser kuma opposite ne da wide ɗin, da yake ana fitowa falourn tv na daga bangon ƙofan so ta bayan kujerun xatabi ta kunna, ɗan ware idanunta tayi dan ba haske kwata kwata a wurin
Karaff taji anyi sama da ita, tun asali ita mutum ce da batada tsoro ko kaɗan dan haka ɗagatan da akayi bae bata tsoro ba kwata kwata sae ma wani fusatata da abun yayi kunsan abu ga mae ciki hannu ta ɗaga daedae xata bugesa ya sauketa akan gadon a hankali yana kunna bedside lamp
''hiii dear'' ya faɗa yana sakin dariya, kallonsa take idonta cike da mamaki kafin tayi gethering caurage tace
''wae kaen.....meye yasa ka dawowa yau? nayi tunanin ae xaka ƙara koda sati

ne'' ta faɗa tana maye gurbin mamakinta da harara
''ina xan iya xuwa batare da kayana ba'' ya faɗa yana ɗan mata cakulkulo, bakinta ta taɓe tana jan gemunsa
''amma ae yanxu kaje ka kwanan koh?''
''ae wannan ne na ƙarshe hakan baxata sake faruwa ba'' bakinta ta taɓe tana juya masa baya, da sauri ya xagaya inda ta maeda fuskar tata, sae ta ƙara juyata ya ƙara juyowa tana kuma juyata sae ya kwanta a gadon shima sannan yasa hannunsa duka a ciccoɓota ya ɗora kan cikinsa ya maƙalƙaleta sosae
Suna xaune wurin 11:30pm tanata bashi labarin rayuwarta ta secondary shidae saedae yayi murmushi kokuma ya rungumeta idan abun dariya ya kama kuma yayi, sosae yake kallonta baya yarda ta fice dga sign ɗinsa, jin tayi shiru yasashi cire tagumin da yayi yana cewa
''kikayi shiru kuma''
''ehh na gama saura kae'' idanunsa ya fito dasu yana nuna kansa da yatsa, sae ta jinjina masa nata kan
''amm.....''
''a'a ni gaskiya sae kamin labari''
''toh shikenan shikenan amm....''
''ka ban labarin ku'' girarsa ɗaya ya ɗaga alamar bae jane ba, sae ta kama hannunsa ta jasa cikin jikinta hannunsa na gefen cikinta tace
''ehh mana labarin rayuwarku bayan mutuwan mamanku''
''there's nothing new about rayuwanmu ae, u know everything''
''everything as how? ni ae bansan komae ba kae da ba a ɗakinmu ka taso ba, kufa ba yan uwanmu bane'' kallon bakin dake maganar yayi yana ƙaramar dariya
''idan aka hangoki daga nesa kaman wata babba sae an xauna dake a gane how childish u're'' bakinta ta turo gaba tana dukansa
''wlh ni ba yarinya bace tunda yanxu na kusa haehuwa''
''aaaaaaaaa, takusa me?'' dariya suka kwashe da ita sosae tana rufe fuskarta da hannu
Officialraah444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 31
Typing.....✍
''bayan rasuwan mother ɗinmu ni ina gun AUNTYna Jamilah kuma ta koma gun dangin dr. lokacin ae kinga tana ƙarama nakanje duk bayan hutu har

naxo na tafi institut auf dem Rosenberg a can nayi secondary''
''what, what, what wae a wannan makarantar kayi karatu?'' kansa ya jinjina mata da sauri tace
''amma wannan makarantar ae tafi ko wacce makaranta tsada a duniya fa ko ba wacce take a Switzerland ba?''
''ehh ita fa, acan nayi karatuna daganan na wuce Cambridge University acan nayi mastered degree ɗina na fara aeki a wani clinic ɗin dr. dake Poland for almost 2 years sae na koma dan yin professional studies ɗina sae nayi changing of institution nayi a Harvard saboda gida dake kusa da ita ina gamawa na fara business which is my dream kuma gadona tunda mahaifina anan yafi bada ƙarfi, shikenan labarin namu''
''umm interesting amma fa baka iya bada labari ba Allah kawae summarizing kamin''
''yah dama na faɗa miki ae''
''kuma sister ɗin naka ban taɓa ganin taxo gidanmu ba'' ''Yah bata xuwa Nigeria randomly gaskiya''
''amma duk bukuwan da ake a gidanmu ba taɓa ganinta ba''
''baki taɓa lura da itana dae amma tana xuwa''
''ummm toh amma su anee ina abbansu? ban gansa ba har akayi abubuwan bikinmu aka gama fa?''ɗan tsaki yayi yana gyara mata kwanciya
wani sakarae ne uwar tasu ta fara soyayya dashi babansa shine minister of transportation na Ethiopia, tun ganin farko danama yaron naji bae kwanta min ba na nuna mata ni bana sonsa amma yarinyarnan bataji ba suketa tarayya nikuma dana gano haka sae na cire hannuna daga lamarinta ban kuma cewa uppan ba, a haka har lokacin bikin yaxo banyi niyyar xuwa ba amma ana gobe auren data kirani tanata kuka da lallaɓani sae naji jikina yayi sanyi dan nasan she doesn't have anyone better than me, lokacin ina professional studies ɗina, before Fatiha na xauna nayi magana da shi akan yanda nakeso xamansu ya kasance dan baxan ɗauki iskancinsa akan ƙanwata ba a gaban dubban mutane ya amince da rules ɗina sannan aka ɗaura'' ɗan shiru yayi for breath sannan yaci gaba
''at first kaman komae lafiya lau, dan duk sanda na tambayeta tana nunamin all is well, so nasan yarinyar akwae xurfin ciki morethan u think so ina monitoring xamansu komae lafiya except when she get pregnant, ya fara fito mata da wasu halaye masu wahalar tafiyarwa saboda taƙi yarda suyi aborting baby's ɗin thought a lokacin ma ba'asan twins bane, so akwae house help da aka kae mata ita take faɗawa ita mom ɗin gidanmu ita kuma ta faɗamin, so ni inada wani abu sam bana bari ƙaramin abu ko babba ya ɓata alaƙana da mutane, sanda na gano how they treated my sister sae naje kae tsaya to his mother matar sae ta nuna kaman batasan komae ba iri ae ɗan baya nunawa a gabanta ban tsaya sauraraenta ba i left so daga lokacin sae abun ya ragu sosae except when do find out abunda ke cikin are twin's female twins, sae suka tada rigima kuma wae a masu tada rigiman hada yaran Uncle ɗinsa''
''saboda samun wuri'' ta faɗa da mamaki, kansa ya jinjina yana ci gaba

''ita yar uncle ɗin nasa daya doctor ce itace ta bada shawaran aje ayi inducing yaran'' idanu Adawiyah ta xaro tana kama bakinta da hannu jin xallar imani da ya cika wannan mutane
''so sae yaxo ya sameta wae yayi magana da yan uwansa sun faɗa masa wahala ce xa'a kawo masa tun yana yaronsa xa'a sakashi ya tsufa ba mataemaki sae ƙarin wahala dan haka xa'aje ayi inducing yaran, kae tsaye ta nuna bata yarda ba hakan sae ya tada wani sabon tashin hankali sae ta nuna tanason kawae auren ya rabu data nuna hakan sae kori duka house help ɗinta sukayi torturing nata a wani ɗaki no phone no any accessory abinci ma random abu suke bata, infact dae kaman wata slave, toh mutane sunga kwana biyu shiru dan ita mutum ce da bata iya xama babu communication
A tafi a tafi almost three weeks mom batajita ba idan ta faɗawa dr. sae yace maybe koh abun cikin ne data gaji sae tayi deciding ta kirani, so a lokacin ashe itama AUNTY da danginmu da yawa sun lura da hakan, sae ta riga kirana ta sanar dani sudae hankalinsu ya tashi so sae na lallaɓata munyi maganar ba jimawa grandma ɗinmu ma ta saka aka kirani wae sunje gidan Jemie an hanasu shiga ance masu babu mae irin sunan a gidan, kinsan babban abun tashin hankalin?'' kanta ta girgixa masa da sauri dan ta ƙagara taji yanda aka ƙare
''muna cikin magana da ita mom ta ɗinga kira, in taƙaece miki basu barni ba a ranar sae da suka tabbatar na isa Chicago so da xan tafi duk boys ɗina almost 26 ne tare dasu na tafi a private jet ɗina dukkansu suka saka suit black nikuma na saka shadda white, so gidansu is in the suburban opposite lightscape botanic garden so akwae babban filin da xae ɗauki 2 jet at a time anan mukayi parking namu muma aka kawo mana motoci suka idamu har gidan, kafin mu isa wasu daga cikin boys ɗina sunje sun daki guards ɗin har sun buɗe mana suna tsaye suna jiranmu, sanda naje basanan ma masu gidan akwae wani festival da sukeyi bean day (ranar wake) a cloud gate dukkansu sun tafi can, thanksfully akwae CCTV a gidan ta cikin wannan cameran akayi tracing event that are happening mukayi copying ɗinsu sannan naje da kaena na fito da ƙanwata dake tsakanin rae da mutuwa daga....h.h.han...nunsu..'' lumshe idonsa yayi saboda wani ɗaci da yakeji yana mamaye masa wuya, ruwan da ke kan bedside ta janyo ta tsiyaya masa a cup ta basa ya sha saeda ya ɗan dawo nutsuwarshi sannan yaci gaba
''direct hospital na badata nikuma na xauna a gidan almost 2hr sannan sae ga masu gidan sunje sun gama yin yanda sukaga dama sun dawo duka a gajiye boys ɗina sae suka hanasu shigowa aka kirani aka sanar dani cewan sun iso, dukkansu sun shiga mummunan shock da suka ganni kuma a take a wurin na bada umarni yarana suka karya masa hannu before police come and chase him, kuma nayi suing nasa to court as i promises him, ba'a wani wahalar da shari'a ba saboda i have everything in hand kawae akayi prison dashi jukuncin bullying matarsa for 15years, sae muka ci gaba da kula da ita har ta haefi yaranta tunda sukaxo duniya koda a hoto ban taɓa yarda dangin ubansu suka gansu ba sae da sukayi 5years a lokacin da kaena nace ta kae

ma kakarsu ta gansu, so yanda ta nuna xagwaron jin daɗi yasa har yaran sukan ɗan je time to time suma da sun fara xuwa wae duba yaran sae suxo sau 2-3 per month shine na hana, amma yanxu everything goes well''
''toh amma uban fa?''
''he die'' idanunta ta buɗe a tsorace xatayi magana ya janyota ya mata rumfa yana saka hannunsa a lips ɗinta
Officialraah 444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 32
Typing.....✍
A haka kwanakin suke tafi da sauri yau gashi har cikinta ya kae seven month, duk ƙarshen sati da kansa yake kaeta check up shi yake driving sannan ya xagaya da ita cikin gidan duk bayan subhi prayer, xae tsareta taci abinci koda kuwa bayanan da lokacin cin abinci yayi xae kirata video call har sae ta gama ci, haka idan lokacin bacci yayi xae kira ya musu addu'a yana mata fira tana amsashi har sae yaji tayi bacci sannan ya kashe yayi abunda ke gabansa
Abuja xasu tafi dan tun farkon samun cikinta da sukaje Abuja bata kuma xuwaba sae a jiya da yace ta shirya xasuje saboda bikin khaleed da khaulat da xa'ayi haɗe dana humaerah da hindu yar gidan uncle musa da xa'a fara duka a jibi Tuesday
Duk abubuwan da tasan xata buƙata ta gama haɗasu shima nasan ta haɗa ta fitar da duk abunda xae lalace before dawowanta dan ba tare xasu dawo ba yanxun ma bayanan daga Morocco xae dawo a yau ɗin gobe kuma su tafi Abuja ita har ga Allah bataso sae yaxo nan ba amma he insisted dole sae yaxo ya tafi da ita, tana cikin haɗa kayan aysha da yake anan yarinyar take hutu yanxu tana cikin sati na biyu, ta jiyo dirin motocinsa dan convoy aka masa
Sae da ya gama sallamar yaransa sannan ya wuto da sallama ya shigo falon as usual, kallon inda aka ajiye luggages ɗinsa yayi sae kuma ya ɗaga kansa yana kallon parlourn daketa ƙamshi, baeji motsinta ba da alama tana ɗayan parlourn can ɗin ya nufa da sassarfa aekuwa yana tura ƙofar yayi kyakyawan gani
Tana ɗan xaune jikin hannun kujera jikinta sanye da leshi black an masa kyalliya da maroon and light green ɗinkin bubu tasha ɗauri mae V shape wuyanta da hannu sun sha gold sae walwali suke tanata tashin ƙamshi, hannayenta dake naɗe ta warware tana ware masa su, a hankali ya fara takowa kaman irin angonnan idan ana event anxo shigowa dashi da abokansa

a baya, wani irin lumshe ido sukayi lokacin guda feeling each others present almost a minute before they break the hug
''welcome hubby'' ta faɗa cikin raɗa bayan ta kara kanta jikin haɓansa ta saka tafin hannunta ta kama gefen haɓan
''nice seeing u wifey'' shima ya faɗa yana kama hannayenta
''ya babynah?'' hannunsa dake cikin nata ta ɗora kan cikin da xa'a iya cewa bae wuce wata 5 ba
''lfy lau tana missing masoyinta''
''masoyinta ma yana missing ɗinta, Bismillahi Allah'' ya ciccißeta dukanta sukayi ciki
''wae ina yar hutun taki ban ganta ba?'' ya tambaya yana cire spoon daga bakinsa
''wallahi wae wanka na kuma mata na barta tana ni ina haɗa kaya kawae bacci ya ɗauketa so sae na gyara mata kwanciya na kyaleta, shine fa har yanxu shiru ba'a tashi ba''
''da alama ana kula da baƙuwarnan sosae'' dariya tayi tana cewa
''koyo ne nake kafin tawa taxo''
''ya dae kamata''
''yanxu goben da wuri xamu tafi koh?'' ta faɗa tana dafa shoulder ɗinsa, hannu yasa ya lakaci hancinta yace
''uwar xumuɗi ae kin bari goben tayi koh? wae ma wait kin haɗa komae naki dae koh'' bakinta ta buɗe tana dariya tace
''Ehh na gama komae, wae ya akayi ka iya sakawa mutane suna kaman wani cikakken bahaushe?'' dariya sosae ya saka yana ratayo kanta ya matse
''me kika mayar da ni?'' jin ta kasa ƙwace kan nata yasata cewa
''babban yayana'' dariya ya kwashe da ita sosae yana sakin kan nata ya rakata da ɗanƙwashi
''kin ceci kanki yarinya'' kan take sosawa itama tana dariyar, sae ga aysha ta fito tanata sosa idanu
''aysha lfy?'' ta faɗa tana kama hannayenta
''anty hayaniya ta hanani bacci'' inji yarinyar tana kallon KONTO dake kallonsu shima, gira adawiyah ta ɗaga masa tana pointing masa aysha dake kallonsa
''kinga baby inaga kuwa hayaniyan yayyenki dake wajene bara naje na musu magana''
''a'a ba hayaniyansu bane it's your laughter'' komawa KONTO yayi yana jingina bayansa da kujeransa
''shikenan toh xo kici abinci''
''no am not hungry, xansha yoghurt''
''toh ina xuwa'' ta faɗa xata wuce yayi saurin cewa
''kinga xauna bara naje na ɗauka mata'' daga haka ya tafi gun fridge dan ɗauko mata
Suna xaune a kan gado wurin 12am magana suke akan wani business nasa tun ɗaxu jin fara jin bacci, sae ta miƙe tana cewa

''koxo kayi wankan mu kwanta bacci nakeji'' hannu ya saka ya janyota ta dawo jikinsa
''ki bari anjima muyi wankan gaba ɗaya mana''
''me yasa toh sae anjima?'' lowering eyes ɗinsa yayi yana shafa bare neck ɗinta cikin wani irin murya yace
''kinaso kisan dalili?'' juyowa tayi tana masa irin kallon da yake mata
''xanso insan dalilin kuwa? umm a'a nama sani ae'' ta faɗa tana haɗe forehead ɗinsu
Washe gari tun wurin 11am suka wuce Abuja da yake a jirgi ne babu jimawa suka isa, masallaci yace a saukesa sukuma akayi ciki da su har bakin part ɗin mamy tasaka a kae ta saboda dangin Ummah na can garinsu duk sunxo so gidan akwae yar hayaniya kuma batason ayita kallonta shiyasa har ƙofarsu aka kaeta sae ga maids ɗin mamy sunxo da kansu suka tareta kamar wata gimbiya sukayi ciki da ita
''oyoyoooo ga mum unborn'' sumee ta faɗa tana xaune a tsakar falon mamy ana mata lalle
''oyoyo ga sweetheart'' ta faɗa tana bata hannu suka buge dan ba'ayi xanen a cikin tafin hannun ba
''tun ɗaxu muke kallon hanya, har ya Aliyah ta gaji ta shig..''
''bacci koh?'' ta tambaya tana janye gyalenta ta jefar a kujera
''wlh kuwa keda kika san ya Aliyah da rashin son xama''
''Allah kyauta mata dae, ina mamy?''
''mamy ta shiga part ɗin Ummah'' da mamaki take kallon sumee a'iya saninta dae basuda matsala da Ummah dan mace ce datasan kanta amma ae mamy bata wani shiga harkarta in ba gaesuwa ta mutunci da sukeyi ba
''me ake a part ɗin naku da har mamy ta tafi?''
''Abby insist wae xasu shafawa indo lalle dole itama taje ayi da ita'' kanta ta jinjina tana kwalawa maid ɗinsu kira
''wae ku meyasa kullum sae ance kuyi abu kukeyi ne?'' ɗan shiru matar tayi tana kallon ƙasa
''nima fa ishirwa nakeji'' cewar Aysha a ɗan kwaɓe
''shiii ba Uncle ya hana magana irin haka ba?'' cewar adawiyah tana hararan Ayshan, tura baki yarinyar tayi tana kauda kanta
''kije kekuma ki kawowa mutane ruwa dan Allah kafin mu mutu da ƙishi'' juyawa tayi da sauri deep down tana tunanin abunda ya sauya adawiyahn haka?
Readers ana tambaya fa
Officialraah 444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)

Story and writing by
Officialraah444

Page 33
Typing.....✍
Kallon ruwan da aka ajiye a gabansu sukayi, wani irin xabura Aysha tayi tana juyawa ta xumɓura baki, ita kuwa gimbiyar ae baki ta saki tana kallon matar dan mamaki sae kuma ta girgixa kae cike da takaeci amma kafin tayi magana sumee ta rigata
''wae dan Allah ku wanne irin dull ne eyeh, i said which kinda dull are u? yanxu mtarnan tace a basu ruwa shine xakije ki ɗauko wannan ruwan xalla kixo ki mimmiƙa masu? babu wani refreshment sae kace wasu almajirae bayan kinsan mutananan daga tafiya suke''
''wae dan Allah yaushe part ɗinmu ya xama haka ne?'' ta faɗa tanabin bayan maid ɗin da kallo
''iskanci koh, wae yanxu nan sakene suka samu sun samu wuri''
''allah kyauta, Aysha jeki part ɗin Ummah ki kira mamy dagacan sae su xuba miki abinci'' miƙewa yarinyar tayi da sauri ta wuce
''bara naje na watsa ruwa xafi nakeji'' daga haka tayi samansu
Tana kwance cikin bathtube Sosae takejin gajiya dan ta jima batayi tafiya mae nisa ba, ƙafafunta sun ɗan tasa abun xama tana fitowa ta shirya ta shafa rob a ƙafan sama sama dan baxata iya dannawa yanda xata saki ba, doguwar rigal material ta saka babydoll maternity saboda cikinta da bataso ya fito dukda ma batada girman ciki tunda in ba ga wanda suka saniba idan aka kalla a ido baxae wuce girman wata huɗuba flip flops ta xura a ƙafarta pink ta yane kanta da mayafi ta ɗauko wayarta ta fito tana ɗan shafa cikinta
''kae mum unborn wannan kyau haka'' cewar sumee itama mae mata lallen saeda ta yaba, itadae murmushi tayi tana addu'a a xuciyarta a fili kuma tace
''bara naje na gaeshe da hajiya babba'' idanuwa sumee ta buɗe da mamaki amma batayi magana ba
Da sallama ta shiga parlourn AUNTY, dukansu suna cikin falon tun daga kanta, sae meenal da na'eem dake ɗauke da ɗan faɗhima takwaran Abby suna ce masa yayah, dukansu juyowa sukayi suna kallonta da mamaki ita kuwa dake xuciyarta tayi ta ƙarasa har kusa da kujerun daga ɗan baya ƙaɗan ta duƙa tace
''barka da wuni hajiya babba mun sameku lfy?'' kasa magana AUNTY tayi sae kallonta da suke barin ma meenal daketa ƙoƙarin ganin cikin adawiyahn amma da yake batada girman ciki kuma ga yanayin rigar da ta saka sae wani tunanin yaxo mata a ka, itama AUNTYn dan babban macene shiyasa har taga alamomin sa da tunani irin na meenal itama xatayi shikuwa Farouk ƙoƙarin ɓoye mamakinsa yayi yana sauke yayah daga jikinsa yace
''AUNTY bara naje na ɗan watsa ruwa inaso xan fita ne'' kanta AUNTYn ta jinjina masa dan jan faɗa sae ya biyo ta gefen da take a duƙen ya wuce yana buge mata guiwa da gangan, itama AUNTYn sae ta miƙe tana cewa meenal

''bara na shiga ciki i want have some nap'' daga haka ta shige sae ya rage su biyu kawae ganin hakan sae ta miƙe xata wuce, yanayin yanda taxo mikewa ne ya taemakawa meenal taga cikin saboda ɗan banƙarowa da tayi
''huum Allah sauwaƙe marasa sanin ciwon kae dae, anata wani 'ni bana sonsa da na auresa gwara na mutu yan,yan,yan' yanxu gashinan ana fama da ƙaton abu kuma nasa'' murmushi tayi tana juyowa ta kalleta ido cikin ido tace
''uhm kae meenal kenan, ance ta yaro kyau take bata ƙarko, nikam inda xan baki shawara da sae nace ki fita harkar mutumin da kinsan cewa baxaki taɓa samunsa ba, a shawarce ki nemi daedae ke ki aura'' a wani irin fusace meenal ɗin ta miƙe tana cewa
''ke har kin is.....''
''shiru!! rufemin baki ko in mammareki anan'' ta faɗa tana ɗora yatsanta a baki, aekuwa meenal ɗin shiru tayi tana kallon old form ɗin adawiyahn
''idan ina magana dani kisan abunda bakinki xae rinƙa faɗa dan bakin rijiya ba gun wasan makaho bane'' jin an turo ƙofar sae ta saki smile tana cewa
''thank u sis''
''me yan uwa biyu suke tattaunawa ne?'' cewar Abby dake shigowa, wani cool smile adawiyah ta saki tanayin gunsa
''barka da wuni Abby'' rungumeta Abby yayi yana tambayarta hanya
''na leƙa part ɗinku ae akace kinanan ɓangaren babarku'' ya faɗa suna xama tare akan kujeran dake pacing ƙofar shigowa
''ehh wlh Abby naxo gaeshe da hajiya ne'' meenal dake kallonsu ta gaeshesa tana xama kusa dashi itama
''kun gaesa da uwar taki koh? lfy lau Aminatu kina lfy?'' Ya tambayi adawiyah yana kuma amsawa meenal daketa harare-harare, sae ga KONTO ya shigo cikin ɗan sauri sae kuma yayi turus ganinta a sake tare kuma da Abby, ganin suna kallonsa sae ya ɗan daedaeta fuskarsa yana ƙarasa
''Abby barka''
''yauwa Ibrahim barka'' ya faɗa yana miƙewa itama adawiyah sae ta miƙe yana bin Abby ɗin
''muje falonka father'' ta faɗa tana saƙala hannunta jikin nasa
''ya Ibrahim sae yanxu aka leƙo gaeda mamyn?''
''Aminatu manya, ke in banda abunki ae an wakilceni koba nan naxo na iske matata ba?''
''toh kuma ya Ibrahim matarka kae ne?''
''meye banbanci toh ae abunda ya yini shi yayi matar tawa, yanxu dae ina AUNTYn?
''abunda fa yayika ya bashi yayi matarka ba, tunda yanda xaka gaeshe da AUNTY cikin ladabi matarka baxatayi ba''
''kinga ni banason wannan anyi ance ɗin ina ita AUNTYn take?''
''tana ciki'' ta faɗa tana taɓe baki ganin kamar jira yake yawani yi gaba

CHARBIN KWAE??
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 34
Typing.....✍

Xama yayi a saman gadon bayan sun gama gaesawa
''ya hidima kuma, abu ya kankama ba kama hannun yaro''
''aekuwa dae masu abun sun dage sunata shan shagalinsu bah''
''gidannan kunajin daɗinku kullum cikin shagali kuke''
''shagali ae mun kusa gamawa yanxu kae xakaxo ka ɗora gidanka xa'ayi abun yanxu tunda kun kusa saukewa'' ta faɗa tana ɗan hararansa yasan me take shirin faɗa shiyasa yace
''AUNTY bara na tashi inaso na watsa ruwa sae naci abinci''
''Allah na tuba Ibrahim dan xakayi abu har sae ka faɗamin? ae yi gaban kanka kawae ko ka manta ka girma ne? you're yet to became a father''
''haba AUNTY mun fa gama maganarnan dake dan Allah karki tado....''
''au kar na tadota? saboda ka maedani mutuniyar banxa koh? tunda munyi magana shine sae ka gama gararamba ka nunawa mutanan gidannan ni a banxa nake sannan xakaxo ka gaesheni tunda yanxu kanajin ka isa koh?'' shiru yayi yana saurarenta har ta gama faɗanta sannan ya sauko ƙasa yaje ya kama hannunta ya rungume yana cewa
''kiyi haƙuri AUNTY wlh tallahi babu inda n tsaya ban samu isowa cikin nan ba saboda part ɗin hajjah dana wuce shiyasa but do believe me babu inda na tsaya ina fitowa direct nan nayo'' kallon sa take dan ganin gaskiyarsa kanta ya jinjina mata sae ta janye hannun
''idan na gano ba gaskiya ka faɗamin ba koh?''
''kae AUNTY inace matar tawa ma anan part ɗin na isketa''
''atoh na sani ko gun uwarta ka tafi ka tare'' dariya yayi yana miƙewa
''nidae ba ruwana da wannan rigiman Allah, bara naje na watsa ruwa''
''sae ka gama xakaci abinci?''
''ehh sae na dawo ba'' ya faɗa yana jan ƙofar dan har ya fita
Yana fitowa ya ɗauki hanyar part ɗinsu ya hangota tana tafiya, wayarsa dake aljihun wandonsa ya ciro yana ci gaba da takawa ya kirata tana gaf da isa part ɗin Ummah itama dan Abby ya sallameta, kallon wayar tayi sae kuma hakanan ta juya bayanta kaman ta sani suka haɗa ido tsayawa tayi tana kallonsa yanda yake yowa gunta da yar sassarfa, murmushi take tana taɓa masa har ya ƙaraso
''awwn a gaeshe da angona'' yana dariya ya saka hannu ya juya mata kanta ya kalli ƙofar Ummah

''muje nima na gaeshe dasu'' batace komae ba taci gaba da tafiya yana binta
Suna tura ƙofar hayaniya ta fara masu welcome dan fin rabin falon a cike yake su Ummahn kuma suna falon sama, mutanan dake wurin ya soma gaesarwa tayi saurin kama masa hannu ta jasa sukayi sama, sakinsa tayi kafin su ƙarasa falon suna kan steps ɗin, ta juyo tana kumbura masa baki
''waye yacema idan anga gungun mutane tsayawa ake ayita wani gaeshesu?'' hannunsa ya ɗora akan shoulders ɗinta ya sakata a tsakiya yana cewa
''Toh matata baxan kuma ba'' da sauri ta ɗago middle finger ɗinta tana nunasa
''gwarama kar ka ƙara dan idan ka ƙara koh...huum i won't spare u''
''oo really?'' blinking ta masa tana cuckling cikinsa, baya yayi yana dariya, itama dariyan tayi tana yin gaba
Da sallama suka shiga falon, Ummah na xaune da wasu oils a gabanta tana mixing da alama na amaryar ne sae mammah dake mixing humra ita kuma humaerah na xaune a kujera ta naɗe ƙafa da wani bowl a hannunta tanacin pepper soup sae ɓata rae take sae hajiya mamy a hakimce tana cin kaxa da wayarta a hannu, duk juyawa sukayi jin sallamarsu har mamy ɗin
''ya yan Abuja'' cewar Ummah tana miƙawa adawiyah hannun da bata ɓata ba, gaeshesu KONTO yayi one by one duk duka amsa suna tanbayarsa hanya da aeki
''alhmdlh wlh su A'ishah lokaci kuma yaxo? toh Allah sa alkhaeri''
''ameen ameen, ameen ya Allah''
''mamy ya hidima'' ya juya yacewa mamy, ɗan taɓe baki tayi tana amsawa cike da isa, shidae addu'a ya kuma musu ya miƙe yana kallon yanda ta wani shige jikin Ummah dake shafa mata oil ɗin a check sallama ya masu ya fice abunsa
''sannu da aeki Ummah anata shan hidima'' ta faɗa bayan ya ida ficewa
''wlh kuwa adawiyah an iso lfy ya hanya''
''alhmdlh Ummah yunwa nakeji'' ta faɗa tana shafa ɗan cikinta, da sauri mamy tace
''toh tun da kuka iso kina aekin me dabaki sa an baki abincin ba?'' ɗan tsaki tayi tana cewa
''a part ɗinmu inaga ba'a gamaba''
''kinaga ba'a gamaba kokuwa ba'a baki ba?'' bakinta ta taɓe tana sauka ƙasan carfet ɗin ta kwanta rigingine da sauri duk sukayi kanta suna kiran sunanta har ta ɗan tsorata
''kaeee! wannan ihun naku ae xae iya saka cikin ma ya xube'' ta faɗa tana tattare rigarta tayi saman Ummah
Bacci ya ɗauketa a bedroom ɗin mamy bayan Ummah ta bata abinci tunda ta kwanta sae da kaɗe-kaɗen da aka fara na wuni suka cika mata kunne wanda suka sakata farkawan dole, ƙafarta da ta ɗan kumbura ta kalla tana xurota ɗan tsaki tayi ganin yanda time yayi nisa gashi koh sallah batayi ba
wanka tayo tare da alwala jikinta sanye da farin towel ɗin mamy wanda ya sauko mata sosae, tana gama sallah kenan akayi knocking sau ɗaya juyawa

tayi da sauri suka haɗa ido yana tsaye rabinsa a ciki rabi a waje ya rungume kyaure ya haɗe bakinsa wuri ɗaya ya turosa, murmushi ta masa tana matsawa inda yake tana cewa
''masoyii barka''
''barka masoyiya, hope kinci abinci'' ya faɗa yana tareta da hannayensa ya xagayeta dasu
''naci abinci nakuma yi bacci na huta'' hannunsa ɗaya dake jikinta ya ciro ya shafa fuskarta dakenan kaman ta jinjira yace
''amma kuma matata isn't all right i guess'' bakinta ta ɗan taɓe tana cewa
''ummmm.....ehh ban ɗan jin daɗi ƙafana ne ke ɗan ciwo''
''subhanallah let me see'' ya faɗa da sauri yana surarta yayi kan gadon mamy ya ajiyeta yana duƙawa ya kama ƙafarta
''bara na duba na gani'' ya faɗa yana ɗan daddanna ƙafar
''ina kika ajiye massage oil ɗinki ne?''
''ban taho dashi ba'' idanunsa ya xaro yana cewa
''baki taho dashi ba as how?'' bakinta ta tura tana kallon gefe cikin maganar shagwaɓa tace
''toh ni mantawa nayi inata saurin xuwa bikin ƙawata'' kansa ya girgixa yana xaro wayarsa yayi kira
''toh kwanta ki huta kafin a kawo wani oil ɗin'' kanta ta jinjina tana kallon ƙeyarsa daya juya mata yana ɗan kalle-kalle a ɗakin
''amour nan fa ɗakin mamy ne ba ko ina xata kalla ba'' murmushi yayi yana dawo da idanunsa kanta
''ehh nasan ɗakin mamy ne, surkana'' murmushi ta saki har haƙoranta na bayyana ta lakuce masa hanci
Kauna yar leda

Officialraah 444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Typing.....✍
Hannuwan ya kama yana yin kneeling ya murɗesu baya yana kae fuskansa jikin tata sae wayarsa ta ɗauki ringing ganin wanda xae kawo masa saƙo ne sae ya saketa ya miƙe ya fice yana faɗan
''kin sila yarinya da sae kin faɗawa yan garinku'' dariya mae sauti ta saka dan yana jinta har ya fice falo bae jimaba ya dawo hannunsa riƙe da avender

oil babban maxubi
''yauwa bara mu shafa mugani koh?''
''ehh mu ɗan yi sauri kaga biki har ya fara nisa'' chin ɗinta ya ja yana saddawa ya fara mata massage yana shafa mata oil ɗin
''kinaji kullum da dare xan riƙa ƙoƙarin samu ina xuwa ina maki massage dan kar ƙafan ta baki wahala a gaba, dama gata da laushi kaman tawa, upp bata kae tawa ba dae amma ya ɗan yi rabi'' ya ƙarasa yana ɗan dariya jin tayi shiru kuma yasan halin kayarsa ya sakashi ɗaga kansa ya kalleta, bacci take a yanda taken murmushi yayi yana ƙarasa mata massage ɗin ya miƙe ya gyara mata ƙwanciya ya xaune kan bedside yanadduba sauran magungunan da aka haɗo dasu, hannunsa ya kae ya dafa forehead ɗinta can ƙasan lips ɗinsa ya furta
''Allah saukeki lfy'' da sauri na nace
'ameeeeeen'
Almost 10pm ta farka da ƙyar ta iya yo wanka ta rama sallolinta saboda wani mugun yunwa da takeji tana gamawa kuwa tayi ƙasa da sauri saedae tana xuwa daedae ɗakin mamy wani abu ya ja hankalinta komawa tayi da baya ta ɗan maƙale jikin ƙofar
''ae bansan wacce irin mata bace Rabi da koh me xaki mata xata shanye ta maedo miki aniyarki, yanxu har na rasa me xan faɗa mata dan na fusatata'' ɗan shiru mamyn tayi da alama wani abu ake faɗa a wayar, sae kuma tace
''toh ae duk na faɗa mata wannan, ke har fa cemata nayi naje an gwada kuma an tabbatar min babytah twins xata haefa mace da namiji kuma sune xasu gaje komae na ubansu baxata tashi da koh allura ba, kinsan data buɗi baki me tace?'' hannunta dake jikin bakinta adawiyah ta sauke tana ƙara nutsuwa jikin ƙofar
''wae duk abunda ya samu bawa daga Allah ne kuma ita bata taɓa damuwa da dukiyar yaron ba tunda dae tasan ba ita ta basa ba Allah ne can u imagine? wae har take cewa abunda xa'a haefa ko menene xataso tunda na ɗanta ne amma kuma mu baxata taɓa sonmu ba saboda bamu fito daga tsatson kirki ba'' shiru for some minutes sae kuma taji tace
''wato duk yanda xan tsoratata in tayar mata da hankali dan ta tashi na alhaji so take hakan ya tashi a banxa kenan? har yanxu halinta na son maedawa mutane aniyarsu yananan ashe, jar yanxu wannan kyakkyawan xuciyar tata tananan, toh kuwa ta jawa kanta naso nayi hakuri kam amma yanxu na fasa sae na cigaba da xuba mata gubar da xata sakata ta nemi saki d.....'' janye jikinta tayi a hankali daga ƙofar ta juya xuwa ɗakinta
A bakin gadonta ta xauna tana sauke numfashi kaman wacce tayi race saeda taji ta dawo nutsuwarta sannan ta matsa ta kwanta ta rufe jikinta da duvet amma fuskarta na waje
''mamy why? why mamy? baxaki bar hajiya babba ta huta ba? me kike nema ne wae ke?''
Washe gari yana gama sallah yayo part ɗinsu ya mata massage ya bar gidan wurin 7am, itama tana gama yin wanka ta fice jikinta sanye da Turkish abaya

ƙafarta sanye da Wellington boot saboda ɗan sanyi da ake ta nufi part ɗin AUNTY
Da sallama ta shiga lokacin AUNTYn ce kaɗae tana juya tea gabanta da kayan breakfast, ɗagowa tayi suka haɗa ido da sauri adawiyah ta sadda nata ita kuma AUNTY sae kallonta take har ta ƙaraso kusa da inda take ta duƙa cikin sanyin murya tace
''ina kwana an tashi lfy?'' shiru sukayi for almost a min kafin ta amsa
''lafiya'' kanta ta jinjina tana miƙa wuyanta tana kallon abincin, ɗan ɗaga kae AUNTY tayi ganin bata wuce ba sae taga tana kallon abincin
''kikayi tsaye ki wuce mana tunda an gama gaesawan'' kanta ta jinjina tana juyawa
''xo nan'' da sauri ta juya ɗin kuwa, pointing kujeran dake opposite ɗinta AUNTY tayi tana cewa
''xo xauna kiyi breakfast nasan bakiyi ba'' aekuwa kaman mae jira tayi saurin matsawa tana xama, da kanta ta xuba mata abincin ta tuttura mata gabanta ɗan ɗagowa tayi dan tun ɗaxu takejin idanuwa a kanta adawiyah ce taketa kallonta idanunta sun ɗan sauya color
''kici abincin mana'' kanta ta jinjina tana ɗaukan tosted bread ta kae bakinta, shiru sosae falon ya ɗauka sae ƙaran kwanuka, ɗaga idanunta tayi tana kallon AUNTYn yanda take cin abinci hankali kwance
she's kind hearted, but why did mamy hated her that much? sae jiya data nutsu ta fahimci dalilin da ya saka bata ƙaunarta amma batada matsala dasu Aliyah kenan saboda abunda mamy take mata ne ita kuma ta ɗauko kamanni da halayen mamyn shiyasa ta tsaneta and now that she carrying her grandchild ta ɗan sauko duk da yanda ake ƙoƙarin ɗorata shine dalilin yin fushinta da ɗanta amma da alama bayan xuwansa sunyi settling differences ɗin
''menene kuma?'' AUNTYn ta faɗa ganin yanda tun ɗaxu take kallonta, kanta ta girgixa tana maeda idanunta kan abincin gabanta da ko bread ɗin bata gama ci ba bare ta kama wani abun
Tana gamawa maemakon ta tafi sae ta koma kan cution tayi xamanta gashi bata ɗauko wayarta ba, maid ɗin AUNTY nata shige da fice wasu aiki wasu gulma duk tana ankare dasu ta share, tanata xaune a haka dan AUNTY ta shige wani bacci ya lallaɓo ya sureta
Ɗan shiru meenal tayi tana kallon yanda take baccin kaman wani falonsu little finger ɗinta ta saka a baki tana tunanin abinda xata mata, lokaci ɗaya idea taxi mata da sauri ta ɗaga gira tana juyawa ba jimawa kuma ta dawo hannunta riƙe da wani bucket cike da ruwa without any hesitation ta ɗaga bucket ɗin duka ta juye mata shi a jiki
Wani irin firgita tayi tana kwalla uban ƙara daya firgita part ɗin ae babu shiri duk waɗanda ke ciki suka firfito AUNTY dake can samanta tana dudduba kayan order da suka rage ɗan shiru tayi jin kaman ihu amma jin shiru bata ji an ƙara ba sae kawae ta shiga harkokinta itama
A falon kuwa dukansu shiru sukayi suna kallon juna, adawiyah na riƙe da

gaban rigarta da yafi jiƙewa idanunta sakk akan meenal dake riƙe da bucket ɗin data watsa mata ruwa har yanxu sukuma maid ɗin AUNTY sae ɓoye baki suke suna dariya ganin yanda tayi wani tsaeee tana kallon meenal
Toh nima dae nayi kasaƙe inaso naga abunda xae biyo baya kuma
Officialraah 444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 36
Typing.....✍
Ajiyar xuciya ta kuma saukewa tanayin murmushi ta girgixa kanta tana cewa
''meenal baki lura na riga nayi wanka bane? kokuwa kwalliyar tawace bata burgeki ba?''
''ke dalla can!! wae ke asu wa da xakice xakimin bari? toh bari kiji tun kafin in ci miki mutunci ki kama hanya ki koma inda kika fito cox u didn't belong here'' meenal ta faɗa tana nuna mata ƙofa, kanta ta jinjina tana juyawa xata wuce gaba ɗaya wanda ke tsaye wurin suka saka dariya except meenal da ta ɗora da faɗin
''ƙaramar mara kunya na ɗauka yau ɗin ma cewa xakiyi xaki faɗan mara ɗaɗi da kinga yanda xanyi dake'' ci gaba tayi da tafiya cikin ɗan hanxari tana dafe cikinta da ya fito sosae saboda matsetan da rigar tayi
Iyyah Nanny ɗin su meenal ɗin ce ta xagayo ta baya ta tari adawiyahn a ƙofa ta lulluɓa mata hijab a jikinta tana goge mata fuskarta, ɗan murmushi tayi tana janye jikinta taci gaba da tafiya, Allah ya taemaketa dan babu kowa a falon nasu bedroom ɗinta ta wuce cikin sauri
Wata princess gown ta saka milk mae kyau ta saka socks a ƙafanta da xundumemiyar himar har ƙasa sae loose cover a ƙafarta ta xari wayarta ta wuce, part ɗin AUNTYn ta koma meenal dake xaune tana breakfast suna haɗa ido ta wani irin shaƙe take kuwa ta fara tari tana kallon adawiyah dake mata murmushi tana ƙarasawa dinning ɗin
''wae dan Allah ke mene yake damunki ne wae? meye haka? wannan wace irin jaraba ce?''
''jaraba kaman ya? wannan part ɗin uwar mijina ne akwae wacce ta isa ta hanani xama ne? besides ɗanku ne yakeson nan ɗin so dole kullum mu rinƙa xuwa'' tana gama faɗar haka ta janye ta koma falon ta xauna, wani irin harara meenal ta bita dashi tana miƙewa ta bar dinning ɗin
''banxa kawae, xakici u*ki ne'' ta faɗa tana bin meenal ɗin da harara ta gyara xamanta tana buɗe data

Babu wacce ta ƙara fitowa har akayi azahar, itama duk sae taji kaman ta karaya kaman baxata iya yin abunda tayi niyyan yi ba jin kamar motsi ya sata ɗaga kanta tsaff kuwa idanunta suka faɗa kan AUNTY dake kallonta daga sama, gyara xamanta tayi tana sauke ƙafafunta ƙasa
''kinanan ne tun ɗaxu?'' cewar AUNTY bayan ta ƙaraso inda taken, kanta ta jinjina mata tana fidgetting fingers ɗinta
''me kika xauna yi tun ɗaxu ne? bakisan har an tafi gidan su khaulat bane ko ke baxaki ba?''
''ba komae'' shiru AUNTYn tayi for some minutes sae kuma ta juya tana yin sama
''idan yanayin falon yana miki daɗi ki tattaro kayanki ki dawo nan ɗin mana'' tana gama faɗa ta shige ciki
''kiji hajiyarnan ma, aekuwa ba inda xan tafi'' ta faɗa tana shigewa kitchen
Duk kallonta cooks ɗin dake haɗa abinci sukayi itama ta kallesu tana buɗe exit door ɗin tayi garden, pipe dakenan ƙasa ta dauka ta fara alwala tana gamawa ta koma ciki ta bayan kujerun ta kabbara sallah, tana cikin yi autan mommah ya shigo hannunsa riƙe da ledojin kasuwa ɗan tsayawa yayi yana kallon bayanta dan ta bawa ƙofar baya
''kae kuma tsayuwar me kake ne?'' har sae da ya ɗan xabura da sauri ya kalli AUNTY dake kallonsa, da sauri yayi gunta yana ƙasa-ƙasa da murya yace
''AUNTY me takeyi anan?'' wani irin kallo AUNTYn ta masa tana jan kunnansa tace
''dan gidanku ina ruwanka xamanta takeyi ne?'' sosa kansa yayi yana tura bakinsa gaba
''sannunka da dawowa koh'' adawiyah ta faɗa bayan ta sallame, ɗan shiru yayi sae da AUNTY ta gyaɗa masa kanta sannan ya amsa yana wucewa kitchen
''menene ka kawo?''
''sukumbiya ne inji baba ado'' ya faɗa yana karasa shigewa
''meyasa bakixo ɗaki kinyi sallah ba?''
''ba komae AUNTY'' baki ta taɓe tana wucewa cikin kitchen ɗin itama
''ya llahi, wallahi na gaji'' ta faɗa tanayin flat a ƙasa
Wurin 7:40pm xa'ayi kamu gashi kuma har ga Allah bataso taje, gashi AUNTY data sauko tace ta shiryo itama kuma tun safe da take nan part ɗinsu bataga wulgawarsa ba dukda sunyi waya har sau biyu kuma ya tabbatar mata da baya gidan amma batayi tunanin xae wuni a inda yaje ba gashi bama taso yasan tana part ɗin wayarta ta kall ta ɗan ja tsaki tana dialing no sa
''nidae ba ruwana babu inda xanje ina fama da babyna'' ta faɗa tana ajiye wayar saboda kiran da yayi reject tasan yanxu xae kira
''ya khaleeeel'' ta faɗa tana jan sunan sosae bayan ta ɗaga
''na'am ya adawiyahhh'' shima yayi yanda tayi dagacan, wata irin dariya ta ƙyalƙyale da ita tana cewa
''kae ya khaleel dan Allah''
''kae ya adawiyah dan Allah''

''huum ya khaleel lamarinka ya girmama ni baxan biye makaba, yanxu dae ya aikin?''
''wooah aeki da godiya ba wuya ba daɗi''
''hakafa, amm nace sae yaushe xaka dawo gida kuma?''
''ehh toh inaga before 9 na dawo''
''toh my Allah maedoka lfy, dama wae haj....em AUNTY ce tace na shirya aje kamu dani nikuma'' sae tayi shiru, dariya ya ɗan yi dagacan yana cewa
''kekuma bakyaso kije?''
''toh masoyi kasan yanayin nawa fa''
''ehh kwarae kuwa na sani yanxu ya kikeso ayi?''
''yauwa mijina sarkin masu ganewa na duniya, pls so nake ka faɗawa AUNTY abunda xae saka ta barni a gida wlh banason xuwannan''
''an gama your royal highness'' murmushu mae kyau ta saki tana ajiye wayar su su kaɗae sukasha hidimarsu dan ita baccine ma ya ɗauketa a kujeran AUNTY bayan sun wuce, sanda ya dawo gidan shiru duk an tafi dole falonsu xae wuce direct, yana xuwa kuwa yayi kyakyawan gani ɗan murmushi yayi yana kallon fuskarta data tasa saboda tsufan cikin sae kuma ya kalli ƙafafunta data duƙunƙune a hijab, to 10 yasan suna hanyan dawowa
Bismillah yayi ya ciciɓeta yayi ɗakinsa dan ba xae iya fita da ita a hannu ba saboda masu aiki da yaransa dakenan akwae nauyi abun amma idan yaje da ita ɗakinsa ya samu baccin ya tafi sae ya lallaɓata taje part ɗinsu, ruwa ya shiga ya watsa yaxo yayi shirin bacci sannan ya xauna a gefen gadon ya kama babbar yatsarta ta ƙafa ya ja sau biyu ya saki ya kama ɗayar a haka har ya gama da left ya kama right
Ɗan motsawa tayi tana janye ƙafar at the same time tana tura bakinta gaba tana magana can ƙasa
''yoh wayace ka tashen daga bacci wae?'' ɗan shiru yayi yana kallonta sae ta buɗe ido da ƙyar tana kallonsa itama
''me yasa kika tashi?''
''massage ɗin da kakemin ne ya tasheni''
''toh taya kikasan nine?''
''saboda kaene kaɗae kakemin irin haka''
''toh yayi kyau tunda kin tashi muje in rakaki gidanku sae kiyi baccin acan, nasan mamy will be worried idan tadawo bata ganki ba''
''wanne gidan kuma bayan wannan?'' ta faɗa tana tashi xaune da kyau
''part ɗinku nake nufi fa''
''aaa'a ni banda wani part daya wuce wannan dan haka ba inda xani''
Officialraah 444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)

Story and writing by
Officialraah444

Page 37
Typing.....✍
Yana kwance ya saka tafin hannunsa ya tokare gefen kansa yana kallon yanda taketa bacci fuskarnan tayi sharr kaman ta jinjira' sosae baccinta yayi increasing those days abinda ya kamata ya faru tun cikin na farko though dae tayi baccin kam ba laefi, miƙewa yayi dan baeyi wankaba ita kaɗae tayi ta kwanta
''na xama kifi nima'' ya faɗa yana shigewa toilet
Tun da safe sukaji knocking kusan duk yan part ɗin ma basu tashi ba amma yanda ake knocking ɗin kaman xa'a ɓalla ƙofar yasa ba iya sama kawae ba har ɗakinsa dayake daga can baya ana jiyowa, a lokacin suna kwance sunata bacci knocking ɗin ya iso har cikin dodon kunnansa, cikin nutsuwa as usual ya buɗe idonsa yana kasa kunne dan jin ƙaran meye yaka xuwa sae kuma ya miƙe cikin ɗan sauri ya lulluɓeta da blanket dan ƙaran ya ɗan ragu da sauri ya fita
Yana saukowa yaga duk su AUNTY sunyi cirko-cirko sae Nanny dataje buɗewa sae kawae ya tsaya bae ida saukowa ba, to their great surprise mamy ce ɗankwali a gaba tana ta tashin ƙamshi, sae da taxo daedae tsakiyar falon sannan tayi wata tsayuwa ƙafa ɗaya a gaba ɗaya a baya ta harɗe hannayenta a ƙirji from head to toe take kallon su AUNTY
''ina yata?'' ta faɗa tana sauke hannayenta, ɗan girgixa kae AUNTY tayi tana juyawa dan komawa ciki
''ke rabi baki isa ina magana kijuya kice xaki barni ba!!! nace ina yata?''
''hajiya naana yarki batanan'' AUNTY ta faɗa tana juyawa dan shigewa
''ke rabi karkice xakimin wani duniyanci anan halama an faɗa miki na mantaki ne? toh wlh tun muna shaeda juna dani da ke gwara kije ki fitomin da yata tun kaf.....''
''Mamyyy!!!!'' ta faɗa da ɗan ƙarfi har tana duƙawa, tana daga case na farko a tsaye, shiru mamyn tayi tana kallonta ganin babu abunda ya sameta da alama ma bacci ta tashi
''au da gaske kinanan ɗin kenan? toh xonan mu wuce''
''mamy meye haka ne wae? nifa lfy nake kuma nan ɗin ma ae gidane bae kamata kixo kiyi abunnan ba''
''me kike nufi?''
''mamy dan Allah ki tafi don't cause any trouble this morning'' ɗan kasaƙe mamyn tayi
Duk da ba yau ne karon farko da yar ta fara bata umarni ba amma hakanan taji xafin wannan saboda a gaban maƙiyanta ne, wata irin xuciya ce ta tunxurota batasan sanda ta tafi saman ba, KONTO dake tsaye ne ya kauce ya bata hanyar dan ta samu isa ga yarta da kyau
Da iya ƙarfinta ta janyo yar ta fara saukowa da ita take abun ya tsama kamar

faɗa ita tana janta ita kuma tana ƙoƙarin ƙwacewa ga ciki dake jikinta ganin haka yasa da sauri AUNTY tayi shahada tayo gun sae kuma ta tsaya saboda hannu da khaleel ɗin ya ɗaga mata alaman kar ta ƙarasa, wani irin kallo ta masa sae ya jinjina mata kansa kafin ma tayi wani motsi ƙaran adawiyah ya karaɗe falon
Wani irin gangara take kaman an sako fura daga bene tun daga na ukun da mamy ta janyota har xuwa na 8 wani irin xabura dukansu sukayi dan basuma san ta yanda abun ya faruba, yana isa da hannayenta ya chaɓeta yana ajiye dukkan guiwoyinsa ƙasa da ƙarfi, kallon fuskanta yake yayinda sauran yar part ɗin suka hau kuka wasu kuma sukayi waje
Shiru yayi yana kallon fuskanta da duk jini ya ɓata gefe da gefen fuskar wanda take fitowa daga gefen hijab ɗin jikinta da alama kanta ne ya fashe sae kuma gefen bakinta shima jinin yake, kasa koda motsawa yayi har aka shigo aka ɗauketa aka saka a ambulance idonsa da guiwoyinsa ba ajiye gu ɗaya, ɗan xabura yayi yana miƙewa da sauri shima ya fitan
Ya musty dake tsaye ne yaga fitowarsa da sauri ya ƙarasa gabansa yana kama hannayensa ganin yanda take wata irin tafiya, pakistan ɗin jikinsa brown sunyi stain ɗin jini ta ko ina ga hannayesa suka da suke rawa duk jinin a jiki kallo ɗaya xa'a masa a gane baya hayyacinsa abunda kawae ya kiyaye xaucewarsa shine ƙarfin imani da kuma nutsuwa da yake da ita, ganin yanda yake tafiya ya sakashi kallon guiwoyinsa da sauri ya ƙara kamasa yana cewa
''ya khaleel muje na kaeka asibitin kaema, u injured''
Ganin kamar ma baya jinsa ya sakashi fara jansa da sauri ya mubarak da isowarsa kenan yaje ya kama masa dan ganin kaman ya masa nauyi (ya Mustapha babban ɗan Abby ne ya mubarak ke binsa kuma shi yanada gida a Abuja so ko sunxo acan matarsa da yaransa suke xama) har car duka sakasa ya rufe ya xagaya da sauri yana yafito ya ruƙayya
''kada a faɗawa Abby wannan abun ku bari idan bayan ɗaurin aure komae ya tafi daedae ya musty da kansa xae faɗa masa, am i clear?'' da sauri ta jinjina masa kanta
Mammah dakenan sama tana kallon duk abunda ke faruwa ce ta lumshe ido tana komawa falonta ta ɗora ƙafa ɗaya ƙan ɗaya tana jiran shigowan ya ruƙayya, aekuwa sae gatan kuwa ta shigo, da sauri mammah ta miƙe tana kama hannun ruƙayyan cikin son jin komae tace
''tell me in full i don't want detailed info'' kanta ta jinjina mata tana kora mata bayanin komae, murmushi tayi bayan gama ji tana sakin ruƙayyan ta fara xagaye falon tana dukan tafin hannunta
''so that means akwae wacce xa'a saki a gidannan yau kenan''
''amma mommah ya mubee yace kar a sake maganar taje gun Abby''
''kema kina ganin kar a sake ɗin? Ruƙayya idan fa kika lura da hankalinki xakigane wannan kyakkyawan opportunity ne yaxo mana na ganin mun mallaki Alhaji da gidannan dama babban shamakin ae su biyun ne idan kuma akayi sa'a ya koresu duka kinga gidan ya xama namu ae tunda ita dae waccan shashashar bama tashi take ba''

''amma mommah bafa mutuwa antyn tayiba, ba'a ma san taƙamaeman abunda ya sameta b..''
''amma ae xa'a sani? Kuma bari na tuna miki abunda kika manta: Najeeb shine wanda xae dubata idan kuma abun yafi ƙarfinsa wani ne xae dubata, me kike tunani idan ni ɗinnan na haɗa baki da mae dubatan?'' ta faɗa tana ɗagawa rukky gira
What's mommah up to now?
Officialraah 444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 38
Typing.....✍
Shiry Abby yayi yana kallon mommah da tayi laushi saboda kukan da ta sha, so yake yayi gathering courage ya miƙe amma ya kasa a xaunen da yake ma jiri jiri yakeji gashi wani abu ya tokare maƙogaronsa bakinsa kaman an ɗora dutse ko magana baya tunanin xae iya yi
''Alhaji kayi shiru bakace komae ba'' tafaɗa dan ta fara jin tsoron shirun nasa kuma, hannu ya miƙa ya ɗauki sauran ruwan dake kan center wanda tun jiya da dare yayi amfani da shi da sauri ya ƀalle murfin ya kafa baki
Ta buɗe baki xatayi magana da hannu ya mata alama ta fice, bata kuma magana ba ta miƙe da sauri ya bita da wani irin kallo yana kwantar da kansa bayan kujera almost two minutes sae kuma ya tashi a xabure yana shigewa ciki ba jimawa ya fito sanye da shadda blue da hula a hannu sae car key ya fice cikin sauri
Shiru yayi yana driving ɗin, saeda ya fatattaki yayansa dakenan da guards ɗinsa sannan duka barsa ya fito sun dage dole sae dae a tuƙasa alhalin su basusan yanda yake ji ba, GPS kawae yayi connecting direct har ward ɗin da suke yayi parking da sauri ya fice
Tunda sukaxo akayi emergency da ita after treatment dr ɗin yace dole xasu mata operation su ciro abunda ke cikin saboda high expectation na wani abu kan iya faruwa da abun, Adeel ne yayi signing saboda KONTO an riga an masa alluran bacci bayan an masa dressing, duk da ma overdose suka masa saboda ƙin kamasa da na farkon sukayi,
An shiga da ita theater room ba jimawa Abby ya shigo, wani irin miƙewa duk sukayi a tsorace barin ma mamy da taji kaman fitsari xae xubo mata saboda tsoron daya kamata ganin Abby ko kallon inda take baeyiba ya samu wuri ya xauna kawae

Wani irin shiru ne ya ratsa wurin a haka har green light yayi appearing, da sauri duk suka miƙe sae ga dr. ya fito
''Congratulations we've successfully brough out the babies they're duplex boy and girl but.....the girl have passed'' ganin yanda duk suka shiga shock yasa dr. ɗin kaɗa kae yace
''its because of the way the mother fall, she fall under the baby's head so kan nata ya tsage saboda buguwar da yayi sakamakon harbin ƙarshe na lokacin da numfashinta xae fita datayi wa uwar a cikine ya sakata suma but thankfully the boy is fine buutt''
''u need to insert him under care''
''yes sir''
Kafin su kuma magana aka fito da ita da sauri humee ta matsa tana dafa gadon cikin kuka take kallon yayar tata that looked fale kaman wacce tayi wata a kwance, suma duk matsowa sukayi ganin haka kawae nurses ɗin suka turata dan a kaeta ta huta
Two hours after ya farka, a hankali yake buɗe idanuwansa bayan brain ɗinsa ta gama dawo da duk abunda ya faru filla filla so that means yana hospital? ina matarsa? meya sameta? miƙewa yayi da ɗan sauran ƙarfin daya rage masa jin guiwansa kaman a ɗaure ya sakashi kallon wurin sae ma a lokacin ya lura da short ne a jikinsa kuma ba xae iya fita dashi ba
Toilet yaje aekuwa ya tadda wandon har ma an wanke amma bae idasa bushewa ba, janyowa yayi ya saka ya ɗauraye fuskarsa ya fito
''yaya ka tashi'' cewar na'eem yana ƙoƙarin kamasa, hannu ya ɗaga masa yana ɗan waege-waege
''kanaso kaga matarka ne? muje xan kaeka'' sae a lokacin ya yarda ya kamasa suka tafi har gaban mota, ganin ya kallesa yasa shi kaɗa kae yana cewa
''ward ɗin da ɗan nisa baxaka iya a ƙafa ba''
''sanda suka shiga yana ward ɗin duk yan gidan nanan kan wasu kujeru dakenan ƙofan ɗakin duk idanu suka xubo masu AUNTY kuwa da yan ɗakinta kansa sukayi da sauri suna dubasa
''ina take?'' ya faɗa a ɗan dake, shiru gaba ɗaya wurin sukayi sae AUNTY ce tayi gathering courage tace masa
Tana ciki kanaso ka ganta ne?'' shiru yayi yana kallonta irin kallonnan na 'what do u mean?' ɗan ɗauke kanta tayi saboda fahimtar sigar kallon da tayi tana cewa
''dr. ya bada umarnin kar a shiga amma kae baxa'a hanaka shigaba so kaje ka gantan'' ɗan janyewa yayi yana ɗangisawa daedae mamy data sadda kanta ya tsaya ba tare da ya ɗaga kansaba amma cike da girmamawa yace
''barkanku'' daga haka ya shige ɗakin
Daga ƙofa ya tsaya yana kallonta yanda take kwance akan gadon an ɗan ɗaga gadon tayo sama so ana ganin fukarta clearlly jikinta sanye da maternity gown har lokacin, a hankali ya ƙarasa inda take idanunsa still on her face
''are u alright?'' ya faɗa yana shafa fuskanta

''dan Allah kiji sauƙi wife, kiji sauƙi I can't recover as soon as you're in this state so pls recover as soon as u can, for me and our baby'' saddawa yayi yayi kissing forehead ɗinta ya juya ya fice
Yana fitowa ya Usman na ƙarasowa wurin direct kuma gun KONTO ɗin yayi yana cewa
''ya jikin yaya Ibrahim ya kuma mae jiki?'' kae KONTO ɗin ya kaɗa masa xae wuce Usman ɗin yace
''da ka ɗan daure munje kaga boy ɗin da aka ciro ɗin shima sae ka huta gaba ɗaya'' chakk ya tsaya yana ƙoƙarin fahimtar inda maganar ta dosa
''ehh khaleel matarka an ciro abunda ke cikinta ɗaxu they're twins amma macen ta koma sakamakon tsagewa da kanta yayi sanadin jefar da uwarta da akayi, sae namijin da aka saka cikin kwalba'' cewar mammah, saurin xaunawa yayi dan jin kaman kansa ya sara yana ganin jira, duk kansa yan ɗakinsu sukayo harma da su Adeel AUNTY kuwa wani irin kallo tayiwa mammah a fusace tace
''kinga idan fa ba abunda xae kwantar mana da hankali xaki rinƙa yi a gunnan ba toh gwara kije ki kula da gida'' sae kukaji mammah anyi tsitttt
Officialraah 444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 39
Typing.....✍
''AUNTY what did she.'' sae yayi shiru yana kallonta, matsawa tayi ta kama kansa ta jingina da cikinta tana rungume kansa
''kayi haƙuri Ibrahim yarka ta koma sae namijin shima kuma sae an bisa da addu'a'' jin yayi shiru yaƙi magana sae ta sakesa tana ɗago kansa, murmushi mae kyau ya sakar mata yana shafa hannunta yace
''ummmana ina lfy kema ki kasance lfy pls, besides nida bama sanin babyn nayiba bare inyita jin ba daɗi sannan ae ɗan uwanta nanan kuma insha Allah xae samu sauƙi sannan ae ba'asan rabon da xae xo nan gaba ba koh?''
''khaleelll'' ta faɗa tana sakin kuka tareda ƙara rungumesa
Kallon yaron dake kwance a cikin cress kuma abun mamaki da ɗan girmansa dan babu wacce xatace bakwaeni ne bare kuma ace wae su biyu suka kwanta a wannan ɗan cikin da kaman anci abinci da yawa ya tashi, wayarsa da tun da yake a duniya mutum ɗaya ta taɓa buɗe cameranta ya ɗauko ya fara masa hoto yanda yakenan kaman ba rae a jikinsa
''i love u Abbyn wife, i love u so much Abakar, pls get well soon u not for me

but for your mother she only has us, we'll have to fight for her, kaji sauƙi kayi ƙarfi kaji don't give love another headache, u'r sis Aminatu takwaran mamy has left...., pls will u stay? for maa and pa?'' ya ƙarasa hawaye na sauko masa
Da kyar mamy ta iya ƙarasawa bayan baby care ɗin da samu wani bango ta jingina, ahankali tsayuwar ta gagareta dole sae silalewa tayi ta duƙa a wurin tana sakin kuka itama, tunda take abubuwanta shekara fin talatin bata taɓa jin nadama daedae da minti ɗaya ba sae yau data kashe rae kuma of all people ma ran jikarta yar yarta ita kuwa wannan wace irin ƙaddara ce ta sameta
''why me? why? whyyyyy? ya Allah am a siner ya Allah i committed a big crime da wanne ido xan kalli yata? da wanne ido xan kalli mijina? da wanne ido xan kalli s....s...sir....s'' sae kuma tayi shiru tana rufe idonta da tafi hannunta
A hankali idanunta suka fara buɗewa tun tana gani dishi-dishi har suka ware tarrr akan POP, shiru tayi tana tunano abunda ya faru har xuwa faɗuwarta, a hankali bakinta ya motsa tana furta 'mamy', sae kuma tayi saurin dafa cikinta tunawa da abunda taji kafin ta suma ae batasan sanda ta tashi xaune da sauri ba sae kuma ta dafe cikin tana sakin ihu kaɗan
Xabura KONTO yayi saboda abunda yaji a jikinsa ganin duk sun kallosa sae ya miƙe yana murmushi yace
''bara na ɗan dubata'' kae duk suka jinjina masa
Yana tura ƙofar tana juyowa baesan sanda wani kyakkyawan murmushi yayi appearing a fuskarsa ba yana takawa xuwa gunta, itama kallon nasa take barin ma fuskarsa ganin yanda yayi xuruu jikinsa sanye da yadi ash
''kin tashi? y jikin'' ya faɗa yana shafa kanta, hannunsa dake kan ta kama tana cewa
''ehh na tashi amma?'' murmushi yayi dan ya fahimci shirun nata sae ya kae hannunsa kan hannunta data dafe inda aka mata theather yace
''yaronki yana cikin lafiyansa amma an sakasa a cress saboda stillborn ne'' wani kyakkyawan smile ya suɓuce mata tana cewa
''wae boy na haefa?''
''boy kika haefa ko boy muka haefa?'' hannayenta dake ɗan rawa ta saka ta kamo fuskarsa tayi kissing nasa for some seconds sannan ta rungumesa
''ina sonka, ina tsananin sonka, ina sonku kae da babynmu baxan taɓa iya rayuwa babu ku ba''
''nima haka ina sonki, ina ƙaunar ki, ina tsantsar ƙaunarku keda ɗan mu, baxan taɓa iya jure rashinku ba, dan Allah kuji s..s...'' kuka ya saki a hankali, hakan yasata ɗan dukan bayansa tana cewa
''toh kukan kuma na meye bani da babyn muna raye ba, babu fa wanda ya mutu aaa'ah'' shima shafa bayanta ya shiga yi yanajin tausayinta na kamasa dan yasan dole sae taji ba daɗi idan har ta samu gaskiyar lamarin
''toh ya isa haka, ya isa'' ta faɗa still mingling on his shoulder
Knocking ɗin da akayi yasashi xare jikinsa ya gyara mata pillow yaje ya buɗe, mamy ce tsaye fuskanta a ɗan jiƙe da alama ruwa ta saka ƙin bari su haɗa

ido tayi shima dama ba wae iya haɗa idon da ita xaeyi ba sae kawae ya buɗe mata sosae yanda xata wuce, tana shigewa ya fito ya ja masu ƙofar
Shiru ɗakin yayi ita tana kallon bangon gabanta ita kuma mamyn tana kallon floor almost a minute sannan ta iya motsa bakinta da ƙyar batare da ta ɗago ta kalleta ba tace
''yaya jikin naki?'' shiru tayi taƙi magana
''dama xan dubaki ne nakuma baki haƙuri''
''haƙurinki ba xae ƙareni da komae ba hakama rashin badashi so pls'' ta faɗa tana pointing ƙofa
''nasani nasan nayi kuskure nasan ban kyauta ba gashi na kashe jikata da hannun.....''
''ban gane ba'' ta faɗa tana ƙoƙarin tashi dan ita tunanin ta boy ɗin ya bata
''ki faɗamin wanne jikan?''
''yar biyun ɗanki''
''yar biyu?'' ta faɗa maganarta har wani sauri ta ƙara
''ehh Rabi'ah yan biyu aka ciromiki amma macen ta koma sa.....sakak....saboda.....turakin da nayi kanta ya fashe ta mutu ehmm'' ta ida maganar cikin kuka sosae
Koƙarin xama take a gadon amma wani irin duhu ya mamaye mata ido ya hanata ganin gadon ma, ga wani irin duum da ears ɗinta sukayi sae lalube take ta gaxa samun gadon
Daga waje kuwa kukan mamy ne ya isa har wurin duk tagumi sukayi abun duniya ya taru ya masu yawa jin tana kiran sunan adawiyah tana kuka yasa ba shiru suka runkuta ɗakin koda suka isa tuni ma ta suma dole dr. aka kira
Dole duk gida suka tafi bayan magrib dan baxata samu sallama a ranar ba saboda jininta daya hau, da yake hospital ɗin ba'a barin yan kwana dukansu suka wuce gida sae kuma gobe, abun mamaki kusan fin rabin yan gidan sae suka kasa rintsawa AUNTY da abun ya gagari tunanin ta tashi tayi ta ɗauro alwala ta kabbara Sallah tana cikin yi meenal da tunda ta kwanta take munanan mafarkae akan sakamakon da xasu samu a lahira na irin xaman da sukayi a gidan ta shigo ɗakin AUNTYN, ganinta akan sallaya sae itama taje ta ɗauro tata taxo ta kabbara
Faka-faka pls
Officialraah 444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Typing.....✍
A part ɗin mamy kuwa tana ta xaune a falonta tunda suka dawo ta kasa tashi ta shiga ciki, yanxu haka waya suka gama da Aliyah dake can greece tanata kuka wanda shi ya ƙara tayarwa mamy hankali ga kuma Usman da khaleed da suka gama nasu faɗan sukayi ciki daga ita sae adeel daya lallasheta shima yayi sama muh'd kuwa ko alamar number sa batagani ba a wayarta duk da taji yayi waya da Abby da yan uwansa amma ba alamar xae kirata
''ya Allah ubangijina ka yafemin'' ta faɗa tana rufe ido
Abby ma a nashi part ɗin sallahr yake idanunsa na xubar da hawaye na neman yafiyar Ubangiji saboda yasan ƙaddara da rabon yaransa ne ya sakashi komawa mamy bayan shekaru har akayi abunda akayi, miƙewa yayi yaje ya buɗe press ya ɗauko wani duvet ya fita KONTO na xaune daga ƙasa jikin kujera ya ɗan sadda kansa da alama bacci ne ya ɗaukesa batare da ya shirya ba, ajiyar xuciya Abby yayi yana
Da asubahi suna masallacin gidan duk a xaune dan dama ƙa'ida ne sae sun xauna, wayar KONTO dake gefensa ta fara haske, shiru yayi ganin daga hospital ake kira sae da ya ida addu'ar dake bakinsa xuwan lokacin har kira na biyu ya shigo, ɗauka yayi yana fita daga mosque ɗin
Shiru yayi har aka gama masa bayanin da xa'a masan, a hankali ya xare wayan yana tin cikin gida da hanxari ya shiryo cikin shadda blue sae tashin ƙamshi yake idan aka gansa daga baya xa'ayi tunanin komae lafiya saboda yanda yake fess amma da an kalli fuskansa huuum
Baƙin da sukayi saura wanda sukenan yake ɗan haɗuwa dasu sama-sama yake gaeshesu yana wucewa har ya isa gaban motarsa sae kuma ya tsaya yana jan ƙaramin tsaki tunowa da yayi ya bar keys ɗin, kallon hannun da ke miƙo masa key yayi har xuwa fuskar mae shi
''kayi sauri yaya kaje ka duba jikin matarka xakaji sauƙi dan nasan jiya ko rintsawa baka samu kayiba'' cewar meenal dake miƙa masa key ɗin, da sauri ya kaɗa mata kae yana amsa ya shige da sauri
Sosae yayi gudun da bae taɓa yi ba dan sosae da nisa tsakanin gidan da hospital, har bakin ward ɗin da take yaje sannan yayi parking gudu-gudu sauri-sauri ya shiga ɗakin sae kuma ya tsaya, tana sadde akan gadon ba'a ganin fuskarta da kyau amma kuma sobbing ɗinta har ƙofar ana jinsa, shiru yayi na ɗan lokaci sannan da kyar ya iya furta
''Moonad ɗinaa'' a hankali ta ɗago kanta ta xuba masa idanunta da sukayi ja sosae
''ya khaleel'' ta faɗa tana ƙoƙarin cire carnula ɗin hannunta, da sauri ya ƙarasa yana kama hannayen nata sae kawae ta faɗa jikinsa tana sakin kukan sosae
''ya khaleel.....h..h...hh...wae....jh..w..we...a''
''shiiiii, shiii, ya isa haka yi shiru ya isa'' ya faɗa muryansa na ɗan rawa jin taƙi yin shirun sae ya maedata kan gadon ya xaunar yana ɗauke ƙafafunta ya xauna sae ya ɗorasu kan laps ɗinsa yana jijjiga shoulder ɗinta
''toh wae kukan na mene tun ɗaxu? ba gani naxo ba''

''hhh....ya khaleel w...we....wae..da gaske mamy....uhm ta''
''kinaji yi shiru ki saurareni, mamy mahaifiyarki ce wacce ta haefeki koh? kuma kinsan tanada iko akan duk wani abu dake mallakinki koh? toh inaso ki nutsu kiyi magana da xuciyarki shin mamy xata iya ɗaukan ran ɗan Adam?'' shiru tayi tana kallonsa
''kin rasa amsa right, toh kaman yanda kika rasa amsa haka nakeso wannan ma ki rasashi a cikin kwalwanki ki manta da wannan labarin da inda kika jisa, ki saka a ranki ɗa ɗaya kika haefa ba twins ba, sannan wannan umarni ne'' da sauri ta buɗe baki ganin irin kallon daya mata sae ta rufe
''banaso ki bari kowa yaji abunda ya faru tsakaninki da mamy, ko kin manta wanne irin gida kukeda shi? kinaso ki miƙa nama hannun kura ne? idan kika nuna ßacin ranki akan abunda ya faru that means kin bawa maƙiya dama akan mamynki, ki tuna fa kece kaɗae sanyin idaniyarta tana ƙaunarki fiye da kanta kuma a gaban kowa take nunawa so pls banaso ki saka wannan abun a ranki tunda abune Allah ya tsara dama can ba rayayya bace kawae dae wannan ne sanadi, kuma fa ita kanta mamyn bakiga yanda duk tayiba, so dan Allah karki sakama kanki damuwa kinji'' hannunta dake ɗan rawa ta saka ta kamo wuyanta tana kwantawa a ƙirjinsan
Tun washegari bayan barin KONTO gida AUNTY da kanta ta ɗebo yayanta sukaje part ɗin mamy lokacin tana xaune yayanta sun gama lallaßata kenan tanacin abinci, da farko har taji hankalinta ya tashi saboda har ga Allah wani irin tsoron mutane taji ya kamata barin ma KONTO, AUNTY da Abby da har yau bae ce da ita ƙala ba, xama AUNTY tayi sosae aka tada abunda ya wuce suka kuma baewa juna haƙuri da neman yafiya, sosae dasu da yaran sukasha kuka da dare ma suka ɗora a part ɗin Abby gaban kowa na gidan wanda har waɗanda abun bae shafaba saeda suka xubar da hawaye shi kanshi Abby kasa haƙuri yayi sae da yayi kuka, anan itama mammah ta tonawa kanta asiri na hoton adawiyah da tasa aka ɗauka ita da KONTO, sosae dae abu yayi xafi kafin duk suka sauko aka ƙara bawa juna haƙuri da dare kuma aka kae humee gidanta, mamy da taxo duba adawiyah jikinta duk a sanyaye amma abun mamaki sae yar take ta mata surutu kaman komae bae faruba da tana dae taƙi magana akan abun sae ita ta ɗauko maganar kae tsaye kuwa ta faɗa mata yanda sukayi da KONTO kuma har cikin ranta ta yafewa mahaifitar tata, sosae mamy tayi kukan da ta jima batayiba sannan a gaban kowa da dare bayan sun dawo ta rungume KONTO tana saka masa albarkha, daganan kuma suka fara tarewa a hospital tunda an maeda sunan boy ɗin sae bayan yayi lafiya yan London ma sae satin suna xasu iso.

****

A week later

Ba laefi ta samu sauƙi dan tana komae lfy lau kawae dae sunƙi discharging natane saboda yaron dake cikin container har lokacin thought ma dae jikinsa ya fara tattaruwa alaman sooner xae yi ƙwari, suna xaune akan gadon AUNTY na yanke mata farce mamy kuma na dama mata fura ita da meenal kuma na duba abu a waya, turo ƙofar akayi duk suka kalli wurin khaulat ce ta

a gaba sae mum da masu aikinta su biyu sae khaleed ɗin daga ƙarshe, ɗan duƙawa tayi ta gaeshe da su mamy tana yin wurin ƙawarta
''amarya bakya eeeeh'' adawiyah ta faɗa tana bata hannu
''huuum kedae kika sani mara kirki kawae''
''mara kirki kuma? rashin kirkin me nayi?''
''kin fini sani ae, ko alamar idonki babu a bikina sannan kixo ki haehu sae da akayi kwana biyarrr sannan xa'a faɗamin kuma a hakan ma ba kene kika faɗan ba''
''haba ta kusa da xuciya kemafa kinsan dalilin bikinki ne kawae naxonan kuma sae jikin duk ba daɗi ranar ɗaurin aurenki da naci alwashin xuwa koda banji sauƙi ba kuma sae wannan abun ya faru''
''baxan taɓa yarda dake ba'' ta faɗa tana tashi dan raka Khaleed
Sunanan har yamma da yan gidan xasu tafi da yake haka suke da 6:00pm tayi suke wucewa shikuma mijinta yaxo xuwa 9:00pm ya koma, ɗaukan wayarta tayi tana ɗan duba chats tanayi tana murmushi dan group ne suka buɗe na yan gidansu anata shan chapter, ɗan rungume wayar tayi tana kallon sama
Nima dae saman na kalla dan wlh na gaji, but kunsan me chapternan is super hit koh?
Officialraah 444

CHARBIN KWAE??
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 41
Typing.....✍

''why i didn't experience this happiness before? ashe ba rayuwa nayiba a baya duk shirme ne a yanxu ne na fara rayuwa'' wani irin dariya ta sake tana bubbuga ƙafafunta a gadon
''oh myyy inajina kaman tsakakkiyar tsuntsawa kuma duk sanadinka ne'' ta faɗa tana pointing ƙofa da iya ƙarfinta sae idanunta suka faɗa cikin nasa
''ohm..ohh...o..'' kasa magana tayi sae kawae ta ɓoye hannun a baya tana kallon gefe
''gulmana akeyi da alama'' ya faɗa yana xama akan plastic chair dake gaban gadon
''ina wuni'' ta faɗa tana yaƙe duka teeths ɗinta, hannu ya saka ya haɗe lips ɗin yana janyo bakin da sauri ta biyoshi
''ban wuni ba tunda ban ganki ba'' ya faɗa yana sakin bakin ya rungumeta

yana kae bakinsa bayan kunnanta ya sakin mata kiss a gun wanda ya sakata shivering, earlobe ɗin ya ɗan cixa yana sakinta
''ya Ibrahim kasan banida lfy koh?'' ta faɗa tana riƙe ƙugu, hannunsa yasa yasha shafa saman chest ɗinta ido ta xaro tana ture masa hannu
''kagaa'' kaman jira yake tace kaga ya miƙe yayi kanta
''ya khaleel a'a, Allah ka bari'' bae kulata ba saeda ya gama abunda yaga damar mata sannan ya rungumeta a hankali yace
''kina sallah ae kuma kinji saurƙi''
''amma ae nan ba gida ba''
''toh dole sae a gida xa'ayi ne?''
''nan ae hospital ne''
''uhum ae akwae gado akwae blanket sannan kuma akwae ki'' ya faɗa cikin waya yana maeda kansa ƙirjinta ya jujjuyashi ae batasan sanda ta fara dariya ba tana ture masa kae
''ya Mu'azzam wayyoo'' ta faɗa tana tsunkulin bare neck ɗinsa
''wayyo yaya anty xafii'' ya faɗa yana maeda ita samansa ya gyara mata zip ɗinta yana kallon idanunta yace
''xan ƙyaleki na yau, saboda idan nace xanyi toh ɗakinnan duka ya mana kaɗan sae dae a bamu fili a hospital compound dan kinsan yanda akeyin mortaling haka xan miki saboda yarinyarnan kinci bashi da yawa fa'' bakinsa taketa kallo har ya gama sae ta ɗora masa ɗan light kiss tana yin dariya tace
''kae ɗinnan fa bawani jarumi bane da xakaxo kana cikamin baki, ka bari sae kayi amarya sae ka faɗa mata haka bani ba'' shiru yayi bakinsa a sake hakan yasa ta kuma masa wani kiss ɗin ganin yaƙi moving sae ta fara masa real one, ɗan janye jikinsa yayi yana maedata kan gadon shikuma ya tashi xaune yana cewa
''idan nace xan ɗauki maganarki serious illa xan miki amma ki ɗauka akwae ranar maimaita wannan maganar, besides sunce sunaga xasuyi dissmissing namu soon''
''amma yaya baka cika Alƙawarin ba fa'' ganin yanda yake kallonta yasata tura baki gaba tana cewa
''yo kapaliçarşi ɗin mana''
''Grand Bazar wae?'' nodding ta masa
''kinga ae yanda haihuwar taxo miki ba'a shirya mata ba amma kinsan da tabbas sae munje''
''toh yanxu masoyi idan akayi suna muka tafi ba sae mu sauka a Istanbul ɗin ba da mun gama siyayya sae mu dawo gida''
''ehh inada tunanin hakan nima..''
''kuma dama gashi kamin alƙawari'' ta faɗa da sauri, hannu ya saka yana dungurin kanta yace
''kinga yarinyarnan huum halinki da mamaki, anyway bara dae muga yanda abun xae kasance'' da sauri tamatsa ta masa kiss a cin tana murmushi shima yimata yayi yana shafa kanta
Kwana uku tsakani aka sallamesu saboda yaron da jikinsa yayi kyau sosae

dan har sucking ya fara, uwar ma tafi fesa abunta kaman bara haehu ba dama ga jiki mae kyau daga hospital gidansu suka wuce a bisa umarnin Abby sae dae yan gidan suje
Sati na xagayowa aka shirya gagarumin taron suna huuum na faɗa muku mutanannan shiri sukayi na gaske dan inaga har shagalin bikinsu da ba'a samu anyi ba suka haɗa sukayi a sunan 'Abbrar' su meenal ansha rawa kaman nothing ever happens mamy kuwa iyayen xamani a chan gidan ma nasu shagalin suka haɗa ita da AUNTY sukayo gayya sukasha ubansun suna duk da ba'a kawo yaro ba, suma kansu a can gidan sunata nasu shagalin sosae akayi ßarin Naira koda yake baku labari ßata lokacine just imagine sunan ɗan gidan yan gayu wanda suka jiƙu da Naira 😜😜
Kusan yaran Abby kaɗan ne basu xo ba dan kusan tun da suke wani event basu taßa yinsa kan iyayen a haɗe ba sae wannan dan haka suka saki jiki suka yi yanda sukaga dama, magrib nayi Jemien ta goyesa dan ita ta iya goyon yan gayu yanda ba xae takura ba tunda ba wani ƙwarin kirki yayi ba
Adawiyah kuma na xaune a ɗaki bayan Isha'i sallah ta gama ga su khaulat sun cika ɗakin suma anata shan fira, duk a gajiye take ma ga wani bacci-bacci dake ɗan son ɗaukarta tana kaucewa meenal ta turo ƙofar ta leƙo kanta tana daga waje tace
''anty yi sauri ki ɗan xo pls''
''lafiyaa''
''ehh toh kawae dae kixo'' hararan meenal ɗin tayi tana ci gaba da sauraren khaulat
''au baxaki xo ba? toh yayi bara naje na faɗawa yayan'' daga haka tajuya ta wuce
Sun ci gaba da firan ba daɗewa sae gashi ya shigo ɗakin da sallama a bakinsa gaeshesa suka shiga yi suna kallon yanda fatar jikinsa taketa wani kyalli saboda ƙaramin hannu da rigar shaddar jikinsa keda, batare da yace ƙala ba ko ya amsa gaisuwar tasu ba ya tsallaka har inda take in just a blink ya ɗauketa in bridal style wani irin tsitt ɗakin yayi suna sadda kawunansu
''idan maxajenku sunxo kawae ku tafi bacci xanje in sakata saboda jikinta'' yana gama faɗa ya fice, for almost a second suka bushe da wata irin dariya Aliyah dake shigowa ke cewa
''lallae na yarda KONTO kam ya sauya da gaskiyar AUNTY''
Gaskiya dae kam babana ka sauya nima na gani wlh, koda yake bani kaɗae na gani ba readers ma sun gani
Officialraah 444

CHARBIN KWAE
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by

Officialraah444

Hii lovelist we're in our last chapter now let's hit the stars
Page 42
Typing.....✍
A hankali rayuwar ta tafi yaro nata girma da lafiya dan sanda sukayi 40 days yayi jiim dashi kaman wanda dama can yakeda lafiya yayi ƀulƀul, kwana biyu suka ƙara akan arba'in ɗin suka tafi London a can ma sati kawae sukayi shima saboda gidan meenal da ta ɗan je yasa har sukayi satin dan itama anyi bikinta kuma anan London aka ajiyeta dan mijin data aura ɗin anan yake, a kwana na takwas suka ɗaga Turkiyya dan xuwa a cika mata alƙawari
ELITE WORLD GRAND İSTANBUL BASIN EKSPRES HOTEL
A kyakkyawa kuma ƙayataccen babban hotel da akeji dashi a turkiyya gaba ɗaya suka sauka yanayin tsarin süit ne kaman self content haka yake, sosae hotel ɗin ya ƙayatu da abubuwan morewa da kuma burgewa amma fa ana cin gidansu kuɗi abun ba ƙarya, su kaɗae sukaxo babu boys ɗinsa da honeymoon yakeso suyi na gaske
As usual kwana ɗaya sukayi suka fara fita da yake Alhamis ne suka je washegarin kuma juma'a ne dan haka sukayi shirin masallaci, jallabiya ya saka maroon ita kuma ta saka abaya blue shikuma Abbrar aka saka masa kayan sanyi an riga an kawo masa Mota dan haka da kansa yayi driving nasu
BLUE MOSQUE suka fara xuwa daɗaɗen masallaci mae cike da tarihi da kuma tsararren gini mae ɗaukar hankali bayan gama Sallah aka ƙarasa dasu suka gaesa da Imam ɗin masallacin sannan suka xaxxagaya ciki wayarta ta ba wata balarabiya ta masu hotuna, daganan suka fito
GRAND BAZAAR suka sauka (itace babbar kasuwar duniya wacce aka gina tun a daular Usmaniyya, babu wani nau'in abu da babu a kasuwar hatta awara😝) da yake Abbrar ɗin da kaurinsa so kayansa na haihuwa duk sun yi kaɗan dan haka shi ta fara yiwa siyayya, KONTO yana kan waiting chair da Abbrar ɗin a jikinsa ganin baya hangota yasa tabi wata hanyar ta ƀulla inda ake siyar da kayan maxa, sosae ta xage ta masa siyayya kusan duk wani nau'i na abu da tasan tanaso ya rinƙa amfani da sae da ta ɗauka
Bata yarda yagani ba tana ajiyewa gun biyan ta janyesa suka tafi wani ƙaramin Rüştü Kazım (kazim resturance) suna saeda shinkafa sosae a wurin dan kusan daga ita sae nama ma suke siyarwa, da kanta ta masu order bata ma tsaya tambayarsa ba shima kuma bae yi complain ba saboda abincin ya masa ba laifi suna gamawa sukaje mosque dakenan bayan kasuwar sukayi sallah, da yake siyayyan nada yawa kuma ga yamma daga Kapalıçarşı ɗin direct hotel suka koma
Washe gari sukaje galata tower (wani babban gidan tarihi ne kuma dogon tsauni ne wanda abubuwan tarihin ƙasar suke a ciki) acan suka ƙaraci wuninsu suna kallon kayan mutan da sae 11pm suka dawo gida a wani irin gajiye barin ma ita dan shi dama yana xaune ne sae idan ta tashesa ya bita kuma da sun shiga wani ƀangaren xae nemi wuri yayi xamansa

A haka sukayi sati biyu anan ana gobe xasu wuce which is another Friday suka kuma xuwa Grand Bazaar da yake da safe ne nan da nan suka gama siyayyarsu suka wuce
HAGIE SOPHIA MOSQUE anan sukayi Sallah sannan sukaje SEVEN HILLS RESTAURANT suna gamawa da nan suka tafi yawo sune har BASILICA CISTERN (wani tsohon gini da ake ɓoye ruwa a lokacin Emperor Justinian saboda yawan fama da ake da rashin ruwa kafin a gina masu dams ɗin da sukeda yanxu almost shekara dubu wurin goma a baya) kallon daɗaɗen Marvel's ɗin da ke xube a ƙasan wurin tayi kaman yau aka xubashi saboda gyara da kuma ci gaba da ƙasar takeda
''wannan wurin dae baxa'a taɓa rasa aljanu ba masoyi'' adawiyah ta faɗa tana taɓa wani gunki dakeda wani uban abu a ka kaman itace
''haba dae?''
''huum ehh mana irin waɗannan wuraren dama ae dole a samu aljanu gafa duk gumaka ne a wurin''
''ga kuma kiɗa yanata tashi ba'' ya faɗa yana ɗan juya wani abu kaman ɗan socket haka dakenan kusan biyar
''bea wannan ko mene'' ta faɗa tana shafa wani abu kaman jirgin ƙasa
''kayansu ne can su suka sani''
Da wuri suka dawo saboda gyaran da tace bata ida ba sanda ta idar 9 tayi tana fitowa wanka ta iskesu shida ɗan nasa sunyi bacci a kujera dan hanasu tayi su bita, ɗan shiru tayi tana kallon su yanda suke baccin peacefully ta kalli uba ta kalli ɗa tana ƙoƙarin gano kamanninsu
Abbrar kam sakk itace har yanda takewa bakinta amma kuma fatarsa kamar ta ubansa ce dan a yanxun ma ya ɗan fara sauyawa yayi duhu kaɗan amma, saedae sanyin hali da alama na uban ne dan sae ya wuni bae nemeta ba kokuma yayi kuka kullum shiru yana jikin babansa
''hi mun miki kyau ne?'' cikin muryan bacci ya faɗa yana buɗe idonsa guda, ɗan firgigit tayi tana gyara yanayin fuskanta tace
''ehh mana sosae ma ae kullum cikin yimin kyau kuke kunfi kowa kyau a idanu na'' chin ɗinta ya ɗan ja yana tashi ya saɓi Abbrar ɗin yana cewa
''shigomin da ruwa bara na kwantar da shi'' kanta ta jinjina masa tana binsa da ido har ya shige ɗakin
''bansan wanne irin so nake maka ba'' ta faɗa tana ɗan sadda kae
Officialraah 444

CHARBIN KWAE??
(Janka sae mae nutsuwa)
Story and writing by
Officialraah444

Page 43
Typing.....✍
Washe garin kuwa suka sauka Madina as promised anan xasu xaune dindindin gidan a Qebaa road yake quite street ne gun duk da akwae hotel daga baya amma street ɗin nasu babu wani hayaniya, gidan nasa self content ne part uku sae compound ɗin da xae iya ɗaukan mota biyu xuwa uku ga wasu shukoki masu kyau sosae sun lulluɓe gidan daga baya kuma pool ne
Yaransa sun rigasu isowa sae ya fita dasu sukaje sukayo siyayyan food items sukaxo suka jere mata a kitchen ɗin har da shi, lokacin ta gama jera masa kaya a sif ɗinsa sae ta shige kitchen ɗin tunda an gama komae
White rice tayi da miya ba'a kawo kifi ba sae wani uban nama da suka kawo na jimina jaɓi guda, wata doguwar tsoka ta janyo ta daddasha taɗora tanata tsaye a kitchen ɗin har komae ya dahu amma naman ko alamar laushi baiyi ba
''yo wae wannan wace irin jaraba ce? ni na gaji gaskiya'' ta faɗa tana yin ɗakinsa yana kwance a gado Abbrar na kan ƙirjinsa sunata shan bacci ae batasan sanda ta wani irin riƙe ƙugu ba tana cewa
''wae bala'i bacci ma kuke ni inata faman wahala'' ganin fa da gaske baccin nasu yayi nisa sae kawae ta juya ta fice tana cewa
''duk xaku sani babu wanda xaeci abinci da nama a gidannan''
Da dare ya shigo ɗakin shida Abbrar a jikinsa dama shi yakewa Abbrar ɗin wanka dan haka ta barsa dashi ta shiga cikin tanata ƙulle-ƙullenta, ganin sun shigo jikin Abbrar ɗin sanye da kayan bacci sae ta miƙe da kanta ta taresa tana amsar yaron
''ummuh what are u up to now?'' ya tambaya yana tayata buɗe gadon yaron
''a'ah me kake nufi?'' ta faɗa tana miƙewa tsaye shima miƙewar yayi yana kama hannayenta
''wife ban fa yarda dake ba when kika fara ɗaukowa Abbrar kaya har ki tayani shiryasa?'' dariya taji ta taho mata tana ƙoƙarin maedawa ammaiinaa ae batasan sanda ta kwashe da wata irin dariya ba
''kae masoyi dan Allah idan akaji sae a ɗauka ae bana kulawa da yaronnan'' ta faɗa tana ƙoƙarin cire masa botur
''kinga ni ba ruwana, a'a karki min un-buttoning mana yanxu na sakata fa''
''tsattt cire kaje sif ɗinka ka ɗauko wasu'' ta faɗa tana ƙarasa cire masa xaeyi magana ta kallesa sae ya turo baki yana kama hanya
''Aminiyaaa, Aminiya dae'' murmushi tayi jin yanata ƙwalo mata kira ɗakin ta nufa tana haɗiye dariyarta
''wannan kiran mafarautan fa?'' ta faɗa tana riƙe ƙugu
''menene wannan?'' ya tambaya yana nuna warlldrope ɗin nasa da hannu
''kayan xaman gida ne dana bacci na tattaro maka daga yau su nakeso ka rinƙa sakawa idan kananan'' hannunsa ya saka a tsakanin hannunta da waist ɗinta ya haɗata da jikinsa yana cewa
''this wife deserves more than love from her husband, thank u so much wife for bringing this unexpected light to my life i love u so much''

''i love u too hayatty'' ta faɗa interlocking their mouth.
Nima kuma i love u so much reader's, I love u from moon and back then❤
Masha Allah alhmdlh Allah yayi lokacin rabuwa kuma yaxo
Cikin ikon Allah on today 24th feb 2025 Allah yayi nayi na gama lafiya sae kuma idan mun sake haɗuwa a saboda book ɗina mae suna (YA MACE) karki/karka/karku bari a baku labarin wannan ƙayataccen labarin da xaeyi hitting stars wlh
For those that always talk about CHARBIN KWAE, CHARBIN KWAE finally charbin kwae dae ya ƙare muna fatan ubangiji ya bawa duk wani ahali da basa xaman daɗi sauƙi a cikin rayuwarsu
As saying komae yayi farko yanada ƙarshe kuma kaman yanda wannan book ɗin yayi ƙarshe haka duk wani matsala yanada ƙarshe kuma muna fatan ilahu ya kawo mana sauƙi akan komae na rayuwa ameen
Your forever writer ce yau ta sauke maku littafinta na farko a rayuwarta wanda wasu masu xafin wanda suka fishi will soon appear maessuna ya mace wanda xae girgixa duniyar yan mata ya kuma nuna maku hanyar da xakubi dan ƙara ƙaunar juna tsakaninku da iyayenku unau
Karku manta OFFICIALRAAH444 dae ce ke magana
Akwae cahnnel ɗina na WhatsApp https://whatsapp.com/channel/0029VayqOnt7z4kbhamJgs0N Officialraah444 wanda anan ne xan riƙa saka muku sabon littafina by pages
Sannan akwae ta Facebook: officialraah444
Akwae Wattpad account ɗina shima mae suna: officialraah444
Karku manta sabon littafinmu na ya mace is for the Lady's karki bari a baki labari
Nagode, nagode, nagode taku har kullum
Rabi'atu Ibrahim officialraah444